# MAFI ALHERIN GUZURIN ZUWA LAHIRA BAYAN AYYUKAN FARILLA A BISA TAFARKIN KOYARWAR MAFIFICIN HALITTU

## خيرالزادإلى يوم المعاد من غيرالفريضةعلى هدي خيرالعباد بلغة الهوسا


*Mawallafi*

***HAKAM BN ADIL ZUMU AL-NUWAIRY AL-AQILY.***

*GaVatarwa:*

***SHEIKH HASSAN BN ABD ALLAH AL-QA'UD***

*Fassara*

**European Islamic Research Center (EIRC)**

**المركز الأوروبي للدراسات الإسلامية**

***&Hashim Muhammad Sani***

***Wanda ya bibiyi fassarar***

***Faiz Shuaib Adam***



**www.islamland.com**




ISLAM LAND

GROW GOODNESS BY YOUR HAND

EXPLORE ISLAM IN ALL LANGUAGES

WWW.ISLAMLAND.COM

# Takataitaccen jawAbun mai gaVatar da littafin

*Godiya ta tabVata ga Allah shi kaxai, tsira da amincin Allah su tabVata ga wanda babu wani AnnAbu a bayan sa da iyalan sa da sahabban sa masu girma da tsarki.*

*Bayan haka:*

*Haqiqa na leqa cikin wannan littafi Mai anfani wanda akayima suna da mafi alherin guziri na Xan uwa injiniya Hakam Xan Adil zumu Al-Aqily, sai na mayar dashi littafi Mai anfani da amfanarwa, Mai littafin ya tattara ayyuka masu falala ta hanya Mai sauki da dadi... yadda ya koro a cikin sa maganganu, da hadisai da labarai wanda sanya shauki, Haqiqa Qwaqwalwa ta tayi kai komo cikin farfajiyar wannan baituka:*

*Yakai matarran kwakwalan mu da mafi alherin guziri*

*Daga karantarwan mafi alherin manzo zuwa ga bayi*

*Ka hada acikin sa dukkanin Abunda yake da dadawa*

*Na fa'idoji wanda suke haskaka zuciya da shiriya*

*Ubangijin al arshi ya saka maka da Abunda ya fishi*

*Da alheri Duniya da kuma lahira*

*Ina roqon Allah mabuwayi da daukaka da ya bamu ikhlasi cikin maganganun mu da ayyukan mu, Allah kai daxin tsira akan AnnAbun mu Muhammad.*

*Wanda ya rubuta*

*Mai neman yafiyar Ubangijin shi*

*Hasan xan Abdullahi Al- qa'ud*

*Riyad cikin 30 ga muharram 1429h*

*Da sunan Allah Mai rahama mai jin qai*

# GAVATARWA

Godiya ta tabVata ga Allah wanda da ni'imar sa ne abubuwa masu kyau suke samuwa. Ina Mai godiya a gareshi godiya irin wacce ta dace dashi da kuma girman mulkin sa, wanda yake faxin cikin mafi hikiman littafi cewa:

﴿ وَٱلۡعَصۡرِ ١ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَفِي خُسۡرٍ ٢ إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلۡحَقِّ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلصَّبۡرِ ٣ ﴾

**Ma'ana: "Ina rantsuwa da zamani (1) lallai dukkanin Mutane suna cikin Asara (2) sai waxnda sukayi imani kuma suka aikata aiki na Qwarai sukayima juna wasiyya da gaskiya kuma sukayi ma juna wasiyya da hakori (3)"[1].**

Ina kuma shaidawa babu abun bautwa da gaskiya bisa cancanta sai Allah shi kaxai wanda bashi da abokin tarayya, shaidawa irin wanda muke kyakyawan cikawa da ita ranar mutuwa, kuma zamu amfanu da ita alokacin haduwar mu dashi ranar Al-qiyama, kuma ina shaidawa shugaban mu Muhammad manzon Allah ne s.a.w, kuma lallai ya isar da Saqon da aka aikoshi da ita kuma ya cika alkawari, babu wani alheri face ya nuna mana shi, kuma babu wata hanya ta shiriya face ya nuna mana ita, tsira da amincin ubangiji na su kara tabVata a gareshi, bayan haka:

---

Suratul asri[1]

Lallai daga cikin ni'imar Allah agaremu shine ya shar'anta mana wasu wajibobi wanda sune ginshikan addini da asalinsa, Duk wanda ya aikata su to hakaki ya saukin nauyin sa, wanda kuma yayi wasa dasu to sauran ayyukan ma bazai iya aikata suba, kyauwun su shine tsiran bawa ranan kiyama, an karvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

" أول ما يحاسب به العبد يوم القيامة صلاته فإن وجدت تامة كتبت تامة وإن كان انتقص منها شيء قال انظروا هل تجدون له من تطوع يكمل له ما ضيع من فريضة من تطوعه ثم سائر الأعمال تجرى على حسب ذلك"

**Ma'ana: "lallai farkon Abunda za'a fara yima bawa HisAbu akansa ranar Al-qiyama cikin ayyukan sa shine Salla, idan tayi kyau to Haqiqa ya rabauta kuma ya tsira, idan kuma Vatayi kyau ba to Haqiqa ya tabe kuma yayi asara, idan wani daga cikin wajibobin su sun samu nakasu Allah Maxaukaki zai ce ku duba cikin ayyukan sa akwai na nafila dayayi sai ku cika wannan nakasun da ya samu a aikin wajibobin sa, daganan sai sauran ayyukansa su kasance irin haka"[2].**

Sa'annan ya ware wasu ayyuka daga cikin jinsinta, wacce take share hawaye da kuma cike nakasu, ya kuma sanya lada Mai tarin yawa da sakayya Mai girma akan aikata ta, ya kuma kara akan haka dukkanin sauran ayyuka na Qwarai wanda zasu rika wanke rai da tsarkaketa, su kuma tara

Sahihul tirmizi (413) da nasa'i (465) da ibn majjah (1425)[2]

mata martaba da lafiya, ya kuma sanya lada masu yawan gaske da Alheri masu xinbi akan wannan ayyuka, duk da kasancewar su ayyuka ne masu sauqin gaske wanda basa sa rai cikin Qunci ko kuma kosawa da su.

Yakai Xan uwana Musulmi da yar uwata musulma lallai dukkanin ayyukan nan da suka gaVata suna da sharuxxa kafin su karvu a wurin Allah Maxaukaki, kuma domin a basu lada cikakke ba tare da tawaya ba, daga cikin abun da ba'a zalumtar mutane da kwatankwacin Qwayar zarra.

**SHARADIN FARKO CIKIN WANNAN SHARUDDA:**

NIYYA: An karvo Hadis daga sarkin muminai Umar Xan khaddab Allah ya kara masa yarda yace: naji manzon Allah s.a.w yana cewa:

"إنما الأعمال بالنيات وإنما لكل امرئ مانوى"

**Ma'ana: "lallai dukkanin ayyuka suna tare da aiki, kuma ko wane Mutum yana samun Abunda yayi niyya domin sa"[3],**

Duk wanda yayi niyya domin neman yardar Allah kuma aikin sa ya kasance tsarkakakke domin sa shi kaxai, wanda be cuXanya shi ba da jin mutane ko kuma riya ko munafurci, to lallai Allah zai karbi aikinsa.

**SHARADI NA BIYU CIKIN WANNAN SHARUDDA:**

---

Malaman Hadis guda shida duk sun rawaito shi[3]

Aikin ya kasance ya dace da Abunda Allah ya shar'anta da kuma koyarwan manzon Allah s.a.w, baza'a karba wani aiki ba wanda yayi kama da aikin kafirai da ma'abota littafi, kuma baza'a karba aikin da aka aikata shi ba da son zuciya ko kuma ta hanyar yan Bidi’a da Vata.

MUNAFIKI: aikin sa ba'a karba saboda niyyar sa Vatacciya ce kuma yana can Qarshen wuta, Allah Maxaukaki yace:

﴿ إِنَّ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ فِي ٱلدَّرۡكِ ٱلۡأَسۡفَلِ مِنَ ٱلنَّارِ وَلَن تَجِدَ لَهُمۡ نَصِيرًا ١٤٥ ﴾

**Ma’ana: "lallai munafukai suna can kasan wuta kuma bazasu samu mataimaki ba (145)"[4].**

XAN BIDI’A aikin sa ba'a karba saboda aikin sa Vatacce ne koda kuwa niyyar say a kasance Mai kyau ce saboda faxin Aisha Allah ya kara mata daga manzon Allah s.a.w yace:

" مَنْ أَحْدَثَ فِي أَمْرِنَا هَذَا مَا لَيْسَ فِيهِ فَهُوَ رَدٌّ"

**Ma’ana: "Duk wanda ya qirqiro wani aikin cikin wannan al'amari namu to an mayar masa da kayan sa"[5].**

Ya kuma kara faxin har wayau:

**Ma’ana: "lallai Allah ya nisanta daga aikin dukkanin wani Xan Bidi’a har sai yabar yin Bidi’ar"[6].**

---

Suratun nisa'i[4]

Buhari ne ya frawaito shi (2697), da muslim (1718), da abu dawud (4606), da ibn mahhaj (14) [5]

Abu shekh ne ya rawaito shi cikin tarihin Asbahani, da dabari da baihaki, albani kuma yace isnadin shi ingantacce ne [6]

Yakai Xan uwa masoyi da yar uwa Mai daraja kafin ka samu wannan fa'idar kuma a rubuta maka karbuwa Duniya da lahira, kuma Ka samu karshe Mai kyau a lahira, na rubuta maka wannan littafi cikin Abunda Allah yamun budi dashi cikin falalar sa mai tarin yawa, na ayyuka da maganganu da ayyuka na neman kusanci, suna karawa Mutum daukaka da kusanci zuwa ga abungijin sa, ayyuka masu tarin lada da anfani masu yawa ga Mutum da iyalan sa da al'ummar sa. Darajar salihai na karuwa dasu cikin aljanna Mai ni'ima, kuma martaban masu biyayya yana banbanta dasu, kuma za'a ba Mutum littafin sa da hannun dama saboda su, kuma suna sanya ma'auni suyi nauyi ranan sakamako, kuma kuma suna sanyawa a tsahi Mutum tare da annabawa da siddikai da shahidai cikin kololuwar aljanna, Allah Maxaukaki yace:

﴿ إِنَّ ٱلْمُسْلِمِينَ وَٱلْمُسْلِمَٰتِ وَٱلْمُؤْمِنِينَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتِ وَٱلْقَٰنِتِينَ وَٱلْقَٰنِتَٰتِ وَٱلصَّٰدِقِينَ وَٱلصَّٰدِقَٰتِ وَٱلصَّٰبِرِينَ وَٱلصَّٰبِرَٰتِ وَٱلْخَٰشِعِينَ وَٱلْخَٰشِعَٰتِ وَٱلْمُتَصَدِّقِينَ وَٱلْمُتَصَدِّقَٰتِ وَٱلصَّٰٓئِمِينَ وَٱلصَّٰٓئِمَٰتِ وَٱلْحَٰفِظِينَ فُرُوجَهُمْ وَٱلْحَٰفِظَٰتِ وَٱلذَّٰكِرِينَ ٱللَّهَ كَثِيرًا وَٱلذَّٰكِرَٰتِ أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُم مَّغْفِرَةً وَأَجْرًا عَظِيمًا ٣٥ ﴾

**Ma’ana: "lallai musulmai maza da musulmai mata da muminai maza da muminai mata da maza masu yawan ibada da mata masu yawan ibada da maza masu gaskiya**

**da mata masu gaskiya da maza masu hakuri da mata masu hakuri da maza masu tsoron Allah da mata masu tsoron Allah da maza masu sadaka da mata masu sadaka da maza masu Azumi da mata masu Azumi da maza masu kiyaye farjin su da mata masu kiyaye farjin su da maza masu ambaton Allah dayawa da mata masu ambaton Allah dayawa Allah ya tanadar masu wata irin gafara da lada Mai girma (35)[7]."**

Anan Duniya kuma Mutum musulmi yana samun walitakan Allah da taimakon sa da nasarar sa da shiriyan sa da ita, an karvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

" إِنَّ ٱللَّهَ قَالَ مَنْ عَادَى لِي وَلِيًّا فَقَدْ آذَنْتُهُ بِالْحَرْبِ وَمَا تَقَرَّبَ إِلَيَّ عَبْدِي بِشَيْءٍ أَحَبَّ إِلَيَّ مِمَّا افْتَرَضْتُ عَلَيْهِ وَمَا يَزَالُ عَبْدِي يَتَقَرَّبُ إِلَيَّ بِالنَّوَافِلِ حَتَّى أُحِبَّهُ فَإِذَا أَحْبَبْتُهُ كُنْتُ سَمْعَهُ الَّذِي يَسْمَعُ بِهِ وَبَصَرَهُ الَّذِي يُبْصِرُ بِهِ وَيَدَهُ الَّتِي يَبْطُشُ بِهَا وَرِجْلَهُ الَّتِي يَمْشِي بِهَا وَإِنْ سَأَلَنِي لَأُعْطِيَنَّهُ وَلَئِنِ اسْتَعَاذَنِي لَأُعِيذَنَّهُ"

**Ma'ana: "lallai Allah Maxaukaki yace: Duk wanda yayi gaba da waliyyi na to Haqiqa yayi umurni da yakan sa, kuma bawa be taba neman kusanci agare ni ba da wani aiki wanda nafiso sama da Abunda na wajabta masa, kuma bawana bazai gushe ba yana neman kusanci zuwa gare ni ba da aikin nafiloli face na soshi, idan kuma na soshi zan kasance masa Abunda yake ji dashi da**

---

[7] Suratul ahazab

**Abunda yake gani dashi da kuma hannun da yake taba abu dashi da kuma kafar da yake tafiya da ita, kuma idan ya tambaye ni wani abu zan bashi kuma idan ya nemi tsari n azan tsare shi"[8].**

A karshe ina roqon Allah Mai ji kuma masani ubangijin al'arshi Mai girma daya amfanar da yan uwana musulmai da wannan littafi, kuma yasanya aiki na dominshi shi kaxai, ya kuma shiryar damu baki dayan mu zuwaga alheri da shiriya da iki da maganganu na kwari, idan na dace to daga Allah ne wanda yake datar da masu masa biyayya zuwa ga alherai kuma ya shiryar dasu zuwa ga hanya madaidaici, idan kuma nayi kuskure to daga gareni ne da zuciyata wacce take yawan umurni da sabo da kuma wasiwasin Shaidan jefaffe, tsinuwar Allah ta tabVata a gareshi har AbaXan, ina kuma yin salati ga wanda aka aiko domin rahama ga talikai shugaban mu Muhammad mafificiyar tsira da cikakkun aminci su tabVata a gareshi da iyalansa da sahabban sa da Duk wanda suka bisu da kyautatawa har zuwa ranar Al-qiyama, ina tasbihi da Allah da dukkanin abun da aka masa tasbihi dashi aka kuma bauta masa dashi cikin sammai da kassai. Amin kuma karshen da'awar mu itace godiya ta tabVata ga Allah ubangijin talikai.

Mawallafi injiniya shugaba/

**HAKAM ZUMUN NUWAIRY AL-AKILY**

---

Buhari ne ya rawaito shi (6502)[8]

7ga watan rAbu'ul auwal, 1426 hijiri.

# Shinfixa:

Shinfida ga wannan littafi inason faxin wasu daga cikin bayanai wanda zasu taimaka wa makaranci wurin fahimtar wannan littafin da kuma hadafin wannan littafi da muhimmancin sa ga ko wani gida da duk Mutumin dake kwadayin rahamar ubangijin sa da tsira ranan Al-qiyama daga azaban sa Mai radadi da tsananin ukubar sa, kuma Haqiqa ya shuka domin kololuwan daraja kuma yazo da ayyuka cikanku masu kyau da falalar Allah ta taufikin sa.

Daga cikin manyan ayyukan lada wandaMutum musulmi zai aikata shine dagewa da tsayuwar sa da cika ayyukan da Allah ya wajabta masa na ibadu, Sallah da zakkah da Azumi da hajji Duk wanda ya aikata su yadda shari'a ke son su kuma a karkashin karantar wan manzon Allah s.a.w to Haqiqa ya biya hakkokin Allah akan sa kuma ya sauke nauyin sa da ke wuyan sa agaban Allah, an karvo Hadis daga dalhata Xan ubaidullah Allah ya kara masa yarda yace:

“جَاءَ أَعْرَابِيٌّ إِلَى رَسُولِ ٱللَّهِ صَلَّى ٱللَّهُ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ فَقَالَ : يَا رَسُولَ ٱللَّهِ ، مَا الإِسْلامُ ؟ قَالَ : خَمْسُ صَلَوَاتٍ فِي يَوْمٍ وَلَيْلَةٍ قَالَ : هَلْ عَلَيَّ غَيْرُهُنَّ ؟ قَالَ : لاَ ، وَسَأَلَهُ عَنِ الصَّوْمِ ؟ فَقَالَ : صِيَامُ رَمَضَانَ قَالَ : هَلْ عَلَيَّ غَيْرُهُ ؟ قَالَ : لاَ . قَالَ : وَذَكَرَ الزَّكَاةَ ، قَالَ : هَلْ عَلَيَّ غَيْرُهَا ؟ قَالَ : لاَ . قَالَ : وَاللَّهِ لاَ أَزِيدُ عَلَيْهِنَّ ، وَلا أَنْقُصُ مِنْهُنَّ ، فَقَالَ رَسُولُ ٱللَّهِ صَلَّى ٱللَّهُ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ : قَدْ أَفْلَحَ إِنْ صَدَقَ”

**Ma’ana: (wani Mutum yazo wurin manzon Allah s.a.w daga cikin mutanen garin Kauye kansa a rufe araunin muryan sa amma ba'a gane Mai yake fada har ya kusanto sai gashi yana tambaya gaMai a musulunci, sai manzon Allah s.a.w yace masa: salloli guda biyar a rana, sai yace shin akwai wasu akai na bayan su? Sai yace: a'a babu sai dai dayi nafila, sai manzon Allah s.a.w yace: da Azumin Ramadan sai yace, shin akwai wani Azumin kuma akai na bayan wannan? Sai yace: a'a bubu sai dai kayi na nafila, sai yace sai manzon Allah s.a.w ya Ambato masa zakka sai yace shin akwai wani akaina bayan sa, sai yace: a'a babu sai dai kayi na nafila sai wannan Mutumi ya juya yana cewa: na rantse da Allah bazan kara komai ba akan wannan abubuwa kuma bazan rage komai ba sai manzon Allah s.a.w yace: Haqiqa ya tsira idan gaskiya yake fadi)[9].**

sai dai ku sani yaku yan uwana lallai ran mumini kullum tana neman kari ne na lada, Xan Mai yasa bazata nema Karin lad aba! Bayan darajar masu tsoron Allah ya banbanta saboda dalilin tasbihi ko kuma ciyar da miskinai ko kuma taimakon mabukaci.

Ya kai Xan uwa Mai daraja da yar uwa Mai girma lallai aiwatar da farillai ba al'amari bane Mai sauki kuma ba karamin abu bane sai ga wanda Allah ya sawwake masa hakan, saboda haka ne a mafiya yawan lokuta zakaga nakasu da barna yana shigan su kuma musamman ma

---

Buhari ne ya rawaito shi (46) da muslim (11) da abu dawud (391) da nasa'i [9] (458)

akwai makiya guda biyu wanda suka zauna a hanya suna dakon mu domin Vatar damu da hanamu bautan ubangijin mu Maxaukaki:

**Na farkon:** shi ne Shaidan wanda yayi rantsuwa da buwayan Allah cikin Al-qur'ani cewa sai ya Vatar da yan Adam, Allah Maxaukaki yace:

﴿ قَالَ فَبِعِزَّتِكَ لَأُغْوِيَنَّهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿٨٢﴾ إِلَّا عِبَادَكَ مِنْهُمُ ٱلْمُخْلَصِينَ ﴿٨٣﴾ ﴾

Ma'ana: " sai yace ina rantsuwa da buwayar ka sai na Vatar da su baki dayan su (82) sai dai bayanka a cikin su tsarkakakku" (83)[10].

Shaidan yana zaman dakon mu a duk lokacin daya samu dama don yi mana wasiwasi kuma yana kokarin ganin ya canzamu daga bautan Allah, an karvo Hadis daga abu Huraira cewa manzon Allah s.a.w yace:

Ma'ana: " lallai dayan ku idan ya tashi yin Salla, sai Shaidan yazo masa ya masa wasiyawasi har ya manta shin raka'a nawa yayi ne"[11].

yana kokari matuka akoda yaushe cikin ko wani hanya domin ganin bamu da wurin gudu da tsira daga gareshi, Allah Maxaukaki yace yana Mai hakaito maganar sheda:

---

Suratu sad[10]

Hadis ne ingantacce, abu dawud ne ya rawaito shi cikin Salla (1031)[11]

﴿ ثُمَّ لَآتِيَنَّهُم مِّنۢ بَيۡنِ أَيۡدِيهِمۡ وَمِنۡ خَلۡفِهِمۡ وَعَنۡ أَيۡمَٰنِهِمۡ وَعَن شَمَآئِلِهِمۡۖ وَلَا تَجِدُ أَكۡثَرَهُمۡ شَٰكِرِينَ ١٧ ﴾

Ma’ana: "sa'annan zan zo masu ta gabansu da bayan su dama da hagu kuma bazaka samu daya daga cikin su suna godiya ba (17)"[12].

Da kuma faxin sa cewa:

﴿ قَالَ رَبِّ بِمَآ أَغۡوَيۡتَنِي لَأُزَيِّنَنَّ لَهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَأُغۡوِيَنَّهُمۡ أَجۡمَعِينَ ٣٩ إِلَّا عِبَادَكَ مِنۡهُمُ ٱلۡمُخۡلَصِينَ ٤٠ ﴾

Ma’ana: "sai yace ya ubangiji tunda ka Vatar Xani sai na zayyana masu abubuwa a cikin kasa kuma sai na Vatar dasu bakin dayan su (39) sai dai bayin ka daga cikin su tsarkakakku (40)"[13]

saboda haka kuyi taka tsantsan yan uwana daga makircin sa, Allah yayi mana tsari daku daga sharrin sa.

**Na Biyu:** zuciyatan ayawan yin umurni da sabo sai wanda ubangiji na yayi masa rahama yadda take kawatawa Mai ita aikata haramun da kuma barin ayuukan lada, Duk wanda yayi mata biyayya dason rai yana cikin wutan jahannama Allah yayi mana tsari da ita, wanda ya saba mata kum Haqiqa ya rabauta, an karvo Hadis daga shaddad Xan aus Allah ya kara masa yarda daga manzon Allah s.a.w yace:

---

Suratul a'araf[12]
Suratul hijri[13]

"الْكَيِّسُ مَنْ دَانَ نَفْسَهُ وَعَمِلَ لِمَا بَعْدَ الْمَوْتِ ، وَالْعَاجِزُ مَنْ أَتْبَعَ نَفْسَهُ هَوَاهَا وَتَمَنَّى عَلَى ٱللَّهِ"

Ma'ana: " Mai dabara da rabo shine wanda ya tarbiyyantar da ran sa yayi aiki domin bayan mutuwar sa gajiyayye kuma shine wanda yAbu son zuciyan sa yayi fata akan Allah"[14],

An kuma karvo daga Umar Xan kaddab Allah ya kara masa yarda yace:

حَاسِبُوا أَنْفُسَكُمْ قَبْلَ أَنْ تُحَاسَبُوا وَتَزَيَّنُوا لِلْعَرْضِ الأَكْبَرِ وَإِنَّمَا يَخِفُّ الْحِسَابُ يَوْمَ الْقِيَامَةِ عَلَى مَنْ حَاسَبَ نَفْسَهُ فِي الدُّنْيَا. وَيُرْوَى عَنْ مَيْمُونِ بْنِ مِهْرَانَ قَالَ لاَ يَكُونُ الْعَبْدُ تَقِيًّا حَتَّى يُحَاسِبَ نَفْسَهُ كَمَا يُحَاسِبُ شَرِيكَهُ مِنْ أَيْنَ مَطْعَمُهُ وَمَلْبَسُهُ.

Ma'ana: "kuyi wa kanku HisAbu gabanin ayi maku HisAbu kuma ku auna aikin ku domin ranan sakamako babba, saboda Duk wanda yayi ma kansa HisAbu anan Duniya to HisAbun sa nayin sauki a ranan Al-qiyama)[15].

An kuma rawaito daga Maimun Xan Mihran cewa: (bawa bazai zama Mai tsoron Allah ba har sai ya yima kansa HisAbu kamar yadda abokin sa kasuwancin sa ke masa HisAbu na cewa a ina yake samo Abunci da tufafin sa)[16].

Wanda yAbu farilla da sunnoni wanda manzon Allah s.a.w ya sunnanta masa na jinsinta, domin ya kamala Abunda ya toye da kuma canji ga Ladan daya rasa. Salla tana da sunnoni na kullum kullum a jere, haka zakka akwai sadaga

---

Hidisi ne ingantacce tirmizi ne ya rawaito shi (2459), da ibn majja (4260) [14]

Tirmizi ya rawaito shi (2459)[15]

A littafi daya aka samo wannan Xana saman[16]

daga jinsinta, Azumin Ramadan akwai Azumin nafila shima, umra kamar hajji take. Bayan farillai da sunnonin ta akwai dayawa daga cikin ayyuka da magana wanda aka shar'anta domin ta kaance taimako ga bawa musulmi na samun Karin lada da kuma kankare zunubai da daga darajar sa kuma wannan ayyuka masu sauki ne ga rai Mai tsarkakkiya da tsabta wanda Allah ya mata gam da katar zuwa hanyan alheri da samun lada babba.

Yan uwana bayan ayyuka masu falala da tarin lada wasu littattafai dayawa sunyi magana akan su saboda haka na dauki manhaji na koro hadisai ba tare da wallafa bAbu ba ko kuma sharhin daga mawallafi, saboda hakaki fikira ya zo mun na hada Abunda Allah ya sawwake mun da Abunda nakeson anbata  cikin Abunda na gani kuma yan uwana suka tunar Xani shi na wannan sunnoni da ayyuka cikin wannan littafin nawa guda daya wanda zai tara maka wannan alheran masu yawa, a rarrabe da tsari Mai saukiwurin fahimta ba tare da yin zunfur ba cikin hukunce hukunce ko kuma yin zurfi cikin fiqhu da ibadu, wata kila zata kasance da yardar Allah Maqogaro ga musulmi wanda zai rika bibiya a kullum kuma littafi ne takaitacce wanda ya kunshi somun tAbu daga dukkanin bangarori, zai amfanar da musulmi da yardar Allah cikin addinin sa da Duniyar sa cikin rayuwan san a yau Xana gobe da mutuwar sa da makomar sa. Kuma ya raba wanann littafin zuwa gida biyu manya ta fuskar anfani da lada da kuma samun lada, akwai ayyuka wanda Ladan su da anfanin su yake komawa ga wanda ya aikata su shi kaxai kamar Sallar sunnoni na kullum da umrah. Kuma akwai ayyuka wanda anfanin su yake ketarawa zuwa ga iyalan Mutum bayan sa da makwabtan sa da al'umman sa baki daya kuma mafanin zai kasance anan Duniya da lahira kamar sadaka da ilimi Mai

anfani. Kuma ku sani yaku yan uwana cewa wannan rarrabawan yana da anfani daga cikin haka akwai cewa musulmi zai tashi daga aiki Mai anfani gareshi shi dakai zuwa aikin da anfanin sa da Ladan zai samu kowa kuma hakan zai taimaka wurin shirya ayyukan da sukafi lada akwai ayyuka masu falala dayawa akwai kuma wanda aka fisu falala kuma akwai masu muhimmanci da kuwa wanda sukafi muhimmanci kuma akwai ayyukan da suka dace da wani zamani banda wani zamanin ko kuma ya zam na wasu wurare ne kawai banda wasu. Ina Mai kafa Hujja cikin Abunda ya na kawo cikin wannan kokari nawa da ayoyi masu girma da hadisai masu daraja da kuma maganganun sahabbai wanda ya dace da hakan ko kuma magaVatan mu na Qwarai ko malaman mu na wannan zamani masu falala, Allah ya amfanar da yan uwana musulmai da wannan littafi ya kuma sanya shi aiki domin neman yardar sa shi kaxai..

Ameen

A karshen wannan shinfida ina roqon yan uwa wanda suka karanta wannan littafi cewa idan sun samu kuskure ko kuma nakasu ko kuma sunason faxin wani tunatarwa Mai anfani ko nasiha ta gaskiya da sumun wasika ta wannan adireshi Kaman haka

Layin waya: 41066 birnin riyad 11021

Ko kuma yanan gizo

@advisor07@hotmail.com

Ya Allah ka amfanar da yan uwana dashi kuma ka amfanar damu da Abunda muka karanta kasanya mu baki dayan mu

cikin wanda idan sunji magana sai subi mafi kyawun ta. Kuma ka gafarta mana zunuban mu da barnan mu cikin al'amarin mu da iyayen mu da sauran musulmai baki daya rayayyun su da matattun su, kuma ka bamu abubuwa masu kyau anan Duniya da lahira ka tsiratar damu daga azabar wuta da rahamarka ya mabuwayi Mai gafara.

# FARKO: ayyukan da anfanin su yake komawa ga Mutum shi kaxai Duniya da lahira.

## 1) Ayyukan masu alaka da Salla:

### a). ayyukan da akeyin su gabanin Salla:

(1) **Al-wala:**

Alwala ya kai Xan uwa makaranci tsarki da kuma wanke gabbai, kuma wanka ce ga zuciya daga zunubai da laifuka, an karvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda manzon Allah s.a.w yace:

« إِذَا تَوَضَّأَ الْعَبْدُ الْمُسْلِمُ – أَوِ الْمُؤْمِنُ – فَغَسَلَ وَجْهَهُ خَرَجَ مِنْ وَجْهِهِ كُلُّ خَطِيئَةٍ نَظَرَ إِلَيْهَا بِعَيْنَيْهِ مَعَ الْمَاءِ – أَوْ مَعَ آخِرِ قَطْرِ الْمَاءِ – فَإِذَا غَسَلَ يَدَيْهِ خَرَجَ مِنْ يَدَيْهِ كُلُّ خَطِيئَةٍ كَانَ بَطَشَتْهَا يَدَاهُ مَعَ الْمَاءِ – أَوْ مَعَ آخِرِ قَطْرِ الْمَاءِ – فَإِذَا غَسَلَ رِجْلَيْهِ خَرَجَتْ كُلُّ خَطِيئَةٍ مَشَتْهَا رِجْلَاهُ مَعَ الْمَاءِ – أَوْ مَعَ آخِرِ قَطْرِ الْمَاءِ – حَتَّى يَخْرُجَ نَقِيًّا مِنَ الذُّنُوبِ ».

"idan Mutum musulmi ko kuma mumini yayi Alwala idan ya wanke fuskar sa ruwan wannan wanke fuskar zai futar masa da dukkanin wani zunubi dayayi ta hanyar kallo da idanun sa, idan kuma ya wanke hannun sa shima wannan ruwan zai wanke masa dukkanin wani zunubi daya aikata da wannan hannu, idan kuma ya wanke kafarsa wannan ruwa zai wanke masa dukkanin wani zunubi daya taka da wannan kafar nasa yaje wurin aikata shi har sai an wanke shi daga zunuban sa"[17].

---

[17] Muslim da tirmizi ne suka rawaito shi

An karvo daga Usman Xan Affan Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: " Duk wanda yayi Alwala ya kumakyautata Alwalar zata wanke masa zunuban sa daga jikin sa ta hanyar farcen sa"[18]. An kara karvowa daga gareshi Allah ya kara masa yarda yace:naga manzon Allah s.a.w yayi Alwala irin wannan Alwalar nawa Xanayi sai yace: " Duk wanda yayi irin wannan za'a yafe masa zunuban sa da suka gaVata sai Sallar sa da tafiyar sa zuwa Masallaci su kasance Karin lada a gareshi"[19]. Ya kai irin wannan falala Mai girma daga Allah wanda ya sanya mana Abunda zamu rika tsarkake kawunan mu dashi daga dattin zunuban mu a kowace rana. Har wayau Alwala tana daga cikin sharadin ingancin Salla, Sallah Vata inganta sai dashiki kuma taimama da kasa idan be samu ruwa ba ko kuma bazai iya anfani da ruwan ba.

Kuma Alwala zata zama kwalliya ga muminai ranan Al-qiyama, ankarvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

إِنَّ أُمَّتِي يُدْعَوْنَ يَوْمَ الْقِيَامَةِ غُرًّا مُحَجَّلِينَ مِنْ آثَارِ الْوُضُوءِ فَمَنِ اسْتَطَاعَ مِنْكُمْ أَنْ يُطِيلَ غُرَّتَهُ فَلْيَفْعَلْ.

Ma’ana: "lallai al'ummata za'a kirasu ranar Alqiyama masu hasken gavvai na Alwala, Duk wanda ya samu dama a cikin ku to ya tsawaita hasken sa sai ya aikata hakan"[20].

## 2). Asuwaki:

Asuwaki yana daga cikin koyarwan shugaban manzanni s.a.w, yana cikin sunna ta fidirar Mutum kuma Haqiqa manzon Allah ya zaburar da sahabban sa akan

---

Muslim ne ya rawaito shi (245)[18]
Muslim ne ya rawaito shi (229)[19]
Buhari da muslim ne suka rawaito shi [20]

aikatashi musamman ma idan sun tashi yin Sallah, an karvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda manzon Allah s.a.w yace:

« لَوْلاَ أَنْ أَشُقَّ عَلَى أُمَّتِي لأَمَرْتُهُمْ بِالسِّوَاكِ عِنْدَ كُلِّ صَلاَةٍ »

Ma'ana: " Ba don kada na tsanantawa al'ummata ba da na umurce su dayin asuwaki yayin ko wani Salla"[21], saboda musulmi ya tsiga ganawa da ubangijin sa cikin tsarki na baki da kamshi Mai dadi kuma saboda kada mala'iku da bayin Allah su cutu daga warin da yake fita daga bakin masu Salla wnai lokaci. Ka sani cewa lallai Ladan asuwaki babba ne, an karvo daga Aisha Allah ya kara mata yarda cewa lallai manzon Allah s.a.w yace:

السِّوَاكُ مَطْهَرَةٌ لِلْفَمِ مَرْضَاةٌ لِلرَّبِّ.

" Asuwaki abun tsarkake baki ne kuma yana jawo yardar ubangiji"[22],

Rabo da tsira ya tabbata ga wanda Allah ya yarda dashi.

## b) Ayyuka da abubuwan da suka alakantu da Masallaci:

### 1) tafiya zuwa Masallaci:

An karvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

Buhari da nasa'I ne suka rawaito shi [21]
Tirmizi da nasa'I ne suka rawaito shi [22]

مَنْ تَوَضَّأَ فِي بَيْتِهِ فَأَحْسَنَ الْوُضُوءَ ثُمَّ خَرَجَ إِلَى الْمَسْجِدِ فَصَلَّى فِي جَمَاعَةِ الْمُسْلِمِينَ لَمْ يَرْفَعْ رِجْلَهُ الْيُمْنَى إِلَّا كَتَبَ ٱللَّهُ لَهُ بِهَا حَسَنَةً، وَلَا يَضَعُ رِجْلَهُ الْيُسْرَى إِلَّا حَطَّ ٱللَّهُ عَنْهُ بِهَا خَطِيئَةً

Ma’ana: " Duk wanda yayi Alwala a Gidan sa san nan ya fita zuwa Masallaci cikin maSallatai domin sauke Salla cikin salloli wajibai sahun sa zasu kasance daya tana kankare masa zunuban sa dayar kuma tana daga darajar sa"[23].

An kara karvo daga gareshi kuma yana cewa manzon Allah s.a.w yace:

Ma’ana: " Duk wanda yayi sammako ko yammaci zuwa ga Masallaci Allah ya tanadar masa da ajanna duk lokacin da yayi sammako ko kuma yamma"[24]. Lada nawa aka kara maka sannan kuma zunubai nawa aka kankare maka ya kai Xan uwa Mai daraja a lokacin da kake fita zuwa Masallaci saubiyar a kullum. Wanda yafi kowa samun wannan lada cikin musulmai shine wanda yafi su nisa da Masallaci wurin tafiya, bari na kawo maka labarin yaran salimata a lokacin da sukaso tashi su dawo kusa da Masallaci sai labarin hakan ya isa zuwa ga manzon Allah s.a.w sai yace masu lallai naji labarin cewa kuna son tashi ku dawo kusa da Masallaci, sia sukace eh haka ne ya manzon Allah Haqiqa munso haka sai yace masu:

« يَا بَنِى سَلِمَةَ دِيَارَكُمْ تُكْتَبْ آثَارُكُمْ دِيَارَكُمْ تُكْتَبْ آثَارُكُمْ ».

Ma’ana: "yaku yayan salimata ku zauna a gidajen ku za'a rubuta maku Ladan ku, lallai ku zauna a gidajen ku za'a rubuta maku ladan ku"[25],

---

Muslim ne ya rawaito shi (666) [23]
Buhari da muslim ne suka rawaito shi[24]
Muslim da ahmad da ibn kuzaima da ibn hibban ne suka rawaito shi [25]

An karvo daga jAbur Xan Abdullahi Allah ya kara masu yarda yace: gidajen su ya kasance nesa da Masallaci sai makaso siyar da gidajenmu mu dawo kusa da Masallaci sai manzon Allah s.a.w ya hana mu yace:
Ma'ana:

Ma'ana: " lallai duk wani sahu naku Xanada daraja akan sa"[26] maganar Abu Musa Al'ash'ary Allah yakara masa yarda yana karfafa wannan Hadis cewa lallai manzon Allah s.a.w yace:

« إن أعظم الناس أجرا في الصلاة أبعدهم إليها مشيا فأبعدهم، والذي ينتظر الصلاة حين يصليها مع الإمام في جماعة أعظم أجرا من الذي يصليها ثم ينام »

Ma'ana: " wanda yafi lada cikin mutane cikin Salla shine wanda yafi su nisa da Masallaci kafin yazo, wanda kuma ya zauna yana jiran Sallah jiran yin Sallah da liman yafi lada akan wanda yayi Sallah ya tafi yayi Bacci"[27]
A cikin wata ruwaya kuma na Abu kuraib: (har sai yayi Salla tare da liman cikin Jama'a).

**2). Tsarki da natsuwa da tsron Allah lokacin zuwa Masallaci da kuma cikin Salla:**

Haqiqa Allah ya kwaxaitar akan kula da tsabtar jiki na bayyane da kuma zuciya cikin dukkanin yanayi, wannan kwaxaitar yafi karfi a lokacin daya ke alaka da dakin Allah Maxaukaki yadda kwaxaitar wan be tsayaba kawai akan tsarki ya ci gaba har zuwa umurni dayin kwalliya a lokacin zuwa Masallaci, Allah Maxaukaki yace:

[26] Muslim da Ahmad ne suka rawaito shi
[27] Buhari da muslim ne suka rawaito shi

﴿ ۞ يَٰبَنِيٓ ءَادَمَ خُذُواْ زِينَتَكُمۡ عِندَ كُلِّ مَسۡجِدٖ ٣١ ﴾

Ma’ana: " yaku yan Adam ku rika yin kawa a lokacin zuwa ko wani Salla"[28].

Amma abun takaici ne zamu rika gani cikin wannan zamani cewa dayawa daga cikin maSallata suna zuwa Masallaci cikin warin zufa ko kuma mai safa wanda yake canza Masallaci daga matsayinsa na dakin Allah wanda aka sanyashi ya zama wurin natsuwa da sukunin zuciyan mutane a cikin sa. Kasani cewa ya kai Xan uwa Mai daraja cewa a lokacin da natsuwa da sukunin zuciya suka tabVata Sallah zai kasance a lokacin cikin natsuwa da sukuni shima kamar yadda manzon Allah s.a.w da girma ya siffata haka cikin faxinsa ga bilall Allah ya kara masa yarda:

"أَرِحْنَا بِهَا يَا بِلَالُ الصَّلَاةَ"

Ma’ana: " tashi ya bilal ka natsar damu da Salla"[29].

Kuma domin rai ta shirya yin Salla manzon Allah s.a.w yayi umurni da zuwa masallci cikin natsuwa da ladAbu, an karvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda daga manzon Allah s.a.w yace:

« إذا سمعتم الإقامة ، فامشوا وعليكم السكينة ، فما أدركتم فصلوا ، وما فاتكم فأتموا »

Ma’ana: " idan kukaji ikima to ku tafi zuwa ga Salla da natsuwa da ladabi kada kuyi sauri, Abunda kuka riske ku Sallata Abunda ya wuce ku sai ku cika"[30].

Wanda yake bibiyan Hadisn daya gaVata zaiga cewa manzon Allah s.a.w ya gaVatar da natsuwa akan riskan Salla

[28] Suratul a'araf ayata 31

[29] Abu dawud ne ya rawaito shi (4986)

[30] Buhari ne ya rawaito shi (636)

cikin mutane dukda cewa riskan Salla cikin mutane yana daga cikin falala Mai girma musamman ma kabbarar harama.

**3). Kiran Salla:**

Kiran Salla shine sanar da shigan lokacin Salla, kuma alama ce har wayau da yake nuna musulunci gari wanda ake kiran Salla acikinta, kuma alama ne da yake nuna tsayuwar alamomin Allah acikin gari. Masu kiran Salla sune aminai akan shigar lokacin Sallah, da kiran Sallar su ne ake sanin lokacin Salla ya shiga sai masu Azumi su sha ruwa ko kuma a kama baki daga cin Abunci da shan ruwa.
Dalili kuma akan falalar kiran Salla da masu kiran Salla shine Hadisn da aka karvo daga mu'awiya Allah ya kara masa yarda yace: naji manzon Allah s.a.w yana cewa:

« الْمُؤَذِّنُونَ أَطْوَلُ النَّاسِ أَعْنَاقًا يَوْمَ الْقِيَامَةِ »

Ma'ana"masu kiran Salla sunfi kowa tsayin wuya ranan Al-qiyama"[31]. an kuma shar'anta ga wanda yaji kiran Salla ya fadi abunXan aka rawaito daga JAbur Allah ya kara masa yarda manzon Allah s.a.w yace:

مَنْ قَالَ حِينَ يَسْمَعُ النِّدَاءَ اللَّهُمَّ رَبَّ هَذِهِ الدَّعْوَةِ التَّامَّةِ وَالصَّلاَةِ الْقَائِمَةِ آتِ مُحَمَّدًا الْوَسِيلَةَ وَالْفَضِيلَةَ وَابْعَثْهُ مَقَامًا مَحْمُودًا الَّذِي وَعَدْتَهُ حَلَّتْ لَهُ شَفَاعَتِي يَوْمَ الْقِيَامَةِ.

Ma'ana: " Duk wanda ya fada idan yaji kiran Salla: ya Allah ubangijin wannan da'awa cikakkiya da Salla tsayayye Karva Muhammad dama da falala ka kuma tayar dashi wuri na godiya da yabo wanda kayi masa alkawari, lallai cecu ta ta tabVata agareshi ranar Al-qiyama"[32], zai samu ceton

---

Muslim da ibn majjah ne suka rawaito shi [31]
Buhari da abu dawud da tirmizi da nasa'I ne suka rawaito shi[32]

manzon Allah s.a.w ranan Al-qiyama da wannan in Allah ya yarda, kuma wanene yafi mu bukatar Mai ceco a wannan rana?

**(4). Salla cikin jam'i:**

An karvo Hadis daga Abu Huraira Allah yakara masa yarda yace: manzo Allah s.a.w yace:

لَقَدْ هَمَمْتُ أَنْ آمُرَ بِالصَّلاَةِ فَتُقَامَ ثُمَّ أُخَالِفَ إِلَى مَنَازِلِ قَوْمٍ لاَ يَشْهَدُونَ الصَّلاَةَ فَأُحَرِّقَ عَلَيْهِمْ

Ma’ana: "Haqiqa nayi yukurin umurni da atsai da Salla sai na umurci wani yayima mutane Salla ni kuma nafita nida wasu mazaje da abun rura wuta mu kona gidajen wanda basu fita Salla ba cikin jam'i"[33]

a cikin wata ruwaya kuma yace (ba dan matan dake cikin gidajen ba da yara).

A cikin wannan Hadisn daya gaVata mun fahimci wajabcin yin Sallah cikin jam'i da Jama’a sai dai da wani uzuri na shari'a, kamar yashin lafiya wacce ta hana Mutum tafiya ko motsi, ko kuma tafiya ko kuma makahon da be samu Xan jagora ba zuwa Masallaci cikin mafi ingancin maganganun malamai. Hakan ya ishe ka sanin cewa lallai kanayin asaran lada masu dunbin yawa ta hanyar barin yin Salla cikin Jama’a an karvo Hadis daga Abdullahi Xan umar Allah ya kara masu yarda cewa manzon Allah s.a.w yace:

«صَلاَةُ الْجَمَاعَةِ أَفْضَلُ مِنْ صَلاَةِ الْفَذِّ بِسَبْعٍ وَعِشْرِينَ دَرَجَةً ».

33 Muslim da ibn majjah da nasa'I da ahmad ne suka rawaito shi

Ma’ana: " Sallar Jama’a tafi Sallar Mutum daya falala da daraja ashirin da bakwai"[34].

(5) **sammakon zuwa Sallah:**

An karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda cewa manzon Allah s.a.w yace:

لَوْ يَعْلَمُ النَّاسُ مَا فِي النِّدَاءِ وَالصَّفِّ الأَوَّلِ ثُمَّ لَمْ يَجِدُوا إِلاَّ أَنْ يَسْتَهِمُوا عَلَيْهِ لاَسْتَهَمُوا وَلَوْ يَعْلَمُونَ مَا فِي التَّهْجِيرِ لاَسْتَبَقُوا إِلَيْهِ وَلَوْ يَعْلَمُونَ مَا فِي الْعَتَمَةِ وَالصُّبْحِ لأَتَوْهُمَا وَلَوْ حَبْوًا

Ma’ana: " da ace mutane sun san Abunda ke cikin kiran Salla na dunbin lada da sahun farko sa'an ace bazasu samu ba sai sunyi kuri'a a tsakanin su da sunyi wannan kuri'a kuwa a tsakanin su, da ace kuma sun san Abunda ke cikin sammakon zuwa Salla na dunbin lada da sun rika gaggawan yin sammako"[35], Cikin wannan Hadisn a kwai dalili akan falalar sahun farko da lada Mai girma akan haka da kuma falalar yin sammakon fita Salla kamar kana saurin samun sahun farko shi kaxai kawai, har wayau Hadisn Abu Huraira yana kara nuni akan falalar haka, manzon Allah s.a.w yace:

«خَيْرُ صُفُوفِ الرِّجَالِ أَوَّلُهَا وَشَرُّهَا آخِرُهَا وَخَيْرُ صُفُوفِ النِّسَاءِ آخِرُهَا وَشَرُّهَا أَوَّلُهَا».

Ma’ama: " mafi alheri sahun maza shine sahun farko mufi sharrin sahun maza kuma shine na karshe, sannan mafi

Buhari da muslim da nasa'I ne suka rawaito shi[34]
Buhari da muslim da abu dawud da nasa'I da trimizi ne suka rawaito shi [35]

alherin sahun mata shine sahun karshe kuma mafi sharrin sahun su shine na farko"[36].

- **Sammako zuwa Sallar jumma'a:**

Lallai kamar yadda ka sani ne ya kai Xan uwa Mai daraja irin falalar dake cikin ranan jumma'a akan sauran ranakun mako saboda Hadisn da rawaito daga Abu Huraira Allah yakara masa yarda yace, manzon Allah s.a.w yace:

« خير يوم طلعت فيه الشمس يوم الجمعة ، فيه خلق آدم ، وفيه أهبط ، وفيه تاب عليه ، وفيه تقوم الساعة »

Ma’ana: " mafi alherin rana shine ranar jumma'a a ranar ne Allah ya halicci Adam kuma a ranar ne aka shigar dashi aljanna kuma a ranar ne aka fitar dashi daga cikinta"[37].

Wannan rana ranar murnan mu da farin yaku al'ummar musulmai, Haqiqa Allah ya zaban mana wannan rana akan sauran al'ummar da suka gabace mu, yahudawa ranar asabar ce tasu kiristoci kuma ranar lahadi ce tasu, manzon Allah s.a.w yace:

« أضل ٱللَّهَ عن الجمعة من كان قبلنا فكان لليهود يوم السبت وكان للنصارى يوم الأحد فجاء ٱللَّهَ بنا فهدانا ليوم الجمعة فجعل الجمعة والسبت والأحد وكذلك هم تبع لنا يوم القيامة »

Ma’ana: " Allah ya Vatar da mutanen dake gabanin mu akan ranar jumma'a, yahudawa sun zAbu ranar sati su kuma kiristoci sun zAbu ranar lahadi, sai Allah ya kawo mu ya

---

Muslim da nasa'I da abu dawud ne suka rawaito shi[36]
Muslim da nasa'I ne suka rawaito shi [37]

kuma shiryar damu da wannan rana kuma suna bayan mu a ranar Al-qiyama"[38].

Haqiqa Allah Maxaukaki ya kebance wannan rana da Sallar jumma'a wacce take a matsayin wurin taro na sati sati domin musulmai suji khuduba da wa'azi daga liman, kuma Haqiqa Allah Maxaukaki ya sanya wa masu sammako zuwa wannan Salla ta jumma'a lada Mai girma yadda abu Huraira yake cewa manzon Allah s.a.w yace:

مَنِ اغْتَسَلَ يَوْمَ الْجُمُعَةِ غُسْلَ الْجَنَابَةِ ، ثُمَّ رَاحَ فِي السَّاعَةِ الأُولَى ، فَكَأَنَّمَا قَرَّبَ بَدَنَةً ، وَمَنْ رَاحَ فِي السَّاعَةِ الثَّانِيَةِ فَكَأَنَّمَا قَرَّبَ بَقَرَةً ، وَمَنْ رَاحَ فِي السَّاعَةِ الثَّالِثَةِ فَكَأَنَّمَا قَرَّبَ كَبْشًا أَقْرَنَ ، وَمَنْ رَاحَ فِي السَّاعَةِ الرَّابِعَةِ فَكَأَنَّمَا قَرَّبَ دَجَاجَةً ، وَمَنْ رَاحَ فِي السَّاعَةِ الْخَامِسَةِ فَكَأَنَّمَا قَرَّبَ بَيْضَةً ، فَإِذَا خَرَجَ الإِمَامُ حَضَرَتِ الْمَلائِكَةُ يَسْتَمِعُونَ الذِّكْرَ.

Ma'ana: " Duk wanda yayi wanka ranar jumma'a wanka irin ta janaba sannan ya fita zuwa Masallaci kamar ya yanka rakumi ne yayi sadaka da ita wanda kuma ya zama na biyu kamar ya yanka sanuwa ce wanda kuma ya zama na uku kamar ya yanka rago ne wanda kuma ya zama na hudu kamar ya yanka kaza ne wanda kuma ya zama na biyar kamar yayi sadaka da kwai ne idan liman yah au minbari sai mala'iku suzo sauraron khuduba"[39].

Ausa assakafi Allah ya kara masa yarda yana cewa cikin falalar ranar jumma da wasu daga cikin ayyukan wannan rana cewa manzon Allah s.a.w yace:

---

Muslim da nasa'I da ibn majjah ne suka rawaito shi [38]
Buhari da muslim da abu dawud ne suka rawaito shi[39]

مَنِ اغْتَسَلَ يَوْمَ الْجُمُعَةِ وَغَسَلَ ، وَغَدَا وَابْتَكَرَ ، وَمَشَى وَلَمْ يَرْكَبْ ، وَدَنَا مِنَ الإِمَامِ ، وَأَنْصَتَ وَلَمْ يَلْغُ ، كَانَ لَهُ بِكُلِّ خُطْوَةٍ عَمَلُ سَنَةٍ.

Ma'ana: " Duk wanda yayi wanka ranar jumma'a ya kuma yi sammakon fita zuwa Masallaci sannan kuma ya tafi a kasa be hau abun hawa ba ya kuma saurari liman beyi wata Magana ba a lokacin khuduba ya kasance duk takunsa daya tana daidai da Ladan aikin shekara daya na Mutumin dayayi Salla da Azumi acikin ta"[40].

An karvo daga salmanul farisi Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

مَنِ اغْتَسَلَ يَوْمَ الْجُمُعَةِ فَأَسْبَغَ وَتَطَهَّرَ وَتَطَيَّبَ مِنْ طِيبِ أَهْلِهِ ، وَخَرَجَ إِلَى الْجُمُعَةِ فَلَمْ يُفَرِّقْ بَيْنَ اثْنَيْنِ ، ثُمَّ صَلَّى مَا قُدِّرَ لَهُ حَتَّى يَخْرُجَ الإِمَامُ غُفِرَ لَهُ مَا بَيْنَهُ وَبَيْنَ الْجُمُعَةِ الأُخْرَى.

Ma'ana: " Mutum bazayyi wanka ba ranar jumma yana tsarki da kuma kwalliya ya gyara gashin kansa ya kuma sanya turare sannan kuma ya fita zuwa Masallaci be raba dayan biyu ba, sa'annan ya Sallaci Abunda aka wajabta masa sannan kuma yayi shiru a lokacin da liman keyin khuduba face an gafarta masa Abunda ya aikata na zunubi a tsakanin jumma'ar da wata jumma'ar"[41].

## <u>6) sallolin nafila cikin ko wace rana (sunan alrawatib):</u>

Yayin da sallolin mu suka kasance cikin mafiya lokuta suna haduwa da wasu ayyuka na nakasu, imam dai rashin ciki wani wajibi ko kuma barin aikata wani sunna ko kuma

---

[40] Abu dawud da tirmizi da ibn majjah da nasa'I ne suka rawaito shi

[41] Buhari ne ya rawaito shi(883)

wasiwasin Shaidan ko kuma tunani cikin al'amuran Duniya da kuma shagalta da Duniya da mantawa da al'amuran Salla da Kankan dakai, saboda haka ne ake samun lada rAbu da rAbu wanda yake karuwa da raguwa gwargwadon natsuwar Mutum da Kankan dakai a cikinta da mayar da hankalin sa akanta da zuwa da dukkanin Abunda ake bukata a cikinta kamar yadda manzon Allah s.a.w yayi nashi Sallar wanda yake cewa:

« صَلُّوا كَمَا رَأَيْتُمُونِى أُصَلِّى ».

Ma’ana: " kuyi Salla kamar yadda kuka ga ina Salla"[42].

Dalili akan haka shine faxin Ammar Xan Yasir Allah ya kara masu yarda cewa manzon Allah s.a.w yace:

Ma’ana: " lallai bawa yana gama Sallar sa amma ba'a rubuta masa ladaba sai na rabinta, ko kuma daya bisa ukunta haka yake ragewa har yace xaya bisa goman ta"[43].

Domin a toshe wannan nakasun da aka samu na Ladan Salla manzon Allah s.a.w ya shar'anta mana yin wannan nafiloli a kullum wanda akeyin su gabanin Salla ko kuma bayanta wacce zata cike ma Mutum wannan nakasu daya samu cikin Sallar sa kuma ta kara masa nauyin ma'aunin sa, raka'a ce goma sha biyu cikin ko wace rana wacce akeyin su kamar haka:

Raka'a biyu kafin Sallar asuba, an karvo daga Aisha Allah ya kara mata yarda tace: manzon Allah s.a.w yace:

« رَكْعَتَا الْفَجْرِ خَيْرٌ مِنَ الدُّنْيَا وَمَا فِيهَا ».

---

[42] Buhari ne ya rawaito shi(631)
[43] Littafin iman na ibn taimiyya

-
Ma’ana: " Raka'a biyu ta alfijir tafi Duniya da Abunda ke cikinta alheri"[44]

- Raka'a hudu gabanin azahar da kuma raka'a biyu bayan Sallar azahar dalilin Hadisn Aliyu Allah ya kara masa yarda yace:

Ma’ana: " Manzon Allah s.a.w ya kasance yana Salla raka'a hudu gabanin azahar, kuma bayanta yayi ra'a biyu"[45] .

akwai wasu falaloli na daban akan yin wannan salloli kamar yadda Ummu hAbuba Allah yakara mata yarda ta fadi cewa manzon Allah s.a.w yace:

مَنْ صَلَّى أَرْبَعَ رَكْعَاتٍ قَبْلَ الظُّهْرِ وَأَرْبَعًا بَعْدَهَا حَرَّمَهُ ٱللَّهُ عَلَى النَّارِ.

Ma’ana: " Duk wanda yayi Salla raka'a hudu gabanin azahar sannan kuma bayanta yayi hudu Allah zai haramtawa wuta fuskar sa"[46].

- Raka'aiyu bayan magriba, Aisha Allah ya kara mata yarda tace:

Ma’ana: " Manzon Allah s.a.w ya kasance yana Sallar magriba sannan ya dawo gida yayi Salla raka'a biyu"[47].

- Raka'a biyu bayan isha'i, an karvo Hadis daga Aisha Allah ya kara mata yarda tace:

---

[44] Muslim da tirmizi da nasa'i ne suka rawaito shi
[45] Hadis ne hasan kuma tirmizi ne ya rawaito shi (424)
[46] Ibn majjah da abu dawud da tirmizi ne suka rawaito shi
[47] Ibn majjah ne ya rawaito shi (1164)

Ma’ana: " Manzon Allah ya kasance yana Salla raka'a biyu bayan isha'i"[48].

Akwai wani banbanci na daban da kuma lada Mai tarin yawa na wannan salloli na nafila saboda sun kasance sabAbu na shiga aljanna kamar yadda ummu HAbuba ta rawaito Allah ya kara mata yarda cewa taji manzon Allah s.a.w yana cewa:

« مَا مِنْ عَبْدٍ مُسْلِمٍ يُصَلِّى لِلَّهِ كُلَّ يَوْمٍ ثِنْتَىْ عَشْرَةَ رَكْعَةً تَطَوُّعًا غَيْرَ فَرِيضَةٍ إِلاَّ بَنَى ٱللَّهُ لَهُ بَيْتًا فِى الْجَنَّةِ أَوْ إِلاَّ بُنِىَ لَهُ بَيْتٌ فِى الْجَنَّةِ »

Ma’ana: "babu wani bawa da zayyi Salla na nafila raka'a goma sha biyu a kullum domin Allah bayan Sallar farilla face Allah ya gina masa gida cikin aljanna"[49].

Haka kuma Salla raka'a hudu gabanin Sallar la'asar inda Abdullahi Xan Umar Allah ya kara masu yarda yake cewa manzon Allah s.a.w yace:

رحم ٱللَّهُ امرءا صلى قبل العصر أربعا

Ma’ana: " Allah yajikan Mutumin da yayi Salla raka'a hudu gabanin la'asar"[50].

Duk Abunda ya karu akan wannan adadin na raka'o'i to lallai Karin alheri ne da albarka da kusanci ga bawa zuwa ga ubangijin sa kuma yana da lada Mai girma akan haka, an karvo Hadis daga sauban Allah ya kara masa yarda yace: na

---

Tirmizi ne ya rawaito shi(436) [48]
Muslim da nasa'I ne suka rawaito shi [49]
Abu dawud da tirmizi ne suka rawaito shi[50]

tambayi manzon Allah s.a.w cewa wani aiki ne yafi soyuwa zuwa ga Allah sai yacemun:

(( عَلَيْكَ بِكَثْرَةِ السُّجُودِ؛ فَإِنَّكَ لَنْ تَسْجُدَ لِلهِ سَجْدَةً إلاَّ رَفَعَكَ ٱللَّهَ بِهَا دَرجَةً ، وَحَطَّ عَنكَ بِهَا خَطِيئَةً ))

Ma'ana: " ka yawaita sujjada saboda bazakayi sujjada daya ba domin Allah face Allah ya daga darajar ka da ita ya kuma kankare maka zunuban ka da ita"[51].

حَدَّثَنِى رَبِيعَةُ بْنُ كَعْبٍ الأَسْلَمِىُّ قَالَ كُنْتُ أَبِيتُ مَعَ رَسُولِ ٱللَّهَ –صلى ٱللَّهَ عليه وسلم– فَأَتَيْتُهُ بِوَضُوئِهِ وَحَاجَتِهِ فَقَالَ لِى « سَلْ ». فَقُلْتُ أَسْأَلُكَ مُرَافَقَتَكَ فِى الْجَنَّةِ. قَالَ « أَوَغَيْرَ ذَلِكَ ». قُلْتُ هُوَ ذَاكَ. قَالَ « فَأَعِنِّى عَلَى نَفْسِكَ بِكَثْرَةِ السُّجُودِ ».

An karvo kuma daga Rubai'ata Xan ka'ab Al-aslami Allah ya kara masa yarda yace: na kasance ina kwana tare da manzon Allah s.a.w sai nazo masa da ruwan Alwala da na biyan bukatar sa sai yacemun:

Ma'ana: "ka roki Abunda kake so, sai nace: ina roqon na zama makwabcin ka a aljanna, sia yacemun: akwai wani abu kuma banda wannan sai nace masa: a'a wannan ne kawai, sai yacemun: to ka dage da neman haka ta hanyar yawaita sujjada"[52].

Sannan kuma sujjada itace mafi kusancin wurin wanda Mutum ke kusantar ubangijin sa acikinta, an karvo Hadis daga Abu Huraira Allah yakara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

---

[51] Muslim da ibn majjah da nasa'I ne suka rawaito shi

[52] Muslim da nasa'I ne suka rawaito shi

« أقرب ما يكون العبد من ربه عز وجل وهو ساجد ، فأكثروا الدعاء »

Ma’ana: " mafi kusancin wurin da Mutum ke kasancewa da ubangijin sa shine lokacin sujjada saboda haka ku yawaita addu'a a cikinta"[53].

**7) zama cikin Masallaci tsakanin salloli:**

Hakan yana da falala Mai girma a wurin Allah yadda manzon Allah s.a.w yace:

« لا يزال العبد في صلاة ما دام في مصلاه لم يحبسه إلا انتظار الصلاة ، والملائكة معه تقول : اللهم اغفر ، اللهم ارحمه ما لم يحدث »

Ma’ana: " bawa bazai kasance ba cikin addu'a matukar yana cikin Masallaci yana jiran Sallah mala'iku zasu rika cewa: ya Allah ka gafarta mas aka mashi rahama har sai ya fita ko kuma Alwalar sa ya warware"[54].

Kuma akwai hadisai masu yawa wanda suka tattaro falalan Abunda muke fada daga cikin su akwai faxin abu Huraira Allah ya kasa masa yarda cewa manzon Allah s.a.w yace:

« صلاة الرجل في جماعة تزيد على صلاته في بيته ، وصلاته في سوقه خمسا وعشرين درجة ، وذلك بأن أحدكم إذا توضأ ، فأحسن الوضوء ، وأتى المسجد ، لا يأتيه إلا للصلاة ، لا ينهزه إلا الصلاة ، لم يخط خطوة إلا رفع له بها درجة ، أو حط عنه بها خطيئة ، حتى يدخل المسجد ، فإذا دخل المسجد كان في صلاة ، فإذا كانت الصلاة تحبسه »

---

Muslim da abu dawud da nasa'I ne suka rawaito shi[53]
Muslim da nasa'I ne suka rawaito shi[54]

Ma’ana: " Sallar Mutum cikin Jama’a ana nunka ta akan Sallar sa shi kaxai agida ko kuma a kasuwa akan nunki ashirin da biyar, hakan kuwa ya kasance ne saboda idan yayi Alwala ya kyautata Alwalar sa sannan ya fita zuwa Masallaci babu kuma Abunda ya fitar dashi sai Sallah to bazaiyi taku ba face an daga darajar sa da ita kuma a kankare masa zunuban sa da ita, sannan idan kuma yayi Sallal mala'iku bazasu gushe ba suna masa addu'a matukar yana cikin Masallaci suna faxin cewa ya Allah kayi masa rahama, dayan ku bazai gushe ba cikin addu'a matukar yana jiran Salla"[55].

An kuma karvo daga Abu Huraira daga manzon Allah s.a.w cewa:

« إذا توضأ الرجل فأحسن الوضوء ، ثم أتى المسجد لا يريد إلا الصلاة ، لم يخط خطوة إلا رفع بها درجة ، وحط عنه بها خطيئة »

Ma’ana: " I dan Mutum yayi Alwala ya kuma kyautata Alwalar sannan ya fita zuwa Masallaci babu Abunda ya fitar dashi sai Salla bazayyi wani taku ba face an daga darajar sa da ita sannan kuma a kankare masa zunuban sa da ita"[56].

An kuma kar karvo daga gareshi har wayau daga manzon Allah s.a.w yace:

« ألا أدلكم على ما يمحو ٱللَّهُ به الخطايا ويرفع به الدرجات ؟ » ، قالوا : بلى ، قال : « إسباغ الوضوء في المكاره ، وكثرة الخطا إلى المساجد ، وانتظار الصلاة بعد الصلاة ، فذلكم الرباط »

---

[55] Buhari da muslim ne suka rawaito shi

[56] Ibn majjah ne ya rawaito shi(281)

Ma’ana: " shin bazan nuna maku Abunda Allah yake kankare maku zunuban ku ba dashi ya kuma daga darajar ku dashi, sai sukace eh fada mana ya manzon Allah sai yace kyautata Alwala a lokacin kin taba ruwa da kuma yawon tafiya zuwa Masallaci da jiran Salla bayan Salla wannan tanadi ne"[57].

- **Zaman cikin Masallaci bayan Sallar asuba da kuma yin Salla raka'a biyu bayan rana ta fito:**

An karvo Hadis daga Anas Xan malik Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

Ma’ana: " Duk wanda yayi Sallar asuba cikin Jama’a sannan ya zauna yana ambaton Allah har rana ta fito sa'annan yayi Sallah raka'a biyuya kasance yana da Ladan irin na aikin hajji da umura, sai yace: manzon Allah s.a.w yace: lada cikakke cikakke cikakke"[58].

## c) Sallar walaha:

An karvo Hadis daga Zaidu Xan Arkama Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah ya fita zuwa ga mutanen kuba ya tarar suna Salla sai yace:

Ma’ana: " Sallar bayin Allah masu yawan ibada idan hantsi ta fito"[59].

Wannan itace Sallar walaha wacce manzon Allah s.a.w yayima sahAbun sa abu Huraira wasiyya akanta da ya

Muslim da nasa'I da tirmizi ne suka rawaito shi [57]
Tirmizi ne ya rawaito shi kuma albani ya inganta shi[58]
Muslim ne ya rawaito shi(784) [59]

kityaye ta, an karvo daga gareshi Allah ya kara masa yarda yace:

أَوْصَانِى حَبِيبِى –صلى ٱللَّهَ عليه وسلم– بِثَلاَثٍ لَنْ أَدَعَهُنَّ مَا عِشْتُ :........

ومنهاَ صَلاَةِ الضُّحَى

Ma'ana: " masoyina yamun wasiyya da abubuwa guda uku.... Ya ambaci Sallar walaha a cikinsu"[60].

Falalar wannan sunna kuma shine Hadisn da aka karvo daga Abu zarri Allah ya kara masa yarda cewa manzon Allah s.a.w yace:

Ma'ana: " ko wace gaVata jikin Mutum yana tashi a kwai sadaka akanta, ko wace tasbihi sadaka ce, kuma ko wace faxin alhamdulilla sadaka ce, haka kuma ko wace faxin la'ilaha illah sadaka ce, faxin Allahu akbar sadaka ce, yin umurni da kyakyawan aiki sadaka ce, hani da mummunan aiki sadaka ce, sannan Sallah raka'a biyu na Sallar walaha ya wadatar daga dukkanin wannan ayyuka"[61].

Ka wassara ka gani yakai Xan uwa Mai daraja yace ya zama dole ne tayi sadaka daga dukkanin gabbai na jikin ka wanda sukakai 360!!! Kila bazaka iya cika wannan sadakar ba sai Allah ya tausaya maka ya karramaka da shar'anta ma Sallar sunna ta walaha domin da fansheka daga wannan sadakokin.

## d) Salla cikin dare:

Jami'ussahih (1178) albani kuma ya inganta shi[60]
Muslim ne ya rawaito shi da abu dawud [61]

Daga cikin salloli masu falala akwai Salla cikin tsakiyar duhun dare, musamman ma cikin ukun karshe na dare lokacin natsuwa da tsarkakan zuciya da jin dadin ganawa da Allah, kuma Haqiqa Allah ya yAbu muminai da Sallar su cikin dare yace:

﴿ كَانُوا۟ قَلِيلًا مِّنَ ٱلَّيْلِ مَا يَهْجَعُونَ ۝١٧ وَبِٱلْأَسْحَارِ هُمْ يَسْتَغْفِرُونَ ۝١٨ ﴾

Ma'ana: " sun kasance basa Bacci cikin wani Vangare kaxan na dare (17) kuma suna Salla da istigfari cikin karshen dare gab da fitowar ajfijir (18)[62]"

kuma hakan yana cikin aikin annAbun mu wanda aka wajabta masa, Allah Maxaukaki yace:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلْمُزَّمِّلُ ۝١ قُمِ ٱلَّيْلَ إِلَّا قَلِيلًا ۝٢ نِّصْفَهُۥٓ أَوِ ٱنقُصْ مِنْهُ قَلِيلًا ۝٣
أَوْ زِدْ عَلَيْهِ وَرَتِّلِ ٱلْقُرْءَانَ تَرْتِيلًا ۝٤ ﴾

Ma'ana: " ya kai Mai lulluva cikin dare (1) ka tashi kayi Salla cikin dare (2) a cikin rAbun sa ko kuma ka rage kaxan daga cikin sa (3) ko kuma ka kara akan haka ka karanta Al-qur'ani cikin rerawa (4)[63].

Akan falalar Sallar dare kuma Abu Huraira yace: manzon Allah s.a.w yace:

أَفْضَلُ الصَّلَاةِ بَعْدَ الْفَرِيضَةِ صَلَاةُ اللَّيْلِ

---

Suratul zariyat [62]
Suratul muzammil[63]

Ma’ana: " mafi falalar Salla bayan Sallar farilla itace Sallar dare"[64].

Sannan kuma manzon Allah s.a.w ya yAbu sahAbu Abdullahi Xan Umar akan Sallar dare da cewa:

نعم الرجل عبدالله ، لو كان يصلي من الليل

Ma’ana: " Madalla da Bawan Allah Abdullahi da ace yana tashi cikin dare yana Salla"[65].

Acikin wata ruwaya kuma yace:

لاَ تَكُنْ مِثْلَ فُلاَنٍ كَانَ يَقُومُ اللَّيْلَ فَتَرَكَ قِيَامَ اللَّيْلِ.

Ma’ana: (kada ka zama irin wane ya kasance yana tashi cikin dare yana Salla sai yabari).

## 2) Ayyuka masu alaka da Azumi:

### a. falalar Azumin nafila baki daya:

an karvo Hadis daga Abu sa'eed alkhudri Allah ya kara masa yarda yace: naji manzon Allah s.a.w yana cewa:

Ma’ana: " babu wani Mutum da zayyi Azumi a wani rana domin Allah face Allah ya nesantar dashi daga wuta na tsawon tafiyan kwan saba'in da wannan Azumi nashi"[66].

[64] Muslim da abu dawu da tirmizi da nasa'I ne suka rawaito shi
[65] Buhari da muslim ne suka rawaito shi
[66] Buhari da muslim ne suka rawaito shi

Yazo kuma cikin Hadisl kudusi Allah Maxaukaki yana cewa:

كُلُّ عَمَلِ ابْنِ آدَمَ لَهُ إِلاَّ الصِّيَامَ هُوَ لِي وَأَنَا أَجْزِي بِهِ

Ma’ana: "dukkanin ayyukan Xan Adam nashi ne sai dai Azumi lallai shi nawa ne zan saka masa dashi"[67].

Azumin nafila ya shiga cikin wannan falala da yardar Allah.

Azumi kariya gaMai da fadawa cikin alfasha da abubuwan da Allah ya haramta, manzon Allah s.a.w yace:

يَا مَعْشَرَ الشَّبَابِ مَنِ اسْتَطَاعَ مِنْكُمُ الْبَاءَةَ فَلْيَتَزَوَّجْ ، وَمَنْ لَمْ يَسْتَطِعْ فَعَلَيْهِ بِالصَّوْمِ فَإِنَّهُ لَهُ وِجَاءٌ.

Ma’ana: " yaku taron samari Duk wanda ya samu dama acikin kun a aure to yayi auren sa saboda shi yafi zama kariya ga ganin sa da kuma farjin sa, wanda kuma be samu dam aba to ya rika Azumi domin ita kariya ce a gareshi"[68].

Haka kuma Azumi na ladabtar da zuciya rashin yin barna wurin more Duniya saboda tana tunatar damu halin yan uwan mu fakirai da talakawa wanda basu samu Abunda zasu saka abaka ba ko kuma su jika makoshin su. Mu'azu Xan Jabal Allah yakara masa yarda yace lokacin da mutuwa tazo mashi yana kuka: (ina kuka ne akan zan daina yin Azumi acikin lokaci Mai tsananin zafi da kuma goganya da malami cikin tsangaya na ilimi). An karvo daga Amir Xan Abdulkais Allah ya kara masa yarda cewa lokacin da mutuwa tazo masa yace: (wallahi bawai ina kuka bane

Buhari da muslim ne suka rawaito shi[67]
Buhari da muslim da abu dawud da ahmad ne suka rawaito shi[68]

domin tsoro mutuwa ina kuka ne akan barin da zanyi nayin Azumi cikin tsananin zafi da tsayuwan dare)[69].

## b) falalan Azumin ashura:

an karvo Hadis daga Xan Abbas Allah ya kara masu yarda yace: lokacin da manzon Allah s.a.w yazo garin madina yaga yahudawa suna azumtar ranar ashurasai yace masu Mai yasa kuke azumtar wannan rana ku kuwa? Sai sukace wannan shine ranar da Allah ya tsiratar da annAbun sa Musa da bani isra'ila daga makiyin su sai Musa amincin Allah ya kara tabVata a gareshi ya azumce shi, sai manzon Allah s.a.w yace: " lallai mu mukafi ku cancanta da kusanci da Musa, sai manzon Allah ya azmunci wannan rana kuma yayi umurni da azumtar wannan rana"[70]. Sannan domin sabama yahudawa cikin ayyukan su sai manzon Allah s.a.w yayi umurni da arika azumtar wani rana tare dashi inda yace: " idan Allah ya rayani zuwa shekara Mai zuwa zan azumci ranar tasu'a"[71]watan tare da ashura a hade.

Ibn kayyim Allah yayi masa rahama yace: (matakin Azumin guda uku ne wanda yafi kamala shine azumtar rana daya kafin ranar ashura da rana daya bayansa, sai kuma azumtar ranan tasu'a da ashura a wannan mataki ne dayawa daga cikin hadisai sukayi nuni akai sai kuma azumtar ranar ashura kawai) kuma acikin falalar Azumin wannan rana ne manzon Allah s.a.w yace:

---

Alzam'ul jawahir shine azumi a tsananin zafi kamar yadda yazo cikin Hadisn[69]
Buhari da muslim da abu dawud da ahmad ne suka rawaito shi[70]
Muslim ne ya rawaito shi da abu dawud[71]

Ma'ana: " ina tsammanin Allah zai kankare ma mutun zunubansa na shekaran da ya gaVata dashi"[72].

## c) Azumin sittu shawwal:

an karvo Hadis daga Abu Ayyub al Ansari Allah ya kara masa yarda cewa manzon Allah s.a.w yace:

« مَنْ صَامَ رَمَضَانَ ثُمَّ أَتْبَعَهُ سِتًّا مِنْ شَوَّالٍ كَانَ كَصِيَامِ الدَّهْرِ ».

مَنْ صَامَ رَمَضَانَ ، ثُمَّ أَتْبَعَهُ سِتًّا مِنْ شَوَّالٍ ، فَذَلِكَ كَصِيَامِ الدَّهْرِ.

Ma'ana: " Duk wanda yayi Azumin watan Ramadan sannan ya bishi da Azumi guda shida cikin watan shawwal kamar yayi Azumin zamani ne baki dayan sa"[73].

Saboda duk aiki daya ana nunka ladar sa ne sau goma kenan Azumin Ramadan ya zama Azumin wata goma shi kuma sittu shawwal a madadin Azumin wata biyu sai ya baka shekara daya kenan cikakke idan Mutum yana haka cikin duk shekara sai yazama Azumin zamani kenan baki daya.

Saboda haka kayi kokari yakai Xan uwa akan azumtar wannan Azumi domin samun lada Mai girma, sannan Mai gaggawa zai fara wannan Azumin ne washe garin ranar idi ga wanda yake jin tsoron kasala da kuma shagala. Anan wurin inason fadakarwa akan yin Azumi ranar idi wanda an haramta haka haka kuma da yin Azumi ranar jumma'a kawai shi kaxai sai dai Mutum ya hada da rana daya kafin sa ko kuma bayan sa, amma idan ranar jumma'ar ta kasance ranar yin wani Azumi ne misali ta kasance ranar arfa ko

---

Muslim ne ya rawaito shi(1162) 72

Malaman Hadis shida duk sun rawaito shi sai buhari kaxai73

kuma Mutum yayi bakance zayyi a zumi a wani rana sai Allah ya kaddara wanna ranar ta zama ranar jumma'a to wannan ya halatta yayi Azumi a ranar jumma'a[74] saboda faxin manzon Allah s.a.w cewa:

« لاَ يَصُومُ أَحَدُكُمْ يَوْمَ الْجُمُعَةِ إِلاَّ أَنْ يَصُومَ قَبْلَهُ يَوْمًا أَوْ بَعْدَهُ يَوْمًا ».

Ma’ana: " kada xayanku yayi Azumi ranar jumma'a sai dai idan ya hadashi da ranan da yake bayan sa ko kuma gabansa"[75]. Dayawa daga cikin malamai sun tafi akan cewa wannan hanin tanan wurin hani ce ta makaruhi ba hani bane na haramci.

## d) Azumin ranar arfa:

an shar'anta Azumin ranar arfa ga Mutum da ba alhaji ba, kuma wannan Azumi shine mafi falalar ayyukan gomaki koma na farkon watan zulhijja ga wanda ba alhaji ba (falalar Azumin kwanaki goma na farkon watan zulhijja bayani zai zo akan su nan gaba kaxan) ba'a shar'antawa alhaji azumtar wannan rana ba domin ya samu karfin yin ibada a wannan rana ta arfa. An karvo Hadis daga Abu katada Allah ya kara masa yarda yace an tambayi manzon Allah s.a.w gaMai da Azumin ranar arfa sai yace:

Ma’ana:" ina fatan Allah zai kankare zunuban shekaran data gaVata da wanda take binta da wannan Azumi ga bawa"[76].

**FADAKARWA:**

---

[74] Azumin bakance wajibi ne shi kuma azumin wajibi ba'a kayyade shi ba da daranan da aka karhanta azumi a cikin faxin wasu malamai

[75] Buhari da muslim ne suka rawaito shi

[76] Muslim ne ya rawaito shi (1162)

Wannan kankare zunuban da za'ayi kamar yadda ya gaVata anan da kuma Azumin ashura kananan zunubai ne ake kankare wa banda manya, su manyan zunubai dole ne sai Mutum ya tuba na Haqiqa akan su da kuma barin wannan ayyuka da yakeyi na zunubai da kuma niyyar cewa bazai kara komawa ba cikin wannan ayyuka da kuma mayar da hakkoki zuwa ga masu shi idan wannan laifin dayayi tana da alaka da hakkokin mutane.

## 3) Lokuta da wuraren da ake ruvanya Ladan ayyuka da kuma amsar addu'a:

### a). lokutan da ake ruvanya lada da amsar addu'a:

**1). Watan Ramadan:**

Kasani yakai Xan uwa lallai lada cikin watan Azumi suna nunkuwa, Haqiqa yazo cikin Hadis daga manzon Allah s.a.w cewa:

Ma’ana: " babu wani wata Mai alfarma ta dake zuwa ma musulmai kamar watan Ramadan sannan kuma babu wata wata mafi sharri da take zuwa ma munafikai kamar watan Ramadan"[77].

Saboda haka kayi kokari yakai Xan uwa Mai daraja akan riVatan wannan wata Mai girma ta hanyar yin ayyukan na Qwarai na salloli da sadaka da bada zakka da dukkanin aiki na Qwarai, godiya ta tabVata ga Allah wanda ya shiryar damu da wannan wata Mai girma ya kuma sanya hanyoyin bautan sa a ciki su zama masu sauki, an karvo Hadis daga

Ahmad ne ya rawaito shi (8350), kuma ibn huhaiza ya ingantashi da malam Ahmad asakir[77]

Abu Huraira Allah ya kara mashi yarda yace manzonn Allah s.a.w yace:

« إِذَا جَاءَ رَمَضَانُ فُتِّحَتْ أَبْوَابُ الْجَنَّةِ وَغُلِّقَتْ أَبْوَابُ النَّارِ وَصُفِّدَتِ الشَّيَاطِينُ ».

Ma'ana: " idan watan Ramadan tazo ana bude kofofin aljanna a kuma rufe kofofin wuta sannan a kulle Shaidanu"[78].

- **Yin umra cikin watan Ramadan:**

Daga cikin falalar Allah cikin nunka lada a watan Ramadan ya sanya yin umra cikin watan Ramadan tana daidai da aikin haji saboda faxin manzon Allah s.a.w ga ummu sinan a lokacin da ta rasa hajjin bankwana sai yace mata:

Ma'ana: " idan watan Ramadan yazo kije kiyi umra, domin umra cikin watan Ramadan tana dai dai da aikin hajji"

ko kuma yace:

Ma'ana: " dai dai take dayin aikin haji tare Xani"[79].

- **Daren lailatul kadari:**

Dare ce Mai girma, Ladan ayyukan mutane a cikin ta sunfi aikin su na wata dubu alheri (shekara tamanin da uku da wata hudu a kataice) Allah Maxaukaki yace:

﴿إِنَّآ أَنزَلۡنَٰهُ فِي لَيۡلَةِ ٱلۡقَدۡرِ ١ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا لَيۡلَةُ ٱلۡقَدۡرِ ٢ لَيۡلَةُ ٱلۡقَدۡرِ خَيۡرٞ مِّنۡ أَلۡفِ شَهۡرٖ ٣﴾

Muslim ne ya rawaito shi (1079) 78

Buhari da muslim da ahmad ne suka rwaito shi79

Ma'ana: " lallai mun saukar dashi cikin lailatul kadari (1) kuma Mai ya sanar dakai lailatul kadari (2) lailatul kadari tafi dare na wata dubu alheri (3)[80].

A cikinta ne aka saukar da Al-qur'ani zuwa ga saman Duniya, kuma acikinta ne ake zantar da dukkanin Abunda zasu auku cikin shekara Mai zuwa, Allah Maxaukaki yace:

إِنَّآ أَنزَلْنَٰهُ فِى لَيْلَةٍ مُّبَٰرَكَةٍ ۚ إِنَّا كُنَّا مُنذِرِينَ ﴿٣﴾ فِيهَا يُفْرَقُ كُلُّ أَمْرٍ حَكِيمٍ

Ma'ana: "lallai mun saukar dashi cikin wani dare Mai albarkalallai mun kasance masu gargadi (3) a cikin sa ne aka rarrabe dukkanin Abunda zai faru (4)[81].

Kuma Allah ya kebance wannan al'umma da wannan dare, imamu malik yace: ya isomun cewa manzon Allah s.a.w tsawon rayuwan al'ummar sa bekai na al'ummar da suka gabace mu ba sai Allah ya bashi lailatul kadari[82].

**2) kwanaki goma na farkon watan zulhijja:**

An kar Hadis daga Abdullahi Xan Abbas Allah yakara masu yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: " babu wasu ranaku wanda ayyukan Qwarai acikin su yafi soyuwa zuwa ga Allah kamar ranakun goman farko na watan zulhijja, sai sukace ya manzon Allah hadda yin hijadi domin daukaka addinin Allah sai yace eh hadda yin hijadi ne domin daukaki addinin Allah sai dai ga Mutumin da yafita da ransa da dukiyan sa kuma baidawo da komai ba cikin haka"[83].

Daga cikin muhimmancin kwanaki goman farko na watan zulhijji shine cewa Allah yayi rantsuwa dasu cikin

---

Suratul kadari[80]
Suratul dukkan [81]
Hadis ne Mai raini imamu malik ya ambace shi cikin muwadda [82]
Buhari da abu dawud da ibn majja da tirmizi ne suka rawaito shi [83]

littafin sa mubuwayi: "ina rantsuwa alfijir (1) da kwanaki goma (2) da shafa'i da witiri (3)[84]. Kwanaki goma kamar yadda malamai suka fadi sune na farkon watan zulhijja.

Saboda haka ka dake yakai Xan uwa akan riVatan wannan kwanaki goma na farkon watan zulhijja da ayyukan Qwaraikamar karatun Al-qur'ani da sadaka da safiloli da Azumi, haka kuma ga Mutumin da yakasance cikin haramin maka da madina musamman, da kuma Azumin ranan arfa kamar yadda falalar haka ya gaVata da yanka ranar Salla dukka wannan suna cikin sunnar manzon Allah s.a.w.

**3) lokuta na karban addu'a:**

**a)** addu'a a tsakiyan dare yana cikin lokutan amsar addu'a masamman lokacin da Mutum yake Sallar tahajjud da ganawa da ubangijin sa, an karvo daga Ajbair Xan Abdullahi Allah ya kara masu yarda yace: naji manzon Allah s.a.w yana cewa: " lallai acikin dare akwai wani lokaci wanda Mutum musulmi bazzai dace ba yana roqon Allah wani alheri acikin sa na abubuwan dauniya Xana lahira face ambashi kuma haka cikin kowani dare ne"[85]. cikin wani Hadisn kuma manzon Allah s.a.w yace: " ubangijin Maxaukaki yana sauko a kullum cikin ko wani dare zuwa saman Duniya a a daren karshe yana cewa wanene zai roke ni na amsa mashi wanenen zai roke ni na bashi wanene zai nemi gafarata na gafarta masa"[86].

Ka dage damtse ya kai Xan uwa kuma ka zama cikin mutane na Qwarai kuma ka amsa kiran Mai rahama.

**b) addu'a a tsakanin kiran Salla da ikama:**

---

Suratul fajri [84]
Muslim da tirmizi da abu dawud ne suka rawaito shi[85]
Muslim da tirmizi ne suka rawaito shi [86]

wannan yana cikin lokutan da ake amsar addu'a, an karvo Hadis daga Anas Xan Malik Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: " ba'a dawo da addu'ar da akayita tsakanin kiran Salla da ikama, saboda haka kuyi addu'a", abu dawud ne ya rawaito shi, tirmizi kuma ya kara da cewa " sai sukace to Mai zamuce ya manzon Allah sai yace ku roki Allah lafiya Duniya da lahira"[87].

**c) wani lokaci a cikin yinin jumma'a:**

daga cikin abubuwan da jumma'a ta kebanta dashi akan sauran ranakun akwai wani lokaci a cikin sa da ake amsa addu'a, an karvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda cewa manzon Allah s.a.w ya ambaci ranar jumma'a sai yace: " a cikinta akwai wani lokaci wanda bawa musulmi bazai dace ba dashi yana Salla, ya tambayi Allah wani abu face Allah ya bashi sai ya nuna ya hannun sa yana takaita lokacin"[88]. Malamai sunyi sabani akan lokacin wasu sukace lokacin da aka gama khuduba zuwa a gaba Salla, wasu kuma sukace lokacin karshe ne na ranar jumma'a bayan Sallar la'asar kuma wannan maganar itace tafi rinjaya saboda faxin manzon Allah s.a.w: " ku nemi lokacin da ake fata na ranara jumma'a bayan Sallar la'asar zuwa faduwar rana"[89].

**d) yayin da Mai Azumi yake bude baki:**

an karvo Hadis daga Abdullahi Xan Amru Xan Aas Allah ya kara masu yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: " lallai Mai Azumi yana da wata a yayi bude bakin sa wacce ba'a mayar da ita"[90]. Saboda haka ne ana son Mai Azumi ya

---

Tirmizi ne ya rawaito shi [87]
Buhari da muslim ne suka rawaito shi[88]
Tirmizi da dabarani ne suka rawaito shi [89]
Ibn majjah ne ya rawaito shi (1753), Hadis ne Mai rauni [90]

yawaita addu'a a lokacin bude bakin sa da kuma roqon Allah daga falalar sa, kuma wannan yana daga cikin falalar masu Azumiwanda Allah ya kebance su dashi.

**e) addu'a ranar arfa:**

manzon Allah s.a.w yace: " mafi alherin addu'a ita ta ranan arfa kuma mafi alherin Abunda nake fadi da annabawan da suka gabaceni cikin wannan rana shine la'ilaha illahu wahdahu la sharikalahu lahul mulku wa lahul hamdu wahuwa ala kulli shai'in kadir"[91].

**f) addu'a a lokacin sauke karatun Al-qur'ani:**

an rawaito daga Anas cewa ya kasance idan yayi saukan karatun Al-qur'ani yana tara yaran sa da matan sa sai ya masu addu'a[92].

**g) addu'a a lokacin shan ruwan zamzam:**

an karvo Hadis daga JAbur Xan Abdullahi Allah ya kara masu yarda cewa manzon Allah s.a.w yace: " ruwan zamzam yana maganin Abunda akasha domin sa"[93].

## b) wuraren da ake ruvanya Ladan aiki acikin su kuma ake amsar addu'a:

**1) Masallacin ka'aba:**

An karvo Hadis daga JAbur Xan Abdullahi Allah ya kara masu yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: "Salla acikin wannan Masallacin nawa yafi falala sau dubu akan Salla a wani Masallaci cikin maSallatai sai dai Masallacin

---

Tirmizi ne ya rawaito shi (3585)[91]
Darimi ne ya rawaito shi da baihaki[92]
Ibn majjah ne ya rawaito shi (3062) [93]

ka'aba, sannan Salla a Masallacin ka'aba kuma mafi falala sau dubu dari falala akan Salla acikin wannan Masallaci nawa"[94]. Kuma shine farkon Masallacin da aka shar'anta balaguro zuwa gare shi, kuma shine dakin Allah a doron kasa wanda ya sanya wa mutane domin samun lada da kuma aminci zukatan muminai yana shauki zuwa gareshi sannan kuma zukatan masu biyayya ya alakantu dashi, kuma shine alkiblar musulmai na biyu kuma shine farkon harami guda biyu madaukaka.

**2) Masallacin manzon Allah s.a.w:**

Shine Masallacin harami na biyu wanda manzon Allah s.a.w ya gina lokacin dazo garin madina domin ya kasance wurin taruwan musulmai da yin ibadun su kuma ya zama cibiyar karatu da karantarwa, daga cikin sa ne sahabbai suke fita domin yada musulunci a faxin Duniya.

Daga cikin falalar Masallacin Abunda aka rawaito daga Abu Huraira daga manzon Allah s.a.w yace: " tsakanin gidana da minbari na dausayi ne cikin dausayin aljanna, kuma minbari na yana cikin tafki na"[95].

An kuma karvo Hadis daga Abu Huraira cewa manzon Allah s.a.w yace: " Salla a cikin wannan Masallaci nawa yafi falala sau dubu akan yin Salla a cikin wani Masallacin da bashi ba sai Masallacin ka'aba kawai"[96].

**3) Masallacin kudus:**

Allah Maxaukaki yace: " tsarki ya tabVata ga Allah wanda yayi balaguro dashi cikin dare daga Masallacin ka'aba zuwa Masallacin kudus wanda muka sanya albarka a

---

Ahmad ne ya rawaito shi (14750) da ibn majjah (1406) [94]
Buhari da muslim da nasa'I ne suka rawaito shi[95]
Buhari da muslim da nasa'I ne suka rawaito shi[96]

cikinsa"[97]. Shine kuma farkon alkibla da kuma wurin malaguron manzon Allah, kuma a cikin sa ne aka tafi dashi sama.

Kuma yana daga daga cikin maSallatai wanda ake balaguro zuwa garesu, an karvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara mashi yarda daga manzon Allah s.a.w yace: " ba'a kulle jaka da niyyar balaguro sai zuwa maSallatai guda uku, Masallacin ka'aba da Masallacin manzon Allah s.a.w da Masallacin kudus"[98]. Daga cikin falalar sa shine Hadisn da Abdullahi Xan Amru Xan Aas ya rawaito mana daga manzon Allah s.a.w cewa: " lokacin da sulaiman Xan dawud y agama gina Masallacin kudus ya roki abubuwa guda uku, hukunci wanda zai rika dacewa da hukuncin sa, da mulki wanda baza'a kara ba wani ba irinsa a bayan sa, da kuma cewa kada wani Mutum da zaizo wannan Masallaci da niyyar yin Salla face ya fita a cikin sa an gafarta masa zunuban sa baki daya ya koma kamar ranar da mahaifiyar sa ta haife shi, sai aka bashi abubuwa biyun farkon daya tambaya kuma ina fatan cewa an bashi na ukun ma"[99].

## 4) Masallacin kuba:

An karvo Hadis daga Asid Xan Hadir Allah ya kara masa yarda daga manzon Allah s.aw. yace: " Salla a Masallacin kuba dai dai yake dayin umra"[100], Sahal Xan Hanif Allah ya kara masa yarda ya kara cewa: manzon Allah s.a.w yace: " Duk wanda yayi Alwala a gidan sa sa'annan ya fita zuwa Masallacin kubuyayi Salla a cikinta to yanada Ladan umra"[101].

---

Suratul isra'I ayata 1 [97]
Buhari da muslim da ibn majjah da nasa'I ne suka rawaito shi[98]
Ibn majjah ne ya rawaito shi (1408) [99]
Tirmizi ne ya rawaito shi (324) da ibn majjah (1411) [100]
Ibn majjah ne ya rawaito shi (1421), da nisa'I (699) [101]

**5) addu'a a wurin multazim (Xan tsakanin hahrul aswad da zuwa kofar ka'aba):**

Ya tabVata cewa fuskantar multazim da addu'a a wurin sa mustahabbi ne[102] saboda Abunda Abdurrahman Xan Safwan Allah ya kara masa yarda ya fadicewa: " naga manzon Allah s.a.w ya lazimci tsakanin kofar ka'aba da hajrul aswad kuma naga mutane suma sun lazimci wurin tare da manzon Allah s.a.w"[103]. kuma an rawaito daga Abdullahi Xan Abbas Allah ya kara masu yarda ya lazimci tsakanin kofar ka'aba da hajrul aswad, ya kuma kasance yana ewa: (tsakanin kofar ka'aba da hajrul aswad ake kira da suna multazim kuma wani Mutum bazai lazimci wurin ba yana Mai roqon Allah wani abu gface Allah ya bashi wannan addu'a tashi)[104].

## c) mutanen da ake amsar addu'ar su:

an karvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda hyace: manzon Allah s.a.w yace: " Mutum uku addu'ar su karbabbiya ce babu shakka a cikin su, addu'ar wanda aka zalumta da addu'ar matafiyi da addu'ar mahaifa akan yaron su"[105].

Acikin wani Hadis kuma da daban daga Abu Huraira Allah yakara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: " Mutum uku ba'a dawo masu da addu'ar su, Mai Azumi a lokacin da yake bude baki, da shugaba adili, da wanda aka zalumta idan ya daga hannunsazuwa sama za'a bude masa

[102] Akwai sabani a wurin malamai akan matsalar

[103] Ahmad ne ya rawaito shi (1898)

[104] Hadis ne maukufun akan ibn abbas isnadin shi Mai rauni ne, littafin almajmu'u sharhin muhazzab na nawawi mujalladi na 8, shafi na 260

[105] Tirmizi ne ya rawaito shi (3448)

kofofin sama sannan ubangiji zai ce: ina rantsuwa da buwaya na sai na taimake ka koda kuwa bayan lokaci ne Mai tsayi"[106].

## 4) wuraren zakiri:

An karvo Hadis daga Abu Huraira Allah yakara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: " mutane basu haduwa cikin daya daga cikin dakin Allah suna karanta littafin sa ko nazari akansa a tsakanin sub a face natsuwa ta sauka a kansu kuma za'a rufe su da rahama kuma mala'iku zasu kewaye su sannan kuma Allah zai ambace su cikin mutanen da suke wurin sa"[107]. Wannan falalolin masu girma da kyauta Mai tarin yawa Allah ya kebe su ne ga wuraren zikiri.

An kuma kara karvo wa daga gareshi Allah yakara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: " lallai mala'iku suna kewaye hanyoyi suna neman mutane masu zikiri idan suka sami wasu mutane suna ambaton Allah sai suyi kira suce kuzo zuwa ga bukatun ku sai suce: sai su shinfida masu fuka fukan su zuwa ga saman Duniya sai yace: sai ubangijin su ya tabbayesu kuma yafi su sanin Abunda bayin sa suke cewa sai suce: suna maka tasbihi ne ka Karvarbori da kuma gode maka da kirari a gareka, sai yace: sun sun ganni ne, sai yace: sai suce basu ganka ba, sai yace : to da ace sun ganni daya zai kasance kenan, sai yace: sai suce da sun ganka da Abunda zasuyi maka yafi haka, sai yace: to Mai suke roko nane akai sai sauce suna roqonka aljanna ne, sai yace sun taba ganin ta ne? sai suce a'a basu taba ganin ta ba, sai yace to ya kuke gani da sun taba ganinta? Sai suce da sun taba ganinta da sunfi dagewa akan roqonta, sai yace to Mai suke

Tirmizi ne ya rawaito shi (3598)[106]

Muslim da abi dawud da ibn majjah da tirmizi ne suka rawaito shi[107]

neman tsari daga dagre shi? Sai suce suna neman tsari ne daga wuta, sai yace sun taba ganinta ne? sai suce a'a basu taba ganinta ba, sai yace to yaya kuke gani da sun taba ganinta? Sai suce da sunfi dagewa wurin neman tsari daga gareta, sai yace to ku shaida na gafarta masu, sai yace: shugaban mala'iku sai yace a cikin su fa akwai wane da wane ba tare yake da sub a kawai yazo ne domin bukatar sa, sai yace su mutane ne wanda Mai sabon cikin su bazai tabe ba saboda zaman da yayi tare dasu"[108].

## 5) zikirin Allah Maxaukaki:

Allah Maxaukaki yace: " da maza masu ambaton Allah da yawa da mata masu ambaton Allah, Allah ya tanadar masu da wata irin gafara da lada Mai girma (35)[109].

Wannan itace ladar su kuma da cikin fa'idar yin zikirifaxin Allah Maxaukaki: " wanda sukayi imani kuma zukatansu take natsuwa da ambaton Allah, ku saurara kuji da ambaton Allah ne zukata suke samun natsuwa"[110].ya kuma kara fadi cewa: " ku ambace ni zan ambace ku"[111].

Daga cikin Ladan zikiri kuma har wayau faxin manzon Allah s.a.w cewa: " mufridun sun tsere, sai aka ce masu su waye mufriduna sai yace: sune wanda suke yawan zikirin Allah maza da mata"[112]. Allah Maxaukaki ya kara fadi cikin Hadisl kudusi cewa: " ni ina wurin da bawana yayi zato na kuma ina tare dashi idan ya ambace ni idan kuma ya ambace ni cikin zuciyar sa zan ambace shi cikin zuciya ta

Buhari da muslim ne suka rawaito shi[108]
Suratul ahazab [109]
Suratul ra'ad[110]
Suratul bakara ataya 152[111]
Muslim ne ya rawaito shi (2676), da kuma tirmizi (3596)[112]

idan kuma ya ambace ni cikin taron Jama'a zan ambace shi cikin taro wanda sukafi su alheri"[113]. Da sauran ayoyi da hadisai wanda suke nuni akan falalar zikirin Allah da masu zikiri, ga wasu daga cikin zikirori nan tafe agare ka tare da anbata n falalar ko wanne daga cikin su da Ladan daya kebanta dashi:

## a) Tasbihi da tahmidi da tahlili:

An karvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda daga manzon Allah s.a.w yace:" Duk wanda yayi tasbihi ga Allah sau talatin da uku bayan ko wani Salla ya kuma godema Allah (alhamdulilla) sau talatin da uku da kuma kabbara sau talatin da sannan ya cika na daren da cewa la'ilaha illah wahdahu la sharikalahu lahul mulku wa lahul hamdu wa huwa ala kulli shai'in kadir za'a gafarta masa zunuban sa ko da sun kai yawan kunfan teku"[114].

Hadis yazo daga Aliyu Allah ya kara masa yarda cewa:fadima tana kukan cewon da ya saMaita ahannunta sai taje gun manzon Allah s.a.w takaimai kokunta bayan an kawo masa fursunonin yake, da taje gidan sai Vata saMaishi ba ya fita sai tabarma Aisha Sallahu, da manzon Allah s.a.w ya dawo sai Aisha ta fAdamasa cewa Fadima tazo da bukatar kaza da kaza Vata saMaika ba tabarmun sako, sai manzon Allah s.a.w ya fita ya tafi gidan su fadima koda ya iso sai ya saMaisu sun kwanta suna kokarin tashi da sukaji shigowar sa sai yace masu a'a kuyi kwanciyar ku ya zauna a tsakanin su yace masu: " bazan sanar daku ba Abunda yafi alheri kan Abunda kuke tambay, idan kunzo Bacci kuyi kabbara sau talatin da uku da tasbihi sau talatin da uku da

Buhari da muslim ne suka rawaito shi[113]
Muslim ne ya rawaito shi (597)[114]

tahmidi sau talatin da uku wannan yafi maku alheri akan wanda zai rika maku hidima".[115]

Acikin falalar tasbihi kuma shi kaxai manzon Allah s.a.w yace: " shin dayan ku zai kasa samun lada dubu cikin ko wani rana! Sai wani ya tambaye shi cikin wanda suke zaune a gefensa: ya zamu samu lada dubu? Sai yace: yayi tasbihi dari za'a rubuta masa lada dubu ko kuma a kankare masa zunuban sa dubu da shi"[116].

## b) Faxin la'ilaha illa Allah:

Manzon Allah s.a.w yace: " ku yawaita faxin la'ilaha illah gabanin mutuwa ta hanaku, sai manzon Allah s.a.w: yace annAbu nuhu yace Xansa a lokacin mutuwar sa ina maka umurni da faxin la'ilaha illah, lallai da za'a sanya sammai bakwai da kassai bakwai akan ma'auni a kuma saka la'ilaha illah a dayan Vangaren sai ta rinjaye shi"[117]. A cikin wani Hadis kuma na daban AnnAbu Musa yace: " ya ubangiji n aka sanar Xani wani wand azan rika kiran ka dashi sai yace: ya Musa kace la'ilaha illah, sai Musa yace: ya ubangiji dukkanin bayin ka suna faxin wannan, sai Allah yace: ya Musa da'ace sammai bakwai da Abunda ke cikin su banXani da kassai bakwai za'a sanya su a ma'auni sai a sanya la'ilaha illah a dayan Vangaren sai ta rinjayesu"[118]. An karvo daga Abu zarri Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: " babu wani Mutum da zaice la'ilaha illah sa'annan ya mutu akan haka face ya shiga aljann"[119].

---

Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn [115]
Muslim ne ya rawaito Hadisn (2698) [116]
Ahmad ne ya rawaito shi kuma albani ya inganta shi [117]
Ibn hibban ne ya rawaito shi hakim kuma ya inganta shi [118]
Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn [119]

La'ilaha illah kore allantan wanin Allah ce da kuma tabVatar da ita ga Allah shi kaxai da kuma kaxai tashi da bauta.

## c) Faxin subhana Allah wAbu hamdihi subhana Allahi El-'Adhîm:

An karvo Hadis daga JAbur Allah ya kara masa yarda yace: maznon Allah s.a.w yace: " Duk wanda yace subhanallahil azim wAbuhamdihi za'a shuka masa bishiyar dAbuno a aljanna"[120]. Kuma manzon Allah s.a.w yace: " kalmomi guda biyu masu sauki a larshe amma suna da nauyi a ma'auni kuma Allah Mai rahama yana son so, sune subhanallahi wAbu hamdihi subhanallahil azim"[121].

## d) Faxin subhana Allahi wAbu hamdihi (tsarki ya tabVata ga Allah da kuma godiya a gareshi):

An karvo Hadis daga Abu zarri Allah yakara masa yarda manzon Allah s.a.w yace: " shin bazan baka labara ba da Abunda Allah yafi so na Magana shine subhanallahi wAbu hamdihi"[122]. A cikin wata ruwaya kuma an tambayi manzon Allah cewa wani Magana ne yafi falala sai yace: " Abunda Allah ya zaban ma bayin sa da mala'ikun sa faxin subhanallahi wAbu hamdihi"[123]. Kuma an karvo daga Abdullahi Xan KAbub Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: " wanda ya tsuke hannu wurin ciyar wa kuma yake son da daddare ya amso shi to sai ya

---

Tirmizi da nasa'I ne suka rawaito shi [120]
Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn [121121]
Muslim ne ya rawaito shi (2731) [122]
Muslim ne ya rawaito shi (2731) [123]

rike faxin subhanallahi wAbu hamdihi"[124]. An karvo kuma daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: " Duk wanda yace subhanallahi wAbu hamdihi sau dari a rana za'a shafe masa zunuban sa koda sun kai yawan kunfan teku"[125].

## e) Faxin subhana Allah wa Al-Hamdu Lillah wala ilaha illa Allahu wa Allahu Akbar (tsarki ya tabVata ga Allah da godiya a gareshi kuma babu abun bautawa da gaskiya sais hi kuma Allah Mai girma):

Manzon Allah s.a.w yace: " na hadu da Ibrahim a daren da akayi tafiya Xani zuwa sama sai yacemun ya Muhammad ka isarmun da Sallamata zuwa ga al'ummar ka kuma ka basu labari cewa lallai aljanna Mai dadi ce da kuma ruwa Mai XanXano kuma dasonta shine subhanalla walhamdulillah wala ilaha illahu wallahu akbar"[126]. Manzon Allah s.a.w yakara fadi cewa: " faxin subhanallah wal hamdulilla wala ilaha illahu wallahu akbar yafi soyuwa a gareni cikin yini baki daya"[127].

## f) Faxin subhana Allahi wAbu <u>h</u>amdihi ‘adada khalkihi warida Nafsihi wa zinata ‘arshihiwa midada Kalimâtih (tsarki ya tabVata ga Allah da godiya a gseshi adadin halittun sa da yardar ransa da nauyin al'arshin sa):

---

Albani ne ya fitar dashi cikin sahihul jami'u (6377) [124]
Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn [125]
Tirmizi ne ya rawaito shi (3462) [126]
Muslim ne ya rawaito shi (2695)[127]

An karvo Hadis daga juwairiyya uwar muminai Allah ya kara mata yarda cewa:

manzon Allah s.a.w ya fita ya barta a zaune tana kirikiri bayan Sallar asuba har ya dawo ya tarar da ita a zaune bayan hantsi sai yace mata har yanzu kina zaune kina Abunda natafi nabarki kinayi tace masa eh sai yace mata: " Haqiqa na fadi wasu kalmomi guda hudu bayan ki sau uku wanda da za'a auna su da Abunda kika fadi tun dazu baki daya da sunyi daidai dasu, cewa: (tsarki ya tabVata ga Allah da godiya a gseshi adadin halittun sa da yardar ransa da nauyin al'arshin sa ", a cikin wani ruwayan kuma (tsarki ya tabVata ga Allah adadin halittun sa tsarki ya tabVata ga Allah yardar ransa tsarki ya tabVata ga Allah daidai nauyin al'arshin sa tsarki ya tabVata ga Allah yawan kalmomin sa).[128]

## g) Faxin la 'ilaha illa Allah Wahdahu la sharika Lahu, Lahu al-mulku wa Lahu al-hamdu wa Huwa ‘ala kulli shai'in Kadîr (babu abun bautawa da gaskiya sai Allah shikaxai yake bashi da abokin tarayya shike da godiya da mulki kuma shine Mai ikon akai komai:

Manzon Allah s.a.w yace:

" Duk wanda yace bayan ya tashi da safe la'ilaha illallahu wahadahu la sharikalahu wahul mulku walahul hamdu wa huwa ala kulli shai'in kadir, kamar yay anta bawa ne cikin yaran Isma'il, kuma za'a shafe masa zunuban sa goma kuma adaga darajar sa so goma kuma zai kasance cikin kariya daga Shaidan har sai ya yammaci, idan kuma ya fadi hakan

Muslim ne ya rawaito shi (2726)[128]

da yamma shima haka zai kasance har sai ya wayi gari"[129]. An karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda manzon Allah s.a.w yace: " Duk wanda yace la'ilaha illah wahadahu la sharikalah lahul mulku walahul hamdu wa huwa ala kulli shai'in kadir sau dari a rana zata kazam maii kmaar yay anta bayi goma kuma a rubuta masa lada dari kuma a kankare masa zunuban sa dari kuma zai kasance cikin kariya daga Shaidan har sai ya yammaci gari kuma babu wanda zaizo da aiki wanda yafi nashi falala sai Mutumin daya fadi hakan adadin dayafi nashi"[130].

### h) Faxin lahaula wala kuwwata illa Billah:

An karvo daga Abu Musa al ash'ari Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: " yakai Abdullahi Xan kais, bazan nuna maka arziki ba cikin arzikin aljanna? Sai nace eh ka nunamun ya manzon Allah. Sai yace: " la haula wala kuwwata illa billah"[131].

## 6) Kaffaratul majlisi (kaffaran wurin zama):

An karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

"مَنْ جَلَسَ مَجْلِسًا كَثُرَ فِيهِ لَغَطُهُ، فَقَالَ قَبْلَ أَنْ يَقُومَ: سُبْحَانَكَ رَبَّنَا وَبِحَمْدِكَ، لا إِلَهَ إِلا أَنْتَ أَسْتَغْفِرُكَ وَأَتُوبُ إِلَيْكَ، كَانَ كَفَّارَةٌ لَمَّا كَانَ فِي ذَلِكَ الْمَجْلِسِ".

[129] Ibn majjah ne ya rawaito shi (3867)
[130] Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn
[131] Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn

" Duk wanda ya zauna a wani majalisi wanda ya ambaci sabo dayawa sai yace kafin ya tashi daga wannan majalisin " subhanakalla humma wAbuhamdika ashhadu alla ilaha illa anta astagfiruka wa'a tubu ilaik", zai gafarta masa zunuban sa dayayi a wannan majalisin"[132].

## 7) Jin tsoron Allah:

Allah Maxaukaki yace:

﴿ وَلِمَنْ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِۦ جَنَّتَانِ ۝٤٦ ﴾

Ma’ana: " Duk wanda yaji tsoron ubangijin sa yana da aljanna guda biyu (46)" [133].

Ya kuma kara fadi cewa:

﴿ وَأَمَّا مَنْ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِۦ وَنَهَى ٱلنَّفْسَ عَنِ ٱلْهَوَىٰ ۝٤٠ فَإِنَّ ٱلْجَنَّةَ هِىَ ٱلْمَأْوَىٰ ۝٤١ ﴾

Ma’ana: "amma waxan da sukaji tsoron ubangijin su suka hana ransu Abunda take bukata (40) to lallai aljanna itace makoma a garesu (41)"[134].

Ya kuma kara fadi har wayau:

﴿ إِنَّ ٱلْمُتَّقِينَ فِى جَنَّٰتٍ وَعُيُونٍ ۝٤٥ ﴾

Ma’ana: " lallai masu jin tsoron Allah suna cikin aljanna da korami (45)[135].

---

Nasa'I da tirmizi ne suka rawaito shi[132]
Suratul rahman [133]
Suratun nazi'at [134]

Tsoron Allah ita take zaburar da bawa ya aikata Abunda Allah ya umurce shi kuma ya nisanci Abunda ya haramta, Allah Maxaukaki yace:

Ma’ana: " kodai wanda ke wayan bauta cikin dare yana sujjada da tsayuwa yana Mai tsoron lahiran sa kumakwadayin samun rahamar ubangijin sa"[136].

Da kuma faxin sa Maxaukaki:

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ هُم مِّنۡ خَشۡيَةِ رَبِّهِم مُّشۡفِقُونَ ٥٧ وَٱلَّذِينَ هُم بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمۡ يُؤۡمِنُونَ ٥٨ وَٱلَّذِينَ
هُم بِرَبِّهِمۡ لَا يُشۡرِكُونَ ٥٩ وَٱلَّذِينَ يُؤۡتُونَ مَآ ءَاتَواْ وَّقُلُوبُهُمۡ وَجِلَةٌ أَنَّهُمۡ إِلَىٰ رَبِّهِمۡ رَٰجِعُونَ
٦٠ أُوْلَٰٓئِكَ يُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡخَيۡرَٰتِ وَهُمۡ لَهَا سَٰبِقُونَ ٦١﴾

Ma’ana: " lallai wanda suke tsoron ubangijin su dukda aikin su ya alheri da suke aikatawa (57) wanda kuma suke imani da ayoyin ubangijin su (58) wanda kuma basa hada ubangijin su dawani cikin bauta (59) wanda suke bayar da Abunda aka basu zuciyar su yana cike da tsoron cewa lallai zasu koma zuwa ga ubangijin su (60) wa'inna sune wanda suke rigegeniya zuwa ga alheri kuma suke isa zuwa gareta (61)"[137].

Malamai sune ma'abota tsoron Allah, sunfi kowa cikin mutane tsoron Allah saboda sunan girman sa da sukayi da ayoyin sa masu girma da kuma tsananin azabar sag a wanda suka saba masa, Allah Maxaukaki yace:

﴿إِنَّمَا يَخۡشَى ٱللَّهَ مِنۡ عِبَادِهِ ٱلۡعُلَمَٰٓؤُاْۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ غَفُورٌ ٢٨﴾

---

Suratul hijri [135]
Suratul zumar [136]
Suratul muminun [137]

Ma’ana: " lallai wanda sukafi jin tsoron Allah cikin bayin sa sune malamai"[138].

An karvo Hadiss daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda cikin mutane bakwan da Allah zai sanya su cikin inuwar ranar da babu wata inuwa sai inuwar sa daga cikin su akwai

وَرَجُلٌ دَعَتْهُ امْرَأَةٌ ذَاتُ مَنْصِبٍ وَجَمَالٍ إِلَى نَفْسِهَا ، فَقَالَ : إِنِّي أَخَافُ ٱللَّهَ

Ma’ana: "Mutumin da wata mace Mai daraja da matsayi da kyau ta nemi yayi fasikanci da ita sai yace mata a'a ina tsoron Allah na"[139].

a cikin wani Hadis kuma na daban daga Xan Abbas Allah ya kara masu yarda yace: naji manzon Allah s.a.w yana cewa:

« عَيْنَانِ لاَ تَمَسُّهُمَا النَّارُ عَيْنٌ بَكَتْ مِنْ خَشْيَةِ ٱللَّهَ وَعَيْنٌ بَاتَتْ تَحْرُسُ فِي سَبِيلِ ٱللَّهَ »

Ma’ana: " idanu guda biyu wuta baya taba su, duk idon da ta tuna Allah sai tayi kuka da kuma idan da ta kwana tana gani domin daukaka Kalmar Allah"[140]

## 8) hakurin mutuwar yaro:

### a) gidan godiya:

---

[138] Suratu fadir

[139] Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn

[140] Tirmizi ne ya rawaito shi (1639)

an karvo daga Abu musa al ash'ari Allah ya kara masa yarda cewa manzon Allah s.a.w yac:

إِذَا مَاتَ وَلَدُ الْعَبْدِ قَالَ ٱللَّهَ لِمَلائِكَتِهِ : قَبَضْتُمْ وَلَدَ عَبْدِي ؟ قَالُوا : نَعَمْ ، قَالَ : قَبَضْتُمْ ثَمَرَةَ فُؤَادِهِ ؟ قَالُوا : نَعَمْ ، قَالَ : فَمَا قَالَ ؟ قَالُوا : اسْتَرْجَعَ وَحَمِدَكَ ، قَالَ : ابْنُوا لَهُ بَيْتًا فِي الْجَنَّةِ وَسَمُّوهُ بَيْتَ الْحَمْدِ

Ma’ana: " idan yaron wani Mutum ya mutu sai Allah yace ma Mala'iku: kun kashe yaron bawane? Sai suce eh, sai yace kun kashe farin cikin zuciyar sa? Sai suce eh, sai yace: to Mai bawana ya fadi? Sai suce ya gode maka ne kuma yace innalillahi wa inna ilaihi raji'un, sai Allah yace: ku ginama wannan bawan nawa gida cikin aljanna kuma ku kira shi da suna gidan godiya"[141].

## b) Rasuwan yaran Mutum biyu ko uku:

an karvo Hadis daga Abu sa'id Allah ya kara masa yarda yace: wata mata tazo wurin manzon Allah s.a.w sai tace masa:

ذَهَبَ الرِّجَالُ بِحَدِيثِكَ ، فَاجْعَلْ لَنَا مِنْ نَفْسِكَ ، يَوْمًا نَأْتِيكَ فِيهِ تُعَلِّمُنَا مِمَّا عَلَّمَكَ ٱللَّهُ . فَقَالَ « اجْتَمِعْنَ فِى يَوْمِ كَذَا وَكَذَا فِى مَكَانِ كَذَا وَكَذَا » . فَاجْتَمَعْنَ فَأَتَاهُنَّ رَسُولُ ٱللَّهِ – صلى ٱللَّهُ عليه وسلم – فَعَلَّمَهُنَّ مِمَّا عَلَّمَهُ ٱللَّهُ ثُمَّ قَالَ « مَا مِنْكُنَّ امْرَأَةٌ تُقَدِّمُ بَيْنَ يَدَيْهَا مِنْ وَلَدِهَا ثَلاَثَةً ، إِلاَّ كَانَ لَهَا

[141] Tirmizi ne ya rawaito shi (1021)

حِجَابًا مِنَ النَّارِ » . فَقَالَتِ امْرَأَةٌ مِنْهُنَّ يَا رَسُولَ ٱللَّهِ اثْنَيْنِ قَالَ فَأَعَادَتْهَا مَرَّتَيْنِ ثُمَّ قَالَ « وَاثْنَيْنِ وَاثْنَيْنِ وَاثْنَيْنِ »

" ya manzon Allah mazaje sun kwace mana kai sune suke jin hadisan ka kasanya mana rana muma wanda zamu rika haduwa dakai kana karantar damu cikin ilimin da Allah ya sanar dakai, sai manzon Allah s.a.w yace masu ku hadu a rana kaza da kaza a wuri kaza sai suka hadu a wannan wuri da rana sai manzon Allah s.a.w yaje ya karantar dasu cikin ilimin da Allah ya sanar dashi sai yace masu: " babu wata daga cikin ku da yaranta uku zasu rigata mutuwa face sun zaman mata kariya daga wuta, sai wata mata tace ya manzon Allah ko kuma guda biyu sai ya maimaita mata sau biyu sa'annan yace ko kuma yara biyu har sau uku"[142]. An kuma karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda cewa manzon Allah s.a.w yace:

« لاَ يَمُوتُ لأَحَدٍ مِنَ الْمُسْلِمِينَ ثَلاَثَةٌ مِنَ الْوَلَدِ فَتَمَسَّهُ النَّارُ إِلاَّ تَحِلَّةَ الْقَسَمِ »

" babu wani Mutum cikin musulmai wanda yaran sa uku zasu mutu wuta ta shafe shi sai dai warware rantsuwa"[143].

## 9) Biyayya ga Aanzon Allah s.a.w:

Manzon Allah s.a.w shine abun koyin mu, manzon Allah s.a.w shin eja gaban mu, cikin masa biyayya ne alheri da nasara yake, kuma a cikin saba masa asara da sharra yake anan Duniya da lahira.

---

[142] Buhari ne ya rawaito shi (6656)

[143] Buhari ne ya rawaito shi, abunda ake nufi kuma da warware rantsuwa shine: ayar da Allah yayi rantsuwa acikinta shine: "babu wanda bazai wuce ba ta saman wuta"

Allah Maxaukaki yace:

﴿لَّقَدْ كَانَ لَكُمْ فِي رَسُولِ ٱللَّهِ أُسْوَةٌ حَسَنَةٌ لِّمَن كَانَ يَرْجُوا۟ ٱللَّهَ وَٱلْيَوْمَ ٱلْءَاخِرَ وَذَكَرَ ٱللَّهَ كَثِيرًا ﴿٢١﴾﴾

Ma’ana: "Haqiqa manzon Allah ya kasance abun koyin ku ga Duk wanda yake fatan rahamar Allah Duniya da lahira kuma ya ambaci Allah dayawa (21)"[144].

Biyayya ga manzon Allah biyayya ce ga Allah, Allah Maxaukaki yace:

﴿مَّن يُطِعِ ٱلرَّسُولَ فَقَدْ أَطَاعَ ٱللَّهَ ۖ وَمَن تَوَلَّىٰ فَمَآ أَرْسَلْنَٰكَ عَلَيْهِمْ حَفِيظًا ﴿٨٠﴾﴾

Ma’ana: " Duk wanda yayi biyayya ga manzon Allah to Haqiqa yayi biyayya ga Allah"[145].

Biyayya ga manzon Allah sabAbu ne na samun daukaka cikin aljanna Allah Maxaukaki yace:

﴿وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ فَأُو۟لَٰٓئِكَ مَعَ ٱلَّذِينَ أَنْعَمَ ٱللَّهُ عَلَيْهِم مِّنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ وَٱلصِّدِّيقِينَ وَٱلشُّهَدَآءِ وَٱلصَّٰلِحِينَ ۚ وَحَسُنَ أُو۟لَٰٓئِكَ رَفِيقًا ﴿٦٩﴾﴾

" Duk wanda yayi ma manzon Allah biyayya to wa'innan suna tare da wanda Allah yayi masu ni'ima cikin annabawa da siddikai da shahidai da salihai, Haqiqa abotakan su ya kyautata (69)"[146].

Kuma biyayyar manzon Allah s.a.w sabAbu ne na samun soyayyar Allah ga bayin sa da kuma kankare masu zunuban su da kura kuran su, Allah Maxaukaki yace:

---

[144] Suratul ahazab
[145] Suratun nisa'I ayata 8
[146] Suratun nisa'I

﴿ قُلۡ إِن كُنتُمۡ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ فَٱتَّبِعُونِي يُحۡبِبۡكُمُ ٱللَّهُ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡ ذُنُوبَكُمۡۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٣١ ﴾

Ma’ana: " kace masu idan kun kasance kuna son Allah to ku so tabbas Allah zai so ku kuma zai gafarta maku zunuban ku Allah ya kasance Mai gafara da rahama (31)"[147].

Kuma Haqiqa an umurce mu dayi masa biyyay da kuma nisantar Abunda ya hana mu cikin dukkanin Abunda yazo dasu na maganganun sa da ayyukansa da Abunda akayi agaban say a tabVatar be hana ba da sunnonin sa saboda faxin Allah Maxaukaki:

﴿ وَمَآ ءَاتَىٰكُمُ ٱلرَّسُولُ فَخُذُوهُ وَمَا نَهَىٰكُمۡ عَنۡهُ فَٱنتَهُواْۚ ٧ ﴾

Ma’ana: " duk Abunda manzon Allah yazo maku dashi to ku amshe shi wanda kuma ya hanaku ku bari"[148].

Taya hakan bazai kasance ba bayan shi rahama ne kuma Mai shiryar wa, yazo ne domin tsarkake Mutum da shiryar dashi zuwa ga gaskiya, Allah Maxaukaki yace:

﴿ لَقَدۡ جَآءَكُمۡ رَسُولٞ مِّنۡ أَنفُسِكُمۡ عَزِيزٌ عَلَيۡهِ مَا عَنِتُّمۡ حَرِيصٌ عَلَيۡكُم بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ رَءُوفٞ رَّحِيمٞ ١٢٨ ﴾

Ma’ana: " Haqiqa manzon yazo maku daga cikin ku yana mutukar daukaka da duk Abunda zai fito da siffar mutanen sa kuma Mai yawan kwadayi ne akan kuma Mai yawan sauki ne da tausayi ga muminai (128)"[149].

Ya kuma kara fadi har wayau cewa:

---

[147] Suratu al'imran
[148] Suratul hashri
[149] Suratul tauba

﴿وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ إِلَّا رَحۡمَةٗ لِّلۡعَٰلَمِينَ ١٠٧﴾

" bamu aikoka ba face ka zama rahama ga mutane baki daya (107)"[150].

Da kuma faxin sa:

﴿وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ إِلَّا مُبَشِّرٗا وَنَذِيرٗا ٥٦﴾

" bamu aikeka ba face ka zama Mai bishara da gargadi (56)"[151].

## 10) salati ga manzon Allah s.a.w:

Allah Maxaukaki yace:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ وَمَلَٰٓئِكَتَهُۥ يُصَلُّونَ عَلَى ٱلنَّبِيِّۚ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ صَلُّواْ عَلَيۡهِ وَسَلِّمُواْ تَسۡلِيمًا ٥٦﴾

" lallai Allah da mala'ikun sa suna salati ga manzon Allah, yaku wanda sukayi imani kuyi salati agareshi da Sallama gareshi Mai tarin yawa (56)"[152].

An karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda manzon Allah s.a.w yace:

« مَنْ صلَّى عليَّ واحِدَة صَلى ٱللَّهُ عليه عَشْرا»

" Duk wanda yayimun salati daya Allah zeyi masa gomada ita"[153].

---

Suratul anbiya'I [150]
Suratul furkan [151]
Suratul ahazab [152]
Muslim da abu dawud da tirmizi da nasa'I ne suka rawaito shi [153]

Ya kuma kara rawaito wa cewa: manzon Allah s.a.w yace:

مَا مِنْ أَحَدٍ يُسَلِّمُ عَلَيَّ إِلاَّ رَدَّ ٱللَّهَ إِلَيَّ رُوحِي حَتَّى أَرُدَّ عَلَيْهِ السَّلاَمَ

" babu wani da zayyimun Sallama face Allah ya dawomun da raina domin na mayar masa da Sallamar sa"[154].

Ya kuma kara rawaito wa cewa: manzon Allah s.a.w yace:

لاَ تَجْعَلُوا قَبْرِي عِيدًا ، وَلاَ بُيُوتَكُمْ قُبُورًا ، وَصَلُّوا عَلَيَّ ، وَسَلِّمُوا فَإِنَّ صَلاتَكُمْ تَبْلُغُنِي.

" kada ku mayar da Karvarina ya koma wurin taro kurika mun salati ne domin salatin ku yana riske ni a duk inda kuke"[155].

An karvo daga Abu dalhata Allah ya kara masa yarda cewa manzon Allah s.a.w yace:

(أتاني جبريل، فقال: يا محمد أما يرضيك أن ربك عز وجل يقول: انه لا يصلي عليك من أمتك أحد صلاة، إلا صليت عليه بها عشراً، ولا يسلم عليك أحد من أمتك تسليمة إلا سلمت عليه عشراً؟ فقلت: بلى أي ربّ)

Ma'ana: " mala'ika Jibrilu yazo mun sai yacemun ya Muhammad shin be ishe ba cewa ubangijin ka mabuwayi yana cewa babu wanda zayyi maka salati cikin al'ummar ka face Allah yayi masa salati goma da ita, kuma babu wanda zayyi maka Sallama cikin su face anyi masa Sallama goma da ita sai manzon Allah yace eh tabbas kuwa ina rantsuwa da ubangiji na ya ishe ni"[156].

A cikin Sallah an shar'anta mana yin salati ga manzon Allah s.a.w: an karvo Hadis daga Abu mas'ud albadari Allah ya kara masa yarda yace: bashar Xan sa'ad yace: ya manzon

---

Abu dawud ne ya rawaito shi (2041) [154]
Abu dawud ne ya rawaito shi (2042) [155]
Nasa'I ne ya rawaito shi (678) [156]

Allah ya zumuyi maka salati? Sia manzon Allah yayi shiru sa'annan yace:

" قولوا أللهم صل على محمد وعلى آل محمد كما صليت على إبراهيم وآل إبراهيم إنك حميد مجيد وبارك على محمد وعلى آل محمد كما باركت على إبراهيم وآل إبراهيم إنك حميد مجيد ".

Ma’ana: " kuce allahumma salli ala Muhammad wa ala ali Muhammad kama Sallaita ala Ibrahim wa ala ali aibrahim, Allahumma barik ala Muhammad wa ala ali Muhammad kama barakta ala Ibrahim wa ala ali Ibrahim innaka hamidun majid"[157].

Allah kai dadin tsira da aminci da albarka da ni'ima akan shugaban mu Muhammad da iyalan sa da sahabban sa bayin Allah masu tsarki da wanda suka bi bayan su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, tsira da aminci cikakke kamulallu.

## 11) wasu daga cikin addu'o'i da falalar dake cikin su:

### a) Addu'ar kwanciya Bacci

An karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

« إذا أوى أحدكم إلى فِراشه فَلْيَنفُض فِرَاشه بِدَاخِلَةِ إِزَارِهِ ، فَإِنه لا يَدْرِي ما خَلفَه عليه ، ثم يقول : باسمك ربي وَضَعْتُ جنبي، وبك أرفعُهُ ، إنْ أَمْسكْتَ نَفْسي فارْحَمْها ، وإنْ أرْسَلتَها فَاحْفَظْها بما تَحفظُ به عبادَك الصالحينَ»

Muslim ne ya rawaito shi (407) [157]

Ma'ana: " idan dayanku ya kafi zuwa ga makwancin sa ya share wurin shinfidan sa da wanXanso domin besan Abunda ke ciki ba, sa'annan yace da sunanka ya Allah na kwnata da jiki na kuma da ikon kazan tashi idan ka amshi raina kamun rahama idan kuma ka dawomun da ita ka kare ni da Abunda kake kare bayinka salihai dashi"[158].

Kuma manzon Allah s.a.w yace ma barra'u Xan azib Allah ya kara masa yarda:

« إذَا أَوَيْتَ إِلَى فِرَاشِكَ طَاهِراً فَقُلِ اللَّهُمَّ أَسْلَمْتُ وَجْهِى إِلَيْكَ وَأَلْجَأْتُ ظَهْرِى إِلَيْكَ وَفَوَّضْتُ أَمْرِى إِلَيْكَ رَغْبَةً وَرَهْبَةً إِلَيْكَ لاَ مَلْجَأَ وَلاَ مَنْجَا مِنْكَ إِلاَّ إِلَيْكَ آمَنْتُ بِكِتَابِكَ الَّذِى أَنْزَلْتَ وَنَبِيِّكَ الَّذِى أَرْسَلْتَ فَإِنْ مُتَّ مِنْ لَيْلَتِكَ مُتَّ عَلَى الْفِطْرَةِ وَإِنْ أَصْبَحْتَ أَصْبَحْتَ وَقَدْ أَصَبْتَ خَيْراً كَثِيراً ».

" idan ka tafi kwanciya kayi Alwala irin Alwalar Salla sa'annan ka kwanta ta Vangaren ka na dama sai kace ya Allah na mika raina zuwa gare ka kuma na mika al'amari na gareka ya shinfida bayana gareka ina Mai tsoro da kwadayin zuwa gareka babu wurin tsira da wurin gudu sai zuwa gare ka nayi imani da littafin ka wanda saukar da kuma annAbun ka wandaka turo idan ka mutu cikin wannan dare ka mutu akan musulunci idan kuma ka wayi gari to ka samu lada"[159].

## b) addu'ar yayi damuwa da biyan bashi:

Hadis yazo daga Aliyu Allah yakara masa yarda yace wani bawa wanda yayi yarje jeniya da ubangidan sa akan zai biyashi wasu kudi ya yantashi yazo wurin yace masa Haqiqa

---

Buhari da muslim ne suka rawaito shi[158]
Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn [159]

nagaza biyan kudin na nayi alkawari ka taimakamun sai yace masa: bazan sanar dakai ba wasu kalmomi wanda manzon Allah s.a.w ya sanar Xani su ba wanda da ace akwai bashi akanka wanda yakai girman dutsen sAbur Allah zai biya maka bashin ka, sai yace kace:

اللَّهُمَّ اكْفِنِى بِحَلاَلِكَ عَنْ حَرَامِكَ وَأَغْنِنِى بِفَضْلِكَ عَمَّنْ سِوَاكَ ».

" ya Allah ka isarmun da halaliyar ka akan cin haramun kuma ka taimakeni da falalar ka akan Duk wanda bakai ba"[160].

An karvo daga Anas Xan malik Allah ya kara masa yarda cewa manzon Allah s.a.wyace:

اللَّهمَّ إِني أعُوذ بك من الهمِّ والحَزَنِ ، والعَجْزِ والكَسَلِ ، والبُخْلِ وضَلَعِ الدَّيْنِ وغَلَبَةِ الرِّجال».

" ya Allah ina neman tsarin ka daga kunci da bakin ciki da kasawa da kasala da rowa da ragwanci tarin bashi da kuma rinjayen makiya"[161]

## 12) karatun Al-qur'ani:

Allah Maxaukaki yace:

﴿ وَإِذَا قُرِئَ ٱلْقُرْءَانُ فَٱسْتَمِعُواْ لَهُۥ وَأَنصِتُواْ لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ ٢٠٤ ﴾

" idan ana karanta Al-qur'ani kuyi shiru ku saurara koda maku rahama (204)"[162].

---

Tirmizi ne ya rawaito shi (3563) [160]
Buhari da tirmizi ne suka rawaito shi[161]
Suratul a'araf [162]

An karvo Hadis daga Xan mas'ud Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

« مَنْ قَرَأَ حَرْفًا مِنْ كِتَابِ ٱللَّهِ فَلَهُ بِهِ حَسَنَةٌ وَالْحَسَنَةُ بِعَشْرِ أَمْثَالِهَا لاَ أَقُولُ الم رْفٌ وَلَكِنْ أَلِفٌ حَرْفٌ وَلاَمٌ حَرْفٌ وَمِيمٌ حَرْفٌ »

" Duk wanda ya karanta harafi daya cikin Al-qur'ani yanada lada goma bawai ina nufin alif-lam-min harafi daya bane a'a alif harafi daya ne sai lamun shima harafi daya sai mimun shima harafi daya"[163].

An karvo daga Abdullahi Xan Amru da Aas Allah ya kara masu yarda yace: manzon Allh s.a.w yace:

« يُقَالُ لصاحبِ القرآنِ : اقرأْ وارْق ورتِّلْ كَمَا كُنت تُرتِّل في دار الدنيا ، فَإِنَّ مَنزِلَكَ عند آخرِ آية تقرأ بها »

" za'ace ma ma'aboci Al-qur'ani ranan Al-qiyama ka karanta kamar yadda kake karantawa a Duniya karshen gida shine ayar da ka karanta karshe"[164].

An ladabtar damu da karanta Al-qur'ani da natsuwa cikin rerawa da nazarin ma'anonin sa masu tunani cikin daukan izinar sa da kuma anfani da hukunce hukuncen sa, Allah Maxaukaki yace:

﴿أَوۡ زِدۡ عَلَيۡهِ وَرَتِّلِ ٱلۡقُرۡءَانَ تَرۡتِيلًا ۝٤﴾

" ku karanta Al-qur'ani a hankali cikin rerawa (4)"[165] .

a nan wurin umurnin da akayi na wajibi ne[166] da kuma masdarin, Abdullahi Xan mas'ud ya kasance yana cewa:

---

[163] Tirmizi ne ya rawaito shi (2914)
[164] Abu dawud da tirmizi ne suka rawaito shi
[165] Suratul muzzammil

(idan kukaji ance yaku wanda sukayi imani to ku bayar da jin ku kodai za'a umurce ku ne da wani abu ko kuma za'a hanaku aikata wani abun ne)[167].

Acikin falalar karanta Al-qur'ani da surar bakara da al'imran akwai Hadisn da aka rawaito daga abu umamata Allah ya kara masa tarda yace: naji manzon Allah s.a.w yace:

« اقْرَءُوا الْقُرْآنَ فَإِنَّهُ يَأْتِى يَوْمَ الْقِيَامَةِ شَفِيعًا لأَصْحَابِهِ اقْرَءُوا الزَّهْرَاوَيْنِ الْبَقَرَةَ وَسُورَةَ آلِ عِمْرَانَ فَإِنَّهُمَا تَأْتِيَانِ يَوْمَ الْقِيَامَةِ كَأَنَّهُمَا غَمَامَتَانِ أَوْ كَأَنَّهُمَا غَيَايَتَانِ أَوْ كَأَنَّهُمَا فِرْقَانِ مِنْ طَيْرٍ صَوَافَّ تُحَاجَّانِ عَنْ أَصْحَابِهِمَا اقْرَءُوا سُورَةَ الْبَقَرَةِ فَإِنَّ أَخْذَهَا بَرَكَةٌ وَتَرْكَهَا حَسْرَةٌ وَلاَ تَسْتَطِيعُهَا الْبَطَلَةُ »

Ma'ana: " ku karanta Al-qur'ani domin zai zo ranar Al-qiyama a matsayin Mai ceto ga mutanen sa, kuma ku karanta zahrawain suratul bakara da al'imrana domin zasu zo ranan Al-qiyama kamar hadari suna inuwa ga mutanen su, ku karanta suratul bakara domin cikin roko da ita akwai albarka kuma barinta asara ne kuma matsafa bazata iya ba"[168].

Daga cikin falalar karanta suratul kahfi ranar jumma'a Hadisn da aka rawaito daga Abu sa'id alkudri Allah ya kara masa yarda cewa manzon Allah s.a.w yace:

مَنْ قَرَأَ سُورَةَ الْكَهْفِ فِي يَوْمِ الْجُمُعَةِ أَضَاءَ لَهُ مِنَ النُّورِ مَا بَيْنَ الْجُمُعَتَيْنِ

---

Wasu daga cikin malamai basa ganin wajabcin tajawidi kamar sheikh bin bazz Allah yayi masa rahama[166]

Littafin umdatul tafsir na Ahmad shakir [167]

Muslim ne ya rawaito shi (804) [168]

Ma’ana: " Duk wanda ya karanta suratul kahafi ranar jumma'a za'a haskaka masa haske cikin ranakun da suke tsakanin wannan jumma'ar guda biyu"[169].

Cikin falalar karanta suratul ikhlas kuma Hadisn da aka rawaito daga Ubayyu Xan ka'ab Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

"مَنْ قَرَأَ: "قُلْ هُوَ ٱللَّهُ أَحَدٌ" فَكَأَنَّمَا قَرَأَ ثُلُثَ الْقُرْآنِ".

Ma’ana: " Duk wanda ya karanta kulhuwallahu to Haqiqa ya karanta sulusin Al-qur’ani"[170].

**Mutane sun kasu gida biyu Xan gane da iya karatun Al-qur’ani:**

Manzon Allah s.a.w yace:

« الَّذِى يَقْرَأُ الْقُرْآنَ وَهُوَ مَاهِرٌ بِهِ مَعَ السَّفَرَةِ الْكِرَامِ الْبَرَرَةِ وَالَّذِى يَقْرَؤُهُ وَهُوَ يَشْتَدُّ عَلَيْهِ فَلَهُ أَجْرَانِ ».

Ma’ana: " wanda yake karanta Al-qur’ani da iyawa yana sahun gama tare bayu masu karamci zababbu wanda kuma yake karanta Al-qur’ani da da kakarewa domin rashin iyawa da wahala yana da lada biyu Ladan karatu da Ladan wahalar sa"[171].

Mutane kuma ta Vangare samun lada da zunuba kan karatun Al-qur’ani sun kasu gida uku[172]:

---

[169] Hakim da baihaki ne suka rawaito shi kuma albani ya inganta shi

[170] Nasa'I ne ya rawaito shi (686)

[171] Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn

[172] Ya dauko ne daga littafin bugyatu ibadurrahman na sheikh Muhammad Xan shahad al gaul amma ya canza wani abu ba asalin nassin bane

1) Wanda ya kwarance wurin karatun Al-qur’ani kuma yana karantashi yadda yadace tare da dabbaka hukunce hukuncen tilawar sa da tajwidi wannan yana samun lada.
2) Wanda kuma yake karanta Al-qur’ani da wahala bayan ya koyi karatun Al-qur’ani amma baya iya karantashi ta daidai saboda harshen sa ko kuma wahalar furta wasu haruffan cikin sa shima yana da lada.
**3)** Wanda kuma yayi girman kai gaMai da koyan karatun Al-qur’ani Mai kyau ya karkata zuwa karanta shi da harshen ajami to wannan yana samun zunubi akan haka.

### a) wajabcin koyon kaatun Al-qur’ani:

dalili akan wajabcin sa a wurin wanda yake ganin haka cikin malamai shine Abdullahi Xan mas'ud ya kasance yana koyar da wani Mutum sai Mutumin ya karanta faxin Allah

﴿ إِنَّمَا ٱلصَّدَقَٰتُ لِلۡفُقَرَآءِ وَٱلۡمَسَٰكِينِ ﴿٦٠﴾ ﴾

Ma’ana: " lallai sadaka ana bayar da ita ne ga fakirai da miskinai"[173].

Ba tare da yaja maddi ba sai Xan mas'ud yace masabah aka muka koyo shi ba daga manzon Allah s.a.w sai Mutumin yace masa yay a karantar daku shi ya babab Abdurrahman: (sai ya karanta mashi ayar tare dajan maddi)[174].

## 13) Haddar Al-qur’ani da falalar wasu surorin:

[173] Suratul taubah ayata 60

[174] Sa'id Xan Mansur ne ya rawaito shi cikin littafin sa kuma albani yace isnadin sa ingantacce ne

Manzon Allah s.a.w yace:

« إِنَّ الَّذِى لَيْسَ فِى جَوْفِهِ شَىْءٌ مِنَ الْقُرْآنِ كَالْبَيْتِ الْخَرِبِ ».

Ma’ana: " lallai wanda babu haddar komai a tare dashi na Al-qur’ani kamar gidane rushashe"[175].

**Cikin fafalar haddar wasu sorori hadisai sun zo kamar haka:**

Cikin falalar haddar ayoyin farkon suratul kahfi manzon Allah s.a.w yace:

مَنْ حَفِظَ عَشْرَ آيَاتٍ مِنْ أَوَّلِ سُورَةِ الْكَهْفِ ، عُصِمَ مِنْ فِتْنَةِ الدَّجَّالِ

Ma’ana: " Duk wanda ya haddace ayoyin goman farkon suratul kahfi Allah zai kare shi daga dujal"[176].

Allah yayi mani tsari daga sharrin sa.

Ya kuma fadi cikin falalar suratul mulku cewa:

« إِنَّ سُورَةً فِى الْقُرْآنِ ثَلاَثُونَ آيَةً شَفَعَتْ لِصَاحِبِهَا حَتَّى غُفِرَ لَهُ ».

Ma’ana: " lallai acikin Al-qur’ani akwai wata sura Mai ayoyi talatin zasu ceci Mai wanda suka haddace ta har a gafarta masa"[177].

Ya kuma faxin cikin falalar karanta ayatul kursiyyu gabanin Bacci abun da abu haraira ya Ambato cikin Hadisi:

---

[175] Tirmizi ne ya rawaiyto shi cikin littafin fada'ilul kur'an (2913)

[176] Muslim da abu dawud da tirmizi da nasa'I ne suka rawaito shi

[177] Abu dawud da tirmizi da ibn majjah da nasa'I ne suka rawaito shi

إِذا أويتَ إِلى فراشك فَاقْرَأْ آية الكرسي : ٱللَّهُ لا إِلهَ إِلا هو الحيُّ القيوم ، حتى تختم الآية ، فإنه لن يزال عَلَيْكَ مِنَ ٱللَّهِ حافظ، وَلا يَقْرَبُكَ شيطان حتى تُصْبِحَ

" idan kaje Bacci ka karanta ayatul kursiyyu (Allahu la 'ilaha illa Huwa Al-Hayyu Al-Kayyûm) har zuwa karshenta to bazaka gushe ba kana cikin kariyar Allah kuma Shaidan bazai kusance ka ba har sai ka wayi gari"[178].

An karvo kuma daga Xan mas'ud Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

من قرأ آيتين من سورة البقرة في ليلة كفتاه ( آمن الرسول بما أنزل إليه من ربه والمؤمنون......)

" Duk wanda ya karanta ayoyi biyun karshe na suratul bakara cikin dare sun wadatar" (amanarrasulu bima unzila ilaihi min rabbihi wal mu'uminun...)[179].

---

[178] Buhari ne ya rawaito shi (5010)

[179] Malaman Hadis su shida duk sun rawaito shi

# Na biyu: Ayyukan da anfanin su yake komawa akan wanda ya aikata da wanin sa Duniya da lahira.

## 1. Sadaka:

Allah Maxaukaki yace:

﴿ إِنَّ ٱلْمُصَّدِّقِينَ وَٱلْمُصَّدِّقَٰتِ وَأَقْرَضُواْ ٱللَّهَ قَرْضًا حَسَنًا يُضَٰعَفُ لَهُمْ وَلَهُمْ أَجْرٌ كَرِيمٌ ١٨ ﴾

Ma’ana: " lallai masu bada sadaka maza da mata kuma suka bawa Allah bashi Mai kyau za'a nunnun ka masu kuma suna da lada na karamci"[180].

Yazo kuma cikin Hadis cewa:

"الصدقة حجة"

" sadaka Hujja ce"[181],

ita Hujja ce akan dattin bawa daga rowa da mako, kuma Hujja ce akan yardar sa da ubangijin sa na alkawarin da yayi ya sakawa masu ciyar wa da kuma samun sakamako ranan Al-qiyama, kuma tana tsare Mutum daga wuta ranar Al-qiyama, manzon Allah s.a.w yace:

اتقو ا النار ولو بشق تمرة

Ma’ana: " ku kare kanku daga wuta koda da rabin Dabino ne"[182],

---

[180] Suratul hadid

[181] Muslim ne ya rawaito shi (223) da tirmizi (3517)

an kuma karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

" مَنْ تَصَدَّقَ بِعَدْلِ تَمْرَةٍ مِنْ كَسْبٍ طَيِّبٍ , وَلَا يَصْعَدُ إِلَى ٱللَّهِ إِلَّا الطَّيِّبُ , فَإِنَّ ٱللَّهَ يَتَقَبَّلُهَا بِيَمِينِهِ , ثُمَّ يُرَبِّيهَا لِصَاحِبِهَا كَمَا يُرَبِّي أَحَدُكُمْ فَلُوَّهُ , حَتَّى تَكُونَ مِثْلَ الْجَبَلِ "

Ma’ana: " Duk wanda yayi sadaka da barin Dabino wanda ya samo ta hanyar halal, domin Allah baya amsar dasaka sai wanda aka samo ta hanyar halal, to lallai Allai zai amshe ta da damar sa sa'annan ya reneta ga wanda ya bayar da ita kamar yadda wanin ku yake renon shukar sa har ta zama kamar dutse"[183].

Mutum yana cikin inuwar sadakar sa ranar Al-qiyama har sai an gama yima mutane hukunci, an karvo Hadis daga ukuVata Xan amir Allah ya kara masa yarda yace: naji manzon Allah s.a.w yana cewa:

"كُلُّ امْرِئٍ فِي ظِلِّ صَدَقَتِهِ حَتَّى يُقْضَى بَيْنَ النَّاسِ"

Ma’ana: " ko wani Mutum yana karkashin inuwar sadakar sa har sai an gama hukunci tsakanin mutane"[184],

Mai sadaka kuma domin Allah zai kasance karkashin inuwar al'arshin Mai rahama har wayau tare da mutane bakwan da Allah zai masu inuwa cikin inuwar sa ranan da babu wata inuwa sai inuwar sa cikin faxin manzon Allah s.a.w cewa:

---

Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn [182]
Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn [183]
Ahmad da hakim ne suka rawaito shi [184]

وَرَجُلٌ تَصَدَّقَ بِصَدَقَةٍ أَخْفَاهَا مِنْ شِمَالِهِ

Ma'ana: ".... da Mutumin da yayi Sadaka ya voye ta hatta hagunsa besan Abunda damar sa ya bayar ba..."[185]

Sadaka tana yaye damuwar Mai damuwa kuma tane taimakon mabukaci da sawwake wanda ke cikin kunci da kuma bawa Mai tambaya da makamantan su.

Saboda girman sadaka yasa Mai bayar da ita yana da lada Mai girma a wurin Allah, Allah Maxaukaki yace:

﴿مَّثَلُ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمۡوَٰلَهُمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ كَمَثَلِ حَبَّةٍ أَنۢبَتَتۡ سَبۡعَ سَنَابِلَ فِي كُلِّ سُنۢبُلَةٖ مِّاْئَةُ حَبَّةٖۗ وَٱللَّهُ يُضَٰعِفُ لِمَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ٢٦١﴾

Ma'ana: " misalin wanda suke ciyar da dukiyoyin su ta hanyar Allah kamar kwaya ce da aka shuka sai ta fitar da zangarniya bakwai a kan ko wani zangarniya akwai kwaya gua dari, Allah kuma yana nunkawa ga wanda yaso, Allah ya kasance mayalwaci masani"[186].

Mafi karancin lada shine daga goma zuwa dari bakwai, Allah kuma yana karawa ga wanda yaso nunki yafi haka da karamcin sa da falalar sa.

Mai bada sadaka mala'iku suna masa addu'a, ankarvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

« مَا مِنْ يَوْمٍ يُصْبِحُ الْعِبَادُ فِيهِ إِلاَّ مَلَكَانِ يَنْزِلاَنِ فَيَقُولُ أَحَدُهُمَا : اللَّهُمَّ أَعْطِ مُنْفِقًا خَلَفًا وَيَقُولُ الآخَرُ : اللَّهُمَّ أَعْطِ مُمْسِكًا تَلَفًا »

---

[185] Bayani akan Hadisn ya gaVata a baya

[186] Suratul bakara

Ma’ana: " babu wata rana da ake wayen gari a cikinta face mala'iku guda biyu sun sauko dayan su yana cewa ya Allah ka mayarma wanda yaciyar da kudiyar sa, dayan kuma yana cewa ya Allah ka daidaita dukiyan wanda yaki ciyarwa"[187].

Ya kara fadi kuma har wayau cewa:

Ma’ana: " Bayar da sadaka baya ragema dukiya yawa"[188].

Sadaka bawai kawai sai da kudi bane akeyinta ta kunshi dukkanin komai, an karvo Hadis daga Anas Xan malik Allah ya kara masa yarda yace: manzaon Allah s.a.w yace:

مَا مِنْ مُسْلِمٍ يَغْرِسُ غَرْسًا أَوْ يَزْرَعُ زَرْعًا فَيَأْكُلُ مِنْهُ طَائِرٌ أَوْ سَبُعٌ أَوْ دَابَّةٌ أَوْ إِنْسَانٌ إِلا كَانَتْ لَهُ صَدَقَةٌ.

Ma’ana: " babu wani musulmi da zai shuka wani abu ko kuma ya dasa wani abu sai wani tsuntsu yazo yaci daga gareshi ko kuma dabba face hakan ya zama sadaka a gareshi"[189].

عَنْ أَبِى ذَرٍّ أَنَّ نَاسًا مِنْ أَصْحَابِ النَّبِىِّ –صلى ٱللَّهَ عليه وسلم– قَالُوا لِلنَّبِىِّ –صلى ٱللَّهَ عليه وسلم– يَا رَسُولَ ٱللَّهَ ذَهَبَ أَهْلُ الدُّثُورِ بِالأُجُورِ يُصَلُّونَ كَمَا نُصَلِّى وَيَصُومُونَ كَمَا نَصُومُ وَيَتَصَدَّقُونَ بِفُضُولِ أَمْوَالِهِمْ. قَالَ « أَوَلَيْسَ قَدْ جَعَلَ ٱللَّهَ لَكُمْ مَا تَصَّدَّقُونَ إِنَّ بِكُلِّ تَسْبِيحَةٍ صَدَقَةً وَكُلِّ تَكْبِيرَةٍ صَدَقَةٌ وَكُلِّ تَحْمِيدَةٍ صَدَقَةٌ وَكُلِّ تَهْلِيلَةٍ صَدَقَةٌ وَأَمْرٌ بِالْمَعْرُوفِ صَدَقَةٌ وَنَهْىٌ عَنْ مُنْكَرٍ

---

[187] Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn

[188] Tirmizi ne ya rawaito shi (2325)

[189] Buhari da muslim da tirmizi ne suka rawaito shi

صَدَقَةٌ وَفِى بُضْعِ أَحَدِكُمْ صَدَقَةٌ ». قَالُوا يَا رَسُولَ ٱللَّهِ أَيَأْتِى أَحَدُنَا شَهْوَتَهُ وَيَكُونُ لَهُ فِيهَا أَجْرٌ قَالَ « أَرَأَيْتُمْ لَوْ وَضَعَهَا فِى حَرَامٍ أَكَانَ عَلَيْهِ فِيهَا وِزْرٌ فَكَذَلِكَ إِذَا وَضَعَهَا فِى الْحَلاَلِ كَانَ لَهُ أَجْرٌ ».

An kuma karvo daga Abu zarri Allah ya kara masa yarda cewa wasu mutane cikin sahabban manzo Allah s.a.w sunce ma manzon Allah s.a.w ya manzon Allah s.a.w: masu dukiya sun kwashe lada suna Salla kamar yadda mukeyi kuma suna Azumi kamar yadda mukeyi sannan kuma suyi sadaka da sauran kudin su, sai yace masu: shin Allah be sanya maku abubuwan da zaku rikayin sadaka dasu ba kuma, lallai ko wace tasbihi sadaka ce, kuma dukkanin kabbara dasaka ce, da kuma tahmidi shima sadaka ne, da kuma tahlili shima sadaka ne da kuma umurni da kyakyawan aiki shima sadaka ne da kuma yin hani da mummunan aiki shima sadaka ne, kai acikin saduwar dayan ku da iyalin sa ma shima sadaka ne, sai sukace ya manzon Allah yanzu dayan mu zai biya bukatar sa kuma ya samu lada? Sai yace masu ku bani amsa idan yaje ya biya bukatar sa ta hanyar haramun shin za'a bashi zunubi? To Kaman haka ne idan ya biya bukatar sa ta hanyar halal yanada lada akan haka"[190].

An kuma karvo daga Abu sa'id Xan Abu burdata daga baban sa daga kakan sa daga manzon Allah s.a.w yace: " akan ko wani musulmi akwai sadaka sai sukace: idan be samu bafa? Sai yace: sai ya taimaki Mai son yin wani bukatar sa, sai sukace idan kuma sai samu bafa? Sai yace: sai yayi umurni da kyakyawan aiki kuma ya hanu daga sharri hakan sadaka ne a gareshi"[191].

---

[190] Muslim ne ya rawaito shi (595)
[191] Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn

## 2. falalar ciyar da Abunci da ba Mai Azumin abun bude baki:

Ciyar da Abunci yana daga cikin siffofin bayi Allah masu tsoron sa da biyayya kamar yadda yazo cikin littafin Allah Maxaukaki:

﴿ وَيُطۡعِمُونَ ٱلطَّعَامَ عَلَىٰ حُبِّهِۦ مِسۡكِينٗا وَيَتِيمٗا وَأَسِيرًا ٨ ﴾

Ma'ana: " suna ciyar da Abuncin da suke da bukatar sa ga Miskinai da Marayu da fursinonin yaki (8)[192].

Kuma yana daga cikin sabAbu na shiga aljanna, an karvo Hadis daga Abdullah Xan salam Allah ya kara masa yarda yace: lokacin da manzon Allah s.a.w yazo sai mutane sukaja baya dashi suka tsorata na kasance daga daga cikin u amma bayan naga fuskar sa sai nasan cewa lallai wannan ba fuskar makaryaci bane, ya kasance farkon Abunda nafaraji yana cewa shine:

أَفْشُوا السَّلاَمَ ، وَأَطْعِمُوا الطَّعَامَ ، وَصِلُوا الأَرْحَامَ ، وَصَلُّوا وَالنَّاسُ نِيَامٌ ، تَدْخُلُوا الْجَنَّةَ بِسَلاَمٍ

Ma'ana: " ku yaxa Sallama a tsakanin ku kum ku ciyar da Abinci kuma ku sadar da zumunci kuyi Salla a lokacin da mutane suke Bacci zaku shiga aljanna cikin aminci"[193].

Acikin wannan zamanin namu kuwa Abunda yafi fitowa fili na ciyarwa na falala shine aikin ciyar da masu Azumin Abuncin bude baki.

- **Falalar ciyar da Mai Azumi Abuncin bude baki:**

---

192 Suratul insan

193 Tirmizi da ibn majjah da Ahmad ne suka rawaito shi

A lokacin da musulmai suka kasance masu tausayawa juna kowa yana kallon bukatar Xan uwan sa, ya kasance daga cikin wajibin musulmi ya kalli halin yan uwan sa masu Azumi sun sunada Abunda zasuyi bude baki kuwa dashi ko basu dashi?? Lallai muna gani cikin wannan lokaci dayawa daga cikin yan uwanmu musulumai a garuruwa masu fama da talauci wanda basa samun abun bude baki dashi, saboda hakane kungiyoyin musulunci suka tashi tsayi da shiryawa da yin ayyukan domin ciyar da yan uwanmu masu Azumi bude baki.

Kuma domin manzon Allah ya zaburar da sahabban sa wurin aikata wannan aiki Mai girma sai ya fadi cewa:

مَنْ فَطَّرَ صَائِمًا فَلَهُ مِثْلُ أَجْرِهِ مِنْ غَيْرِ أَنْ يَنْقُصَ مِنْ أَجْرِهِ شَيْءٌ ، وَمَنْ جَهَّزَ حَاجًّا أَوْ جَهَّزَ غَازِيًا أَوْ خَلَفَهُ فِي أَهْلِهِ ، فَلَهُ مِثْلُ أَجْرِهِ مِنْ غَيْرِ أَنْ يَنْقُصَ مِنْ أَجْرِهِ شَيْءٌ .

Ma’ana: " Duk wanda ya ciyar daMai Azumi abun bude baki yana da Ladan Azumin sa ba tare da an rage masa lada daga cikin Ladan Mai Azumin nan ba"[194].

Wannan falala ce kai tsaye na ciyar da Mai Azumin farilla ko kuma na nafila, haka kuma Duk wanda yaba Mai bude baki ruwa ko dAbuno ko kuma wani abun marmari cikin Abunci yayi bude baki dashi to lallai zai samu wannan falala.

An kuma sunnata ma Mutumin da yayi bude baki a wurin wasu mutane yayi masu addu'a kamar yadda Abdullahi Xan zubair Allah ya kara masu yarda yace manzon Allah s.a.w yayi bude baki gidan wani daga cikin sahabbaisai yace:

"أَفْطَرَ عِنْدَكُمُ الصَّائِمُونَ، وَصَلَّتْ عَلَيْكُمُ الْمَلائِكَةُ"

---

[194] Tirmizi ne ya rawaito shi (3332) da ibn majjah (1746)

Ma'ana: " masu Azumi sunyi bude baki a wurin ku kuma bayin Allah sunci Abuncin ku kuma mala'iku sunyi maku addu'a"[195].

## 3. Mahaifa nagari:

Lallai gyaruwan baba da uwa shine gyaruwan yaron su, daga garesu ne yana shan siffofi kyawawa na Qwarai, akan mahaifa ne babban kaso yake na tsirar yaron su Duniya da lahira, idan suka ginashi akan biyayyar Allah ya rabauta a Duniya da lahira idan kuma suka ginashi akan sabon Allah ko kuma kafurci zai wahalu Duniya da lahira, an karvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

"ما من مولود إلا ويولد على الفطرة إلا أن أبويه يهودانه أوينصرانه أو يمجسانه "

Ma'ana: " babu wani yaro da ake Haifa face ana haifan sa ne akan addinin musulunci sai sai iyayen sa su mayar dashi bayahude ko kuma kirista ko kuma Mai bautan wuta".[196]

Haka kuma gyaruwan iyaye sabAbu ne na samun daukaka da karin daraja cikin aljanna, Allah Maxaukaki yace:

﴿ وَالَّذِينَ آمَنُوا وَاتَّبَعَتْهُمْ ذُرِّيَّتُهُم بِإِيمَانٍ أَلْحَقْنَا بِهِمْ ذُرِّيَّتَهُمْ وَمَا أَلَتْنَاهُم مِّنْ عَمَلِهِم مِّن شَيْءٍ ۚ كُلُّ امْرِئٍ بِمَا كَسَبَ رَهِينٌ ﴿٢١﴾ ﴾

Ma'ana: " wanda sukayi imani kuma zuriyar su suka bisu da imani zamu hadasu da zurriyyar su kuma bazamu rage

---

Ibn majjah ne ya rawaito shi (1747) [195]

Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn [196]

masu komai ba cikin aikin su, kowa yana jingine ne da Abunda ya aikata"[197].

Kuma gyaruwan iyaye har wayau anfanin sa yana komawa zuwa ga yayen su anan Duniya kamar yadda Allah Maxaukaki ya fadi xikin suratul kahafi gaMai da marayu guda biyu wanda Allah ya hore masu khidir amincin Allah ya tabVata a gareshi domin ya gina masu Katanga Xan kariya akan dukiyar su da mahaifin su ya bar masu saboda gyaruwan sa, ance kakan su ne na bakwai, cikin faxin Allah Maxaukaki:

﴿وَأَمَّا ٱلْجِدَارُ فَكَانَ لِغُلَٰمَيْنِ يَتِيمَيْنِ فِى ٱلْمَدِينَةِ وَكَانَ تَحْتَهُۥ كَنزٌ لَّهُمَا وَكَانَ أَبُوهُمَا صَٰلِحًا فَأَرَادَ رَبُّكَ أَن يَبْلُغَآ أَشُدَّهُمَا وَيَسْتَخْرِجَا كَنزَهُمَا رَحْمَةً مِّن رَّبِّكَ ۚ وَمَا فَعَلْتُهُۥ عَنْ أَمْرِى ۚ ذَٰلِكَ تَأْوِيلُ مَا لَمْ تَسْطِع عَّلَيْهِ صَبْرًا ﴿٨٢﴾﴾

Ma'ana: " amma wannan Katangata kasance ne ga wasu yara su biyu marayu wanda mahaifin su ya kasance Mutumin kirki kasanta akwai dukiyar su sai Allah yaso sai sun girma kafin ya fitar masu da wannan dukiya tasu a matsayin rahama daga ubangijin ka, ban aikata hakan ba da gaban kai na ba"[198].

Saboda haka ne kayi kokari ya kai Xan uwa domin gyara kanka da matarka domin zuriyar ku ta gyaru ku samu tsira da aminci Duniya da lahira.

## 4. Abubuwan da Ladan su yake koma ga Mutum bayan yam utu:

---

[197] Suratul dur

[198] Suratul kahfi

## a) Yaro na gari:

Lallai daga cikin girmanni'imar Allah ga Mutum shine ya azurta shi da zurriyya na Qwarai masu tsoron Allah, wanda zasu rika taimaka masa wurin yima Allah biyayya kuma su zama masu binsa cikin kyautatawa da biyayya, kuma su zaman masa sabAbu na Karin daraja a aljanna, an karvo Hadis daga Abu Huraira Allah yakara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

« إِنَّ ٱللَّهَ عَزَّ وَجَلَّ لَيَرْفَعُ الدَّرَجَةَ لِلْعَبْدِ الصَّالِحِ فِى الْجَنَّةِ فَيَقُولُ يَارَبِّ أَنَّى لِى هَذِهِ فَيَقُولُ بِاسْتِغْفَارِ وَلَدِكَ لَكَ »

Ma'ana: " Allah Maxaukaki yana daga darajar bawan san a Qwarai cikin aljanna, sai yace: ya ubangiji daga ina na samo wannan kuma? Sai yace masa istigfarin yaron ka ne wanda yake maka"[199].

Kuma Allah ya wasafta muminai cikin littafin sa da cewa suna da:

جَنَّٰتُ عَدْنٍ يَدْخُلُونَهَا وَمَن صَلَحَ مِنْ ءَابَآئِهِمْ وَأَزْوَٰجِهِمْ وَذُرِّيَّٰتِهِمْ ۖ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ يَدْخُلُونَ عَلَيْهِم مِّن كُلِّ بَابٍ

Ma'ana: " Aljanna ta kololuwa zasu shiga da wanda suka shiryu cikin iyayen su da matayen su da zurriyar su, mala'iku kuma suna shiga wurin su ta ko wani kofa"[200].

Kuma daga cikin addu'ar mala'iku ga muminai shine Allah ya hada iyaye da yaran su muminai, Allah Maxaukaki yace ta bakin su:

---

Ahmad ne ya rawaito shi (1068) 199

i suratul ra'ad 200

﴿ ٱلَّذِينَ يَحۡمِلُونَ ٱلۡعَرۡشَ وَمَنۡ حَوۡلَهُۥ يُسَبِّحُونَ بِحَمۡدِ رَبِّهِمۡ وَيُؤۡمِنُونَ بِهِۦ وَيَسۡتَغۡفِرُونَ لِلَّذِينَ
ءَامَنُواْ رَبَّنَا وَسِعۡتَ كُلَّ شَيۡءٖ رَّحۡمَةٗ وَعِلۡمٗا فَٱغۡفِرۡ لِلَّذِينَ تَابُواْ وَٱتَّبَعُواْ سَبِيلَكَ وَقِهِمۡ
عَذَابَ ٱلۡجَحِيمِ ٧ رَبَّنَا وَأَدۡخِلۡهُمۡ جَنَّٰتِ عَدۡنٍ ٱلَّتِي وَعَدتَّهُمۡ وَمَن صَلَحَ مِنۡ ءَابَآئِهِمۡ
وَأَزۡوَٰجِهِمۡ وَذُرِّيَّٰتِهِمۡۚ إِنَّكَ أَنتَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٨ ﴾

Ma'ana: " ka gafartawa wanda suka tuba kuma sukAbu tafarkin ka kuma ka tsiratar dasu daga azabar wutar jahim (7) ya ubangijin mu ka shigar dasu aljanna kololuwa wacce ka masu alkawari dasu da Duk wanda ya shiryu cikin iyayen su da matayen su da zuriyar su, lallai kai mabuwayi ne Mai hikima (8)"[201].

Kuma manzon mu Mai grima ya fadi cewa daga cikin ayyukan da Ladansu baya yanke wa bayan mutuwar Mutum akwai addu'ar yaro na gari kamar yadda Hadis yazo daga abu Huraira daga manzon Allah s.a.w cewa:

"إِذَا مَاتَ الْعَبْدُ انْقَطَعَ عَمَلُهُ إِلَّا مِنْ ثَلَاثٍ ؛ صَدَقَةٍ جَارِيَةٍ، أَوْ عِلْمٍ يُنْتَفَعُ بِهِ، أَوْ وَلَدٍ صَالِحٍ يَدْعُو لَهُ"

Ma'ana: " idan Mutum ya mutu dukkanin ayyukan sa zasu yanke sai guda uku, sadaka Mai gudana ko kuma ilimi wanda ake anfani dashi ko kuma yaro na gari wanda zai rika masa addu'a"[202].

## b) Ilimi Mai anfani:

Daga cikin falalar ilimi da yada shi da karantar dashi shine Vatacce yakan iya shiryuwa dashi, ya kuma tayar da wanda

Suratul gafir [201]
Muslim da abu dawud da tirmizi da nisa'I ne suka rawaito shi [202]

ya gafala, ya kuma karama ma malali dalili da bisira, kuma hajila ya haskaka da hasken sa, kuma shine gadon annabawa, an karvo Hadis daga Abuddar da'i Allah ya kara masa yarda yace: naji manzon Allah s.a.w yana cewa:

مَنْ سَلَكَ طَرِيقًا يَطْلُبُ فِيهِ عِلْمًا سَلَكَ ٱللَّهَ بِهِ طَرِيقًا مِنْ طُرُقِ الْجَنَّةِ ، وَإِنَّ الْمَلائِكَةَ لَتَضَعُ أَجْنِحَتَهَا لِطَالِبِ الْعِلْمِ رِضَاءً بِمَا يَصْنَعُ ، وَإِنَّ فَضْلَ الْعَالِمِ عَلَى الْعَابِدِ كَفَضْلِ الْقَمَرِ لَيْلَةَ الْبَدْرِ عَلَى سَائِرِ الْكَوَاكِبِ ، وَإِنَّ الْعَالِمَ لَيَسْتَغْفِرُ لَهُ مَنْ فِي السَّمَوَاتِ وَمَنْ فِي الأَرْضِ حَتَّى الْحِيتَانُ فِي جَوْفٍ مِنَ الْمَاءِ ، وَإِنَّ الْعُلَمَاءَ وَرَثَةُ الأَنْبِيَاءِ ، وَإِنَّ الأَنْبِيَاءَ لَمْ يُوَرِّثُوا دِينَارًا وَلا دِرْهَمًا ، وَرَّثُوا الْعِلْمَ فَمَنْ أَخَذَهُ فَقَدْ أَخَذَ بِحَظٍّ وَافِرٍ

Ma'ana: " Duk wanda ya kama wata hamya yana neman ilimi a cikin sa, Allah zai sawwake masa kofar shiga aljanna da ita, kuma mala'iku suna shunfida fuka fukan su da daliban ilimin domin yarda da Abunda suke aikatawa, kuma malami komai yana rokan masa gafara hatta kifin dake cikin ruwa, kuma falalar malami akan Mutum Mai bauta kamar falalar wata ne akan sauran taurari, kuma lallai malamai sune magada annabawa, annabawa basu bar gadon dirhami ba ko kuma dinari ba face gadon ilimi da suka bari, Duk wanda yayi riko dashi to Haqiqa yayi ruko da rabo Mai yawa"[203].

Ilimin da ake nufi anan shine ilimi na shari'a. an kuma karvo Hadis daga Abdullahi Xan mas'ud Allah ya kara masa yarda yace: naji manzon Allah s.a.w yana cewa:

نَضَّرَ ٱللَّهَ امْرَءًا سَمِعَ مِنَّا حَدِيثًا فَبَلَّغَهُ كَمَا سَمِعَهُ ، فَإِنَّهُ رُبَّ مُبَلَّغٍ أَوْعَى لَهَا مِنْ سَامِعٍ

---

Abu dawud da ibn majjah ne suka rawaito shi [203]

Ma'ana " Allah yajikan Mutumin daya ji wani abu daga garemu sa'annan ya isar dashi kamar yadda yaji, sau da dama Mai jiyarwa yafi kiyaye wa akan wanda yaji"[204].

An karvo Hadis daga Mu'awiya Xan Abu safyan Allah yakara masu yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

"مَنْ يُرِدِ ٱللَّهُ بِهِ خَيْرًا يُفَقِّهْهُ فِي الدِّينِ".

Ma'ana: " Duk wanda Allah yake son shi da alheri zai fahimtar dashi addini"[205].

Malamai suna da darala Mai girma a wurin Allah, Allah Maxaukaki yace:

﴿ قُلْ هَلْ يَسْتَوِى ٱلَّذِينَ يَعْلَمُونَ وَٱلَّذِينَ لَا يَعْلَمُونَ ۗ ٩ ﴾

Ma'ana: "kace shin wanda ya sani zayyi daidai da wanda be sani ba"[206].

Ya kuma kara fadi har wayau:

﴿ يَرْفَعِ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مِنكُمْ وَٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْعِلْمَ دَرَجَٰتٍ ۚ ١١ ﴾

Ma'ana: " Allah zai daga darajar ku amma wanda aka basu ilimi suna saman ku a daraja"[207].

**Wasu daga cikin hanyoyin yaduwar ilimi:**

Littattafai- buga littafi- yan kananan littattafai- kasuka-yanan gizo- tsangayoyin ilimi- gidan latAbujin- mujalloli- jarudu- gina makarantu da cibiyoyi na musulunci. Wannan wukkanin su akwai lada akan su gwargwadon aikin Mutum

---

[204] Tirmizi da ibn majjah ne suka rawaito shi

[205] Buhari da muslim ne suka rawaito shi

[206] Suratul zumar ayata 9

[207] Suratul mujadala ayata 11

aciki ko dai wallafawa ko kuma yadawa ko bugawa ko kuma daukan nauyin haka da kudi.

**Daga cikin misalin ilimi Mai anfani:**

Karantar da Al-qur'ani da ilimomin sa- karantar da hadisan manzon Allah s.a.w da ilimomin sa da fikihu da ibadu, haka kuma da karantar da imilin da suke taimakawa wurin fahimtar su kamar ilimin harshen larabci na nahawu da sauran su ko kuma wani ilimi wanda zai amfanar da musulmai Duniyan su ko kuma a lahira. Babu shakka ilimin shari'a akwai mutakar bukatar ganin andage akan sa koyan sa da karantar dashi.

## c) Sadaka Mai gudana:

Sadaka m e gudana itace dukkanin wata sadaka wacce anfaninta yake dorewa ga mutane, saboda haka ne Ladanka yake dorewa kuma wannan lada zai ci gaba da daurewa matukar wannan sadaka taka tananan.

Daga cikin misali akan sadaka Mai gudana wacce tayi yawa yanzu kuma take ci gaba da yawaita cikin wannan zamani Alhamdulillah akwa: gina maSallatai ruwan kan hanya, shuka bishiya, wakafi da gidaje da wuraren karatu ga garuruwan talakawa, wannan nau'ukan na karshe suna cikin mafiya falala cikin sadaka saboda dorewar su da kuma shigan da akeyi cikin su domin neman ilimi Mai anfani sai mutane dayawa su amfana dashi cikin mabukata, kuma falalar sadaka ya gaVata a baya.

- **Gina maSallatai:**

Barka gamai aikata alheri Mai kwadayi akansa, dam ace babba wacce ka daure akan haka domin Haqiqa jAbur Xan

Abdullahi Allah ya kara masu yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

« مَنْ بَنَى مَسْجِدًا لِلَّهِ كَمَفْحَصِ قَطَاةٍ أَوْ أَصْغَرَ بَنَى ٱللَّهُ لَهُ بَيْتًا فِي الْجَنَّةِ »

Ma'ana: " Duk wanda ya gina ma Allah Masallaci komai kankantan sa anan Duniya Allah zai gina masa gida a aljanna"[208]

kuma an karvo daga Usman Allah ya kara masa yarda yace: naji manzon Allah s.a.w yana cewa:

« مَنْ بَنَى مَسْجِدًا لِلَّهِ تَعَالَى – قَالَ بُكَيْرٌ حَسِبْتُ أَنَّهُ قَالَ – يَبْتَغِي بِهِ وَجْهَ ٱللَّهِ – بَنَى ٱللَّهُ لَهُ بَيْتًا فِي الْجَنَّةِ »

Ma'ana: "Duk wanda ya gina Masallaci domin Allah Maxaukaki- Bukair yace ina tsammanin yace: yana neman yardar Allah da hakan- Allah zai gina masa gida a aljanna"[209]. Ibn isa yace cikin wata ruwaya: (Allah zai gina masa gida irin sa a cikin aljanna). Allah kuma ya yAbu masa raya gidan sa ya kuma wasafta su da imani cikin faxin sa cewa:

إِنَّمَا يَعۡمُرُ مَسَٰجِدَ ٱللَّهِ مَنۡ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ

Ma'ana: " kawai bawanda yake raya Masallacin Allah sai wanda yayi imani da Allah da ranar karshe"[210].

Rayashi yana kasance wa ne ta fuska biyu Allah shine mafi sani, na farko rayashi wanda ake gani na ginashi da sabanta shi da kula dashi, na biyu kuma rayashi nayin Salla a cikinsa

---

[208] Ibn hibban da ibn kuzaimah da Ahmad ne suka rawaito shi

[209] Buhari da muslim ne suka rawaito shi

[210] Suratul taubah ayata 18

da kuma kula da tsabtar sa da kuma taimaka masa da kudi da tsangayoyi na zikiri da tilawar Al-qur’ani.

Allah Maxaukaki yace:

﴿ فِي بُيُوتٍ أَذِنَ ٱللَّهُ أَن تُرۡفَعَ وَيُذۡكَرَ فِيهَا ٱسۡمُهُۥ يُسَبِّحُ لَهُۥ فِيهَا بِٱلۡغُدُوِّ وَٱلۡأٓصَالِ ٣٦ ﴾

Ma’ana: " a cikin wasu gidaje Allah yayi umurni da a tsayar dasu da gina su da kuma tsarkake su kuma a rika karatun Al-qur’ani da zikirin Allah a cikin su, suna masa tasbihi acikin su safiya da maraice (mazaje ne wanda kasuwanci da saye da siyarwa baya hanasu zikirin Allah"[211].

## 5. Yima Xan musulmi murmushi da sakin fuska:

An karvo Hadis daga jAbur Xan Abdullah Allah ya kara masu ‘yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

وَإِنَّ مِنَ الْمَعْرُوفِ أَنْ تَلْقَى أَخَاكَ بِوَجْهٍ طَلْقٍ وَأَنْ تُفْرِغَ مِنْ دَلْوِكَ فِي إِنَاءِ أَخِيكَ

Ma’ana: " yana gada cikin ayyukan lada ya saki fuskanka ga Xan uwanka idan kun hadu ko kuma Karvashi aron gugar ka ya dibi ruwa da ita"[212].

An kuma karvo daga abu darda'i Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

“تَبَسُّمُكَ في وجه أخيك صدقة”

Ma’ana: " kayi ma Xan uwan musulmi murmushi shima sadaka ne"[213].

Suratun nur [211]
Tirmizi ne ya rawaito shi (1970) [212]
Tirmizi ne ya rawaito shi (1956)[213]

murmushi yana gina soyayya da kaunar ka ga Xan uwarka sai yasa ya bude maka zuciyar sa, ya kuma natsu dakai, da haka ne muka zama dukkanin mu masoya juna kamar zuciyar Mutum daya a jiki daya sai mu kasance kamar yadda manzon Allah s.a.w ya wasiftamu cikin Hadisn sa wanda aka rawaito daga nu'umanu Xan bashir Allah ya kara masu yarda cewa:

«مَثَلُ المؤمنين في تَوَادِّهم وتراحُمِهم وتعاطُفِهم : مثلُ الجسد ، إِذا اشتكى منه عضو: تَدَاعَى له سائرُ الجسد بالسَّهَرِ والحُمَّى».

Ma'ana: " misalin mumunai cikin soyayyar su da tausayi da rahama kamar misalin gini ne shashi yana karfafa wani shashi idan wani shashi yana masa ciwo sai sauran sassan su sauka da zazzAbu da ciwo"[214].

Sai ya zama Mutum ya samu Ladan sadaka da haka da kuma soyayyar yan uwan sa.

## 6. Bayar da kyauta:

An karvo Hadis daga abu Huraira Allah ya kara masa yarda daga manzon Allah s.a.w yace:

لَوْ دُعِيتُ إِلَى كُرَاعٍ لأَجَبْتُ ، وَلَوْ أُهْدِيَ إِلَيَّ ذِرَاعٌ لَقَبِلْتُ

Ma'ana: " da ace za'a gayyace ni zuwa Cinya ko kuma kafar Akuya da amsa gayyata, kuma da za'a bani kautan garin zira'i ko kura'i Xana amsa"[215].

Ya kasance daga cikin sunnar sa amsar kyauta da kuma rashin mayar da ita sai dai idan da wani dalili, an karvo

---

Buhari da muslim ne suka rawaito Hadisn [214]
Buhari da nasa'I ne suka rawaito shi [215]

Hadis daga sa'ab Xan jusamata Allah ya kara masa yarda yace: ya bayar da kyauta jakin daji ga manzon Allah s.a.w sai ya dawomun dashi, lokacin da yaga halin da fuskana ke ciki sai yace:

"إِنَّا لَمْ نَرُدَّهُ عَلَيْكَ إِلا أَنَّا حُرُمٌ"

Ma’ana: " bawai na dawo maka bane da kyautar ka bace hakanan sai saboda an haramta ta"[216]

ya kuma ce

تَهَادُوا تَحَابُّوا

Ma’ana: " ku rika bada kyauta zaku so junan ku",

da kuma kyauta ne zaka lallashi zuciyar Xan uwanka ka kuma jawo soyayyar sa kuma ka tafiyar da wani kulli na kiyayya da yake dashi naka. Kyauta tana kasance tsakanin yan uwa da makwabta da abokanai, ga Aisha nan Allah ya kara mata yarda tanason bayar da kyauta ga makwabta sai tayi tambaya cewa wanene zataba acikin su, an karvod Hadis daga Aisha Allah yakara mata yarda tace:

قُلْتُ: يَا رَسُولَ ٱللَّهَ، إِنَّ لِي جَارَيْنِ فَإِلَى أَيِّهِمَا أُهْدِي؟، قَالَ:"إِلَى أَقْرَبِهِمَا مِنْكَ بَابًا"

Ma’ana: nace ma manzon Allah inada makwabta guda biyu wanene zan ba kyauta a cikin su? Sai yace: " wanda kofarsa yafi kusa da naki"[217].

## 7. Hakkin musulmi akan Xan uwansa:

---

Muslim da Ahmad ne suka rawaito shi [216]
Buhari ne ya rawaito shi (2295)[217]

An karvo Hadis daga abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

حَقُّ الْمُسْلِمِ عَلَى الْمُسْلِمِ خمس ، قِيلَ : مَا هُنَّ يَا رَسُولَ ٱللَّهَ ؟ قَالَ : إِذَا لَقِيتَهُ فَسَلِّمْ عَلَيْهِ ، وَإِذَا دَعَاكَ فَأَجِبْهُ ، وَإِذَا اسْتَنْصَحَكَ بِحَمْدِ ٱللَّهَ فَانْصَحْ ، وَإِذَا عَطَسَ فَشَمِّتْهُ ، وَإِذَا مَرِضَ فَعُدْهُ ، وَإِذَا مَاتَ فَاتْبَعْهُ

Ma'ana: " hakkin musulumi akan Xan uwan sa musulmi guda biyar ne, mayar da Sallama, da gaida mara lafiya, da bin gawar sa, da gaida Mai atishawa da amsa masa kira"[218].

An kuma kara karvowa daga gare shi cikin wani ruwaya ta daban yace: manzon Allah s.a.w yace:

إِذَا لَقِيتَهُ فَسَلِّمْ عَلَيْهِ ، وَإِذَا دَعَاكَ فَأَجِبْهُ ، وَإِذَا اسْتَنْصَحَكَ بِحَمْدِ ٱللَّهَ فَانْصَحْ ، وَإِذَا عَطَسَ فَشَمِّتْهُ ، وَإِذَا مَرِضَ فَعُدْهُ ، وَإِذَا مَاتَ فَاتْبَعْهُ

Ma'ana: " idan ka hadu dashi kayi masa Sallama kuma idan ya gayyaceka ka amsa masa, idan kuma ya nemi nasihar ka kayi masa nasiha, idan kuma yayi atishawa yace Alhamdulillah ka gaishe shi, idan kuma yayi rashin lafiya kaje ka duba shi, idan kuma ya mutu ka raka gawarsa"[219].

## a) Yada Sallama:

Sallama daya ne daga cikin sunan Allah masu kyawu, Allah Maxaukaki yace:

---

Buhari ne ya rawaito shi (1240) [218]
Muslim ne ya rawaito shi (2162) [219]

﴿ هُوَ ٱللَّهُ ٱلَّذِى لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلْمَلِكُ ٱلْقُدُّوسُ ٱلسَّلَٰمُ ٱلْمُؤْمِنُ ٱلْمُهَيْمِنُ ٱلْعَزِيزُ
ٱلْجَبَّارُ ٱلْمُتَكَبِّرُ ۚ سُبْحَٰنَ ٱللَّهِ عَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿٢٣﴾ ﴾

Ma’ana: " shine Allah wanda babu abun bauta bisa cancanta sai shi, almaliku al kuddusu assalamu almuminu almuhaiminu al azizu aljabbaru almukabbiru"[220].

Kuma yana daga cikin sabAbu na yada soyayya a tsakanin musulmai da shiga aljanna, an karvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

وَالَّذِي نَفْسِي بِيَدِهِ لا تَدْخُلُوا الْجَنَّةَ حَتَّى تُؤْمِنُوا ، وَلا تُؤْمِنُوا حَتَّى تَحَابُّوا ، أَوَلا أَدُلُّكُمْ عَلَى شَيْءٍ إِذَا فَعَلْتُمُوهُ تَحَابَبْتُمْ ؟ أَفْشُوا السَّلامَ بَيْنَكُمْ

Ma’ana: " ina rantsuwa da wanda raina ke hannun sa baza ku shiga aljanna ba har sai kunyi imani kuma baza kuyi imani ba har sai kun so junanku shin bazan nuna maku wani Abunda idan kun aikata shi ba zakuso junanku ku yada tSallama a tsakanin ku"[221],

Sallama itace gaisuwar yan aljanna, Allah Maxaukaki yace:

﴿ تَحِيَّتُهُمْ يَوْمَ يَلْقَوْنَهُۥ سَلَٰمٌ ۚ وَأَعَدَّ لَهُمْ أَجْرًا كَرِيمًا ﴾

Ma’ana: " gaisuwar su a ranar da zasu hadu dashi shine Sallama"[222]

Da Sallama ne mala'iku zasu tarbi muminai a kofar shiga aljanna, Allah Maxaukaki yace:

---

[220] Suratul hashri ayata 23
[221] Muslim da ibn majjah da tirmizi ne suka rawaito shi
[222] Suratul ahazab ayata 44

﴿ وَسِيقَ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوْاْ رَبَّهُمْ إِلَى ٱلْجَنَّةِ زُمَرًا ۖ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُوهَا وَفُتِحَتْ أَبْوَٰبُهَا وَقَالَ
لَهُمْ خَزَنَتُهَا سَلَٰمٌ عَلَيْكُمْ طِبْتُمْ فَٱدْخُلُوهَا خَٰلِدِينَ ﴿٧٣﴾ ﴾

Ma’ana: " sai a raka masu tsoron ubangijin su zuwa gag a aljanna kungiya bayan kungiya, idan sun zo sai a bude masu kofofinta ace masu amincin Allah ya tabVata a gareku madalla ku shigeta kuna masu dawwama acikinta"[223].

Kuma yace gaMai da mala'iku a lokacin shigar suwurin muminai a cikin aljanna:

﴿ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ يَدْخُلُونَ عَلَيْهِم مِّن كُلِّ بَابٍ ﴿٢٣﴾ سَلَٰمٌ عَلَيْكُم بِمَا صَبَرْتُمْ ﴾

Ma’ana: " da mala'iku suna shiga zuwa wurin su ta ko wani kofa (23) amincin Allah ya tabbata a gareku"[224].

A wurin maida Sallama kuma an umurce mu da mu mayar da irinta ko kuma wanda ya fita cikin faxin Allah Maxaukaki:

﴿ وَإِذَا حُيِّيتُم بِتَحِيَّةٍ فَحَيُّواْ بِأَحْسَنَ مِنْهَآ أَوْ رُدُّوهَآ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ حَسِيبًا
﴿٨٦﴾ ﴾

Ma’ana: " idan an gaisheku da Sallama mu mayar da wanda tafita ko kuma irinta"[225].

## b) Gaida Mai atishawa:

An karvo Hadis daga Abu musa al ash'ari Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

---

Suratul zumar [223]
Suratul ra'ad [224]
Suratun nisa'I ayata 86 [225]

إِذَا عَطَسَ أَحَدُكُمْ فَحَمِدَ ٱللَّهَ فَشَمِّتُوهُ ، وَإِذَا لَمْ يَحْمَدِ ٱللَّهَ فَلا تُشَمِّتُوهُ

Ma'ana: " idan dayan ku yayi atishawa sai yace Alhamdulillah to ku gaisheshi, idan kuma bece Alhamdulillah ba kada ku gaishe shi"[226].

An karvo kuma daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

إِذَا عَطَسَ أَحَدُكُمْ فَلْيَقُلْ : الْحَمْدُ لِلَّهِ عَلَى كُلِّ حَالٍ ، وَلْيَقُلِ الَّذِي يَسْمَعُهُ :

يَرْحَمُكَ ٱللَّهُ ، وَيَرُدُّ عَلَيْهِ يَهْدِيكَ ٱللَّهُ وَيُصْلِحُ بَالَكَ .

Ma'ana: " idan dayan ku yayi atishawa yace Alhamdulillah sai Xan uwansa yace masa yarhamukallah, idan yace maka yarhamukallah sai kace masa yahdi kumullahu wa yuslihu balakum"[227]

da wannan ne Mai atishawar da wanda yayi gaisuwar duka zasu samu albarkan addu'a.

Ya kasance daga cikin shiryarwan sa s.a.w idan zayyi atishawa yana rufe fuskar sa da hannun sa ko kuma rigar sa ya rufe sautin sa dashi.

## c) Duba mara lafiya:

An karvo Hadis daga aliyu Allah ya kara maa yarda yace: naji manzon Allah s.a.w yana cewa:

مَا مِنْ مُسْلِمٍ يَعُودُ مُسْلِمًا غُدْوَةً إِلاَّ صَلَّى عَلَيْهِ سَبْعُونَ أَلْفَ مَلَكٍ حَتَّى يُمْسِىَ وَإِنْ عَادَهُ عَشِيَّةً إِلاَّ صَلَّى عَلَيْهِ سَبْعُونَ أَلْفَ مَلَكٍ حَتَّى يُصْبِحَ وَكَانَ لَهُ خَرِيفٌ فِى الْجَنَّةِ

---

[226] Buhari da abu dawu da nasa'I ne suka rawaito shi

[227] Tirmizi ne ya rawaito shi (2745)

Ma’ana: " babu wani musulmi wanda zaije duba Xan uwansa musulmi mara lafiya da sassafe face mala'iku dubu saba'in sun masa addu'a har sai ya yammaci gari idan kuma ya koma da daddare mala'iku dubu saba'in zasu kara masa addu'a har sai ya wayi gari kuma yana da faxin tafiyar shekara daya a gidan aljanna"[228],

an kuma karvo daga saubana Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: " Duk wanda yaje duba mara lafiya bazai kasance ba cikin farfajiyar aljanna har sai ya dawo"[229]a cikin wani lafazi na daban abun muslim:

" wanda yaje duba Xan uwansa musulmi".

## d) Raka gawar sa zuwa maKarvarta:

An karvo kuma daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

"مَنْ تَبعَ جِنَازَةً حَتَّى يُصَلِّيَ عَلَيْهَا، ثُمَّ انْصَرَفَ فَلَهُ قِيرَاطٌ مِنَ الأَجْرِ، وَإِنْ تَبِعَهَا فَصَلَّى عَلَيْهَا ثُمَّ قَعَدَ حَتَّى يُفْرَغَ مِنْ دَفْنِهَا فَلَهُ قِيرَاطَانِ، كُلُّ وَاحِدٍ مِنْهُمَا أَعْظَمُ مِنْ أُحُدٍ"

Ma’ana: " Duk wanda ya raka gawar musulmi domin imani da neman lada kuma yana tare da ita har aka mata Salla kuma aka gama birneta dashi, lallai zai dawo da lada kamar girman dutsen uhudu guda biyu, wanda kuma yayi mata Salla sa'annan ya dawo kafin a birneta yanada Ladan dutsen uhudu"[230]. A lokacin da Abdullahi Xan Umar yaji wannan

---

Tirmizi ne ya rawaito shi (969) [228]
Muslim ne ya rawaito shi (2569)[229]
Buhari da muslim ne suka rawaito shi[230]

Hadis sai yace: Haqiqa munyi sakaci da lada kamar dutsen uhudu da yawa.[231].

### e) Taimakon sa akan gaskiya:

An karvo Hadis daga Anas Xan malik Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

انْصُرْ أَخَاكَ ظَالِمًا أَوْ مَظْلُومًا ، قَالُوا : يَا رَسُولَ ٱللَّهِ ، هَذَا يَنْصُرُهُ مَظْلُومًا ، فَكَيْفَ يَنْصُرُهُ ظَالِمًا ؟ قَالَ : تَمْنَعُهُ مِنَ الظُّلْمِ

Ma'ana: " ka taimaki Xan uwanda wanda yayi zalumci ko kuma aka zalumta, sai wani Mutum yace: ya manzon Allah zan taimake shi idan an zalumce shi amma idan shine yayi zalumcin fa yaya kake gann zan taimakeshi? Sai yace: ka hanashi yin zalumcin lallai ka taimakeshi"[232].

Daga cikin wannan Hadis zai bayyanar mana cewa taimako da gaskiya ya kasu gida biyu:

**Na farkon su**, taimakon wanda aka zalumta na tsaya masa gwargwadon iyawar mu da taimaka masa har sai an dawo masa da hakkin sa ko dai da ranka ko kudin ka ko kuma addu'ar ka kuma acikin haka akwai lada Mai girma, manzon Allah s.a.w yace:

وَاللَّهُ فِي عَوْنِ الْعَبْدِ، مَا كَانَ الْعَبْدُ فِي عَوْنِ أَخِيهِ

Ma'ana: " Allah yana cikin taimakon Mutum matukar Mutum yana cikin taimakon Xan uwansa"[233].

Ya kuma kara fadi har wayau:

---

[231] Buhari da muslim ne suka rawaito shi
[232] Buhari da tirmizi ne suka rawaito shi
[233] Muslim ne ya rawaito shi(2699)

مَنْ فَرَّجَ عَنْ مُسْلِمٍ كُرْبَةً فِي الدُّنْيَا، فَرَّجَ ٱللَّهُ عَنْهُ كُرْبَةً مِنْ كُرَبِ يومِ الْقِيَامَةِ

Ma'ana: " Duk wanda ya yayewa wani musulmi damuwar sa na Duniya Allah zai zai yaye masa damuwa cikin damuwar ranar Al-qiyama"

taimakon sa da rai yana kasancewa ne da jajircewa da kanka ko kuma shiga masa tsakiya ko kare masa mutuncin sa ko kuma kareshi, yana kuma kasancewa da kudi ta hanyar bashi taimakon kudi da sadaka domin yayi anfani dashi wurin kwato hakkin sa ko kuma yi masa addu'a a bayan idon san a samun nasara da kuma yayewan damuwar sa da bakin cikinsa, a cikin yi masa addu'a Hadis yazo daga abuddar da'i Allah yakara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

مَا مِنْ عَبْد مُسْلِم يدعوا لأَخِيهِ في ظَهْرِ الْغَيْبِ إِلاَّ قَالَ الْمَلَكُ وَلَكَ مِثْلُ ذَلِكَ

Ma'ana: " babu wani Mutum musulmi wanda zayyima Xan uwansa addu'a a bayan idon sa face mala'ika yace masa kaima kanada irin Abunda ka roka masa"[234].

**Na biyun su**, taimakon sa idan shi yayi zalumcin ta hanyar hanashi zalumcin ta hanyar tsayawa a gabansa kuma kayi masa addu'a ta shiriya da gyaruwa, acikin wannan taimakon akwai tsaro da zaman lafiya ga zaman takewar al'umma baki dayan sa da kuma kare cucarwa koda kuwa hakan zai kai ga yakar sa ne har sai ya dawo kan hanya ya bar barnar da yakeyi, Allah Maxaukaki yace:

234 Buhari da muslim ne suka rawaito shi

﴿ وَإِن طَآئِفَتَانِ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٱقۡتَتَلُواْ فَأَصۡلِحُواْ بَيۡنَهُمَاۖ فَإِنۢ بَغَتۡ إِحۡدَىٰهُمَا عَلَى ٱلۡأُخۡرَىٰ فَقَٰتِلُواْ ٱلَّتِي تَبۡغِي حَتَّىٰ تَفِيٓءَ إِلَىٰٓ أَمۡرِ ٱللَّهِۚ فَإِن فَآءَتۡ فَأَصۡلِحُواْ بَيۡنَهُمَا بِٱلۡعَدۡلِ وَأَقۡسِطُوٓاْۖ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُقۡسِطِينَ ٩ ﴾

Ma’ana: " idan mutane biyu daga cikin muminai suna fada kayi sulhu a tsakanin su, idan daya yayi dagawa akan dayan ku yaki wanda yayi dagawar har sai ya dawo zuwa ga al'amarin Allah, idan ya hanu kuyi sulhu a tsakain su da adalci, kuyi adalci "[235].

Hakan ya faru ne saboda tushe kofofin barna da yada adalci da daidaito a tsakanin al'umma ya wanzar da natsuwa a tsakanin mutane ta yadda Mai karfi bazai zalumci mara karfi ba, a cikin hasken wannan fadakarwan na musulunci shugaban mu Abubakar siddik ya rubuta manhaji domin bawa shugaba damar taimakon wanda yake shugabanta cikin faxin sa cewa: (Mai karfi a wuri na mara karfi ne zan amshi hakkin da banashi ba a wurin sa, mara karfi kuma a wurina Mai karfi ne saboda zan kwato masa hakkin sa)[236].

## 8. Kawar da wani abun cutarwa daga hanya:

[An karvo Hadis daga Abu malik al ash'ari Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

الطَّهُورُ شَطْرُ الإِيمَانِ

---

[235] Muslim da baihaki ne suka rawaito shi

[236] Suratul hujurat

Ma’ana: " tsarki rabin imani ne"[237]

tsarki yana cikin tsafta kuma sunada matsayi Mai girma a musulumci. Kawar da abun cutarwa daga hanya shine mafi karancin imani, manzon Allah s.a.w yace:

"الإِيمَانُ بِضْعٌ وَسَبْعُونَ شُعْبَةً، أَعْلاهَا شَهَادَةُ أَنْ لا إِلَهَ إِلا ٱللَّهَ، وَأَدْنَاهَا إِمَاطَةُ الأَذَى عَنِ الطَّرِيقِ، وَالْحَيَاءُ شُعْبَةٌ مِنَ الإِيمَانِ"

Ma’ana: " imani yanki saba'in da bakwai ne zuwa tara, mafi falalar su shine faxin la'ilaha illah, mafi kankantar su kuma shine kawar da cuta akan hanya"[238].

An karvo kuma daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

لَقَدْ رَأَيْتُ رَجُلا يَتَقَلَّبُ فِي الْجَنَّةِ فِي شَجَرَةٍ قَطَعَهَا مِنْ ظَهْرِ الطَّرِيقِ تُؤْذِي النَّاسَ

Ma’ana: " Haqiqa naga wani Mutum yana kai komo cikin aljanna saboda wata bishiya dayakawar da ita daga hanya wacce take cutar da mutane"[239].

An kuma kara karvowa daga gareshi Allah ya kara yarda a agareshi cewa manzon Allah s.a.w yace:

بَيْنَمَا رَجُلٌ يَمْشِي بِطَرِيقٍ إِذْ وَجَدَ غُصْنَ شَوْكٍ عَلَى الطَّرِيقِ فَأَخَذَهُ فَشَكَرَ ٱللَّهَ لَهُ فَغَفَرَ لَهُ

Ma’ana: " a lokacin da wani Mutum yake tafiya akan hanya sai yaci karo da wata kaya sai ya dauke ta ya kawar da ita

[237] Muslim ne ya rawaito shi(223)
[238] Buhari da muslim ne suka rawaito shi
[239] Muslim ne ya rawaito shi(1914)

daga hanya sai Allah ya gode masa akan haka ya gafarta masa"[240].

## 9. Da saurarawa talaka wanda kake binsa bashi da kuma kawar da kai daga wanda yake cikin kunci:

an karvo Hadis daga Abu katada al Ansari Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

« مَنْ سَرَّهُ أَنْ يُنْجِيَهُ ٱللَّهَ مِنْ كُرَبِ يَوْمِ الْقِيَامَةِ فَلْيُنْظِرْ مُعْسِرًا أَوْ لِيَضَعْ عَنْهُ »

Ma’ana: " wa nene yake son Allah ya tsiratar dashi daga cikin kunci da damuwar ranar Al-qiyama to ya yayewa wanda yake cikin kunci ko kuma ya yafe masa"[241].

Da kuma Hadisn wani Mutum wanda yake kawar dakai daga mutane idan yana binsu bashi, an karvo daga manzon Allah s.a.w yace:

« كَانَ رَجُلٌ يُدَايِنُ النَّاسَ فَإِذَا أَعْسَرَ الْمُعْسِرُ قَالَ لِفَتَاهُ تَجَاوَزْ عَنْهُ فَلَعَلَّ ٱللَّهَ يَتَجَاوَزُ عَنَّا فَلَقِيَ ٱللَّهَ فَتَجَاوَزَ عَنْهُ »

Ma’ana: " wani Mutum ya kasance yana bin mutane bashi ya kasance yana cema yaron sa idan kaje gun wanda bashi dashi ka kawar dakan ka daga gareshi wata kila Allah zai kawar dakai daga garemu muma sai ya hadu da Allah sai ya kawar dakansa daga laifukan sa"[242].

---

Buhari da muslim da tirmizi ne suka rawaito shi [240]
Muslim ne ya rawaito shi(1563) [241]
Muslim ne ya rawaito shi (1562)[242]

An kuma karvo Hadis daga Huzaifa Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

تَلَقَّتِ الْمَلائِكَةُ رُوحَ رَجُلٍ مِمَّنْ كَانَ قَبْلَكُمْ ، فَقَالُوا : أَعَمِلْتَ مِنَ الْخَيْرِ شَيْئًا ؟ قَالَ : لاَ قَالُوا : تَذَكَّرْ قَالَ : كُنْتُ أُدَايِنُ النَّاسَ فَآمُرُ فِتْيَانِي أَنْ يُنْظِرُوا الْمُعْسِرَ وَيَتَجَاوَزُوا عَنِ الْمُوسِرِ قَالَ : فَقَالَ ٱللَّهُ عَزَّ وَجَلَّ : تَجَوَّزُوا عَنْهُ

Ma’ana: " Mala'iku sun haxu da ran wani Mutum cikin mutanen da suka gabace ku sai sukace masa: shin kasan wani cikin alheri? Sai yace a'a bansani ba, sai suka ce mas aka tuna dai, sai yace na kasance idan inAbun mutane bashi ina umurtan yaro na da ya rika jinkirta ma wanda suke cikin kunci na rashi kuma ya rika kawar dakai daga wanda bashi dashi, sai yace: Allah Maxaukaki ya kawar dakai daga gareka kaima"[243].

## 10. Kira zuwa ga Allah:

Allah Maxaukaki yace:

﴿ وَمَنْ أَحْسَنُ قَوْلًا مِّمَّن دَعَآ إِلَى ٱللَّهِ وَعَمِلَ صَٰلِحًا وَقَالَ إِنَّنِى مِنَ ٱلْمُسْلِمِينَ ﴿٣٣﴾ ﴾

Ma’ana: " wanene yafi Magana Mai kyau akan wanda yayi kira zuwa ga Allah kuma yace ni ina cikin musulmai (33)"[244]. Kira zuwa ga Allah al'amarin ta Mai girma ne sannan kuma wajiba ce wanda mutane da dama suka manta da ita cikin musulman mu nayau. Kofa ne Mai girma na shiriyan mutane zuwa ga addinin gaskiya, da isar da hasken

[243] Muslim ne ya rawaito shi (1560)
[244] Suratu fussilat

muslunci zuwa ga faxin Duniya. Da'awa ba kawai ya takaita bane akan mutanen da ba musulmai ba domin shiryar dasu zuwa ga musulunci, da'awa ta kunshi kitran musulmai zuwa ga manhaji Mai karfi da kuma fadakar da wasu su bar yin bidi'o'i da kuma ayyukan Vatan da shirka. Muna da koyi Mai kyau gada manzon Allah s.a.w shugaban masu da'awa lokacin daya kira mutanen sa domin su bar aikata shirka da komawa zuwa ga bautan Allah shi kaxai, dagan kuma yayi sulhu da kuraishawa a hudaibiya, har ya koma yana kiran sauran kAbulu da garuruwa wanda suke kewaye dashi zuwa ga musulunci, ya aika masu da yan sako wanda zasu isar masu da da'awar gaskiya zuw aga sarakunan kasashe da manyan kAbulu, karantarwan sa s.a.w ta kasance tattare da lallashi da rangwaMai yana Mai riko da umurnin Allah Maxaukaki:

﴿ ٱدْعُ إِلَىٰ سَبِيلِ رَبِّكَ بِٱلْحِكْمَةِ وَٱلْمَوْعِظَةِ ٱلْحَسَنَةِ ۖ وَجَٰدِلْهُم بِٱلَّتِى هِىَ أَحْسَنُ ۚ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ أَعْلَمُ بِمَن ضَلَّ عَن سَبِيلِهِۦ ۖ وَهُوَ أَعْلَمُ بِٱلْمُهْتَدِينَ ١٢٥ ﴾

Ma’ana: " kayi kira zuwa ga tafarkin ubangijin ka da hikima da kuma lafuzza masu kyau"[245]

daga nan kuma sai sahabban sa sukayi koyi da irin manhajin sa bayan sa har suka isar da musulunci zuwa faxin Duniya kuma hasken say a haskaka mutane karni dayawa suna masu koyi da faxin Allah Maxaukaki:

﴿ قُلْ هَٰذِهِۦ سَبِيلِىٓ أَدْعُوٓا۟ إِلَى ٱللَّهِ ۚ عَلَىٰ بَصِيرَةٍ أَنَا۠ وَمَنِ ٱتَّبَعَنِى ۖ وَسُبْحَٰنَ ٱللَّهِ وَمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ١٠٨ ﴾

[245] Suratun nahli ayata 125

Ma'ana: " kace wannan shine tafarki na ina Mai kira zuwa ga Allah, akan Hujja ni da wanda suka bini, tsarki ya tabVata ga Allah kuma ban kasance ba cikin masu yin shirka (108)"[246].

A cikin wannan zamani namu jahilci ya yadu cikin tsakiyar garuruwan musulmai dayawa, wanda suke hana mutane sanin musulunci kuma suna masu dashashe hasken musuluncin a fuskan wand aba musulmai ba gabas da yamma, sabod ahaka ne ya zama wajibi ga kowani Mutum Mai iko cikin musulmai na wata fikira ce ko kuma taimako na dukiya ya taimaka wurin yada musulunci ya kuma yi anfani da damar sa wurin yada da'awa Mai albarka.

## 11. Shiriyan Mutum ga musulunci da sunna Mai kyau:

Daga cikin alamun amsuwar da'awa zuwa ga Allah shine shiriyan mutane zuwa ga musulunci, kuma masu rabo nawa ne wanda Allah yayi masu gam da katar ya shiryar da bayinsa ta dalilin sa kamar yadda manzon Allah s.a.w ya fadi ga Aliyu Allah ya kara masa yardalokacin daya turashi zuwa ga bude garin khaibara:

"لأَنْ يَهْدِىَ ٱللَّهَ بِكَ رَجُلاً وَاحِدًا خَيْرٌ لَكَ مِنْ أَنْ يَكُونَ لَكَ حُمْرُ النَّعَمِ ».

Ma'ana: " ka sani cewa Allah ya shiryar da wani Mutum daya ta sanadiyyar ka yafi maka alheri a baka tarin rakuma jajaye masu tsada"[247],

Suratu yusuf [246]

Buhari da muslim ne suka rawaito shi [247]

Abunda ake nufi shine kada burin Mutum ya zama na tara dabbaobi da abubuwan rayuwan Duniya anaso ya zama burin sa shine shiryar da mutane zuwa ga musulunci.

Ya Allah kasanya mu zama masu kira gareka shiryayyu masu shiryarwa ba Vatattu ba ko masu Vatarwa.

Shiriyar Mutum yana kasancewa ne kodai shiryar dashi zuwa ga dagewa da yima Allah biyayya ko kuma shiryar da wand aba musulmai ba zuwa ga musulunci, dukkanin su kanada lada akai Mai girma har zuwa ranan sakamako, idan ka kasance yakai Xan uwa cewa bazaka iya shiryar da mutane ba ta hanyar fuskantar su saboda karancin ilimin ka ko kuma rashin lokaci ko kuma hanyar da ta dace da hakan to Haqiqa Allah ya hore mana cibiyoyi a kasar mu wanda suke da'awa ga wand aba musulmai ba ko kuma bibiyan musulmai da fadakar dasu kamar su (cibiyoyin fadakar da mutane) (jam'iyyu na taimako) ka bada naga gudun mawar na kudi gare su domin ka samu Ladan shiryar da mutane. Sannan hakan zai zamn maka lada nunki ba nunki domin aikin shiryar da mutanen ya kasance ne ta dalilin ka ko kuma a hannun ka za'a nunka maka Ladan ka, Jarir Xan Abdullahi yace Allah ya kara masa yarda: manzon Allah s.a.w yace:

" مَنْ سَنَّ فِي الإِسْلامِ سُنَّةً صَالِحَةً كَانَ لَهُ أَجْرُهَا ، وَأَجْرُ مَنْ عَمِلَ بِهَا مِنْ بَعْدِهِ إِلَى يَوْمِ الْقِيَامَةِ ، لا يُنْقَصُ مِنْ أُجُورِهِمْ شَيْءٌ "

Ma’ana: " Duk wanda ya fara wani aiki cikin musulunci yana da Ladan haka da Ladan Duk wanda yayi aiki da ita Vatare da an rige masu komai ba cikin ladar su"[248].

an kuma karvo daga Xan mas'ud Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

---

Muslim da nasa'I da ibn majjah ne suka rawaito shi [248]

"مَنْ دَلَّ عَلَى خَيْرٍ فَلَهُ مِثْلُ أَجْرِ مَنْ فَعَلَهُ"

Ma'ana: " Duk wanda yayi nuni zuwa ga aikin alheri yanada lada irin na Mutumin daya aikata wannan alheri"[249].

An karvo kuma daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

"مَنْ دَعَا إِلَى هُدًى كَانَ لَهُ مِنَ الْأَجْرِ مِثْلُ أُجُورِ مَنْ تَبِعَهُ مِنْ غَيْرِ أَنْ يَنْقُصَ مِنْ أُجُورِهِمْ شَيْئًا"

Ma'ana: " Duk wanda yayi kira zuwa ga shiriya yana da lada irin Ladan wanda ya bishi"[250].

Daga cikin hanyoyi na shiryarwa shine buga littattafai da kaset da makamantan su kamar yadda ya gamaVata a baya cikin bAbun ilimi Mai anfani da kuma daukan nauyin da'awa cikin faxin Duniya shima kanada Ladan wanda ya shiryu a hannnun su.

## 12. Biyayyar mata ga mijinta:

An karvo Hadis daga Abdullahi Xan Abu aufa Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

"لَا تُؤَدِّي الْمَرْأَةُ حَقَّ رَبِّهَا حَتَّى تُؤَدِّي حَقَّ زَوْجِهَا"

Ma'ana: " mace Vata bayar da hakkin ubangijinta har sai ta bada hakkin mijinta"[251]..

Ya kuma kara cewa har wayau:

---

[249] Muslim da tirmizi da abu dawud ne suka rawaito shi
[250] Muslim da tirmizi da abi dawud ne suka rawaito shi
[251] Ibn majjah ne ya rawaito shi (1853)

"إِذَا صَلَّتِ الْمَرْأَةُ خَمْسَهَا، وَصَامَتْ شَهْرَهَا، وَحَصَّنَتْ فَرْجَهَا، وَأَطَاعَتْ بَعْلَهَا، دَخَلَتْ مِنْ أَيِّ أَبْوَابِ الْجَنَّةِ شَاءَتْ"

Ma'ana: " idan mace tayi salloli biyar da Azumi kuma ta kiyaye farjinta ta kuma yima mijinta biyayya, za'a ce mata ta shiga aljanna ta kofar da taga dama"[252].

Biyayyar muji yana kewaye da gyaruwa da tsiran iyali da kuma tabVatan halinsu idan ya kasance karkashin shari'ar musulunci saboda babu biyayya ga wani mahaluki cikin sabon Allah, iyali kamar jirgin ruwa ne wanda miji shine direban ta, babu tsira ga wannan jirgi sai da masa biyayya shi kuma yaja ragaminta tare da shawartan iyalan nasa, Allah Maxaukaki yace:

﴿ٱلرِّجَالُ قَوَّٰمُونَ عَلَى ٱلنِّسَآءِ بِمَا فَضَّلَ ٱللَّهُ بَعْضَهُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ وَبِمَآ أَنفَقُواْ مِنْ أَمْوَٰلِهِمْۚ فَٱلصَّٰلِحَٰتُ قَٰنِتَٰتٌ حَٰفِظَٰتٌ لِّلْغَيْبِ بِمَا حَفِظَ ٱللَّهُۚ ٣٤﴾

Ma'ana: " mazaje sune Jagorori akan mata da Abunda Allah ya daukaka wani shashin su dashi akan sashi da kuma Abunda suke ciyarwa na dukiyoyin su,su kuma salihan mata masu yawan ibada da kiyaye kansu a bayan ido da Abunda Allah ya kiyaye su"[253].

Ya ishe mace Hujja cikin biyayya ga mijinta Hadisn da aka rawaito daga daga ummu salmah Allah ya kara mata yarda na maganar manzon Allah s.a.w cewa:

" أَيّمَا اِمْرَأَة مَاتَتْ وَزَوْجها رَاضٍ عَنْهَا دَخَلَتْ الْجَنَّة "

---

[252] Ahmad ne ya rawaito shi (1662)
[253] Suratun nisa'I ayata 34

Ma’ana: " duk macen da ta mutu mijinta ya yarda da ita zata shiga aljanna"[254].

Barka ga mace ta Qwarai Mai neman aljannan ubangijinta da yardar sa.

## 13. Daga cikin Addu'ar da suke amfanar Mutum da iyalan sa:

### 1) Addu'ar shiga gida:

An karvo Hadis daga abu musa al ash'ari Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

"اللَّهُمَّ إِنِّي أَسْأَلُكَ خَيْرَ الْمَوْلِجِ وَخَيْرَ الْمَخْرَجِ ، بِاسْمِ ٱللَّهِ وَلَجْنَا ، وَباسْمِ ٱللَّهِ خَرَجْنَا ، وَعَلَى ٱللَّهِ رَبِّنَا تَوَكَّلْنَا ، ثُمَّ يُسَلِّمُ عَلَى نَفْسِهِ ".

Ma’ana: " ya Allah ina roqon ka alherin kofar shiga da alherin kofar fita, mun shiga da sunan Allah, kuma mun fita da sunan Allah kuma ga ubangijinmu muka dogara"[255].

An kuma karvo daga JAbur Xan Abdullahi Allah ya kara masu yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

« إِذَا دَخَلَ الرَّجُلُ بَيْتَهُ فَذَكَرَ ٱللَّهَ عِنْدَ دُخُولِهِ وَعِنْدَ طَعَامِهِ قَالَ الشَّيْطَانُ : لاَ مَبِيتَ لَكُمْ وَلاَ عَشَاءَ وَإِذَا دَخَلَ فَلَمْ يَذْكُرِ ٱللَّهَ عِنْدَ دُخُولِهِ قَالَ الشَّيْطَانُ أَدْرَكْتُمُ الْمَبِيتَ فَإِذَا لَمْ يَذْكُرِ ٱللَّهَ عِنْدَ طَعَامِهِ قَالَ أَدْرَكْتُمُ الْمَبِيتَ وَالْعَشَاءَ ».

---

[254] Tirmizi da ibn majjah ne suka rawaito shi

[255] Abu dawud ne ya rawaito (5096) kuma Hadis ne Mai rauni

Ma’ana: " idan Mutum zai shiga gidan sai ya ambaci sunan lokacin shigar sa da lokacin da zai fara cin Abunci sai Shaidan yace shikenan bamu da wurin kwanan da Abunci yau, amma idan ya shiga be ambaci Allah ba lokacin shigar sai Shaidan yace kun samu wurin kwana, kuma idan be ambaci Allah ba lokacin cin Abuncin sa sai Shaidan yace kun samu Abunci"[256], mu kare gidan mu daga sharrin Shaidan da Xangin sa yaku yan uwana da ambaton Allah da addu'a lokacin da zamu shiga gida, Allah ya mana tsari da Shaidan baki daya ni daku, amin.

## 2) Addu'ar saduwa (jima'i):

An karvo Hadis daga Abdullahi Xan Abbas Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

« أَمَا لَوْ أَنَّ أَحَدَهُمْ يَقُولُ حِينَ يَأْتِى أَهْلَهُ بِاسْمِ ٱللَّهِ ، اللَّهُمَّ جَنِّبْنِي الشَّيْطَانَ ، وَجَنِّبِ الشَّيْطَانَ مَا رَزَقْتَنَا ، ثُمَّ قُدِّرَ بَيْنَهُمَا فِى ذَلِكَ ، أَوْ قُضِىَ وَلَدٌ ، لَمْ يَضُرَّهُ شَيْطَانٌ أَبَدًا »

Ma’ana: " da ace dayan zai fadi idan yazo saduwa da iyalin sa cewa: ya Allah ka nesantar Xani da Abunda zaka azurtani dashi daga Shaidan, idan yasamu yaro daga wannan saduwar Shaidan bazai cutar dashi ba kuma bazaici galaba ba akansa"[257]

da wannan za'a samu iri na kawarai tun daga ranan farko har ta girma a rubutaba mashi gyaruwa a nan Duniya da lahirata fitar da tsirrau masu kyau da izinin Allah kuma ta

Muslim da ibn hibban da Ahmad ne suka rawaito shi [256]
Malam Hadis su shida duk sun rawaito shi [257]

kasance cikin bayin Allah salihai, Allah Maxaukaki yana cewa:

﴿ إِلَّا عِبَادَكَ مِنْهُمُ ٱلْمُخْلَصِينَ ۝٤٠ ﴾

Ma'ana: " sai dai bayin ka daga cikin su da suka kasance salihai"[258].

Wannan sune bayin da suka tsarkaka daga makircin Shaidan da sharrin sa.

## 14. Ziyara da kuma soyayya domin Allah:

An karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

سَبْعَةٌ يُظِلُّهُمُ ٱللَّهَ يَوْمَ الْقِيَامَةِ فِى ظِلِّهِ يَوْمَ لاَ ظِلَّ إِلاَّ ظِلُّهُ إِمَامٌ عَادِلٌ ، وَشَابٌّ نَشَأَ فِى عِبَادَةِ ٱللَّهَ عَزَّ وَجَلَّ ، وَرَجُلٌ ذَكَرَ ٱللَّهَ فِى خَلاَءٍ فَفَاضَتْ عَيْنَاهُ ، وَرَجُلٌ كَانَ قَلْبُهُ مُعَلَّقًا فِى الْمَسْجِدِ ، وَرَجُلاَنِ تَحَابَّا فِى ٱللَّهَ وتفرقا عليه

Ma'ana: " Mutum bakwai Allah zai masu inuwa cikin inuwar sa ranan da babu wata inuwa sai inuwar sa sai ya anbata daga cikin su mutane guda biyu wanda sukayi abota domin Allah sun hadu akan sa kuma sun rabu akansa"[259].

An karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

أَنَّ رَجُلا زَارَ أَخًا لَهُ فِي قَرْيَةٍ أُخْرَى فَأَرْصَدَ ٱللَّهَ عَلَى مَدْرَجَتِهِ مَلَكًا ، فَلَمَّا أَتَى عَلَيْهِ ، قَالَ : أَيْنَ تُرِيدُ ؟ قَالَ : أُرِيدُ أَخًا لِي فِي هَذِهِ الْقَرْيَةِ ، فَقَالَ : هَلْ لَهُ عَلَيْكَ مِنْ

[258] Suratul hijri
[259] Buhari da muslim ne suka rawaito shi

نِعْمَةٍ تَرُدُّهَا ؟ قَالَ : لا غَيْرَ أَنِّي أَحْبَبْتُهُ فِي ٱللَّهِ ، قَالَ : فَإِنِّي رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيْكَ بِأَنَّ

ٱللَّهَ عَزَّ وَجَلَّ قَدْ أَحَبَّكَ كَمَا أَحْبَبْتَهُ لَهُ

Ma'ana: " wani Mutum ya ziyar ci Xan uwan sa cikin wani gari sai Allah ya aiko masa dawani mala'ika, lokacin da ya riske shi sai yace masa ina kake son zuwa ne haka? Sai yace: inason ziyartan wani Xan uwanane a wani gari, sai yace shi akwai wani abune na alheri da kake nema agunsa? Sai yace: a'a babu nidai kawai inason sa ne domin Allah madaukakaki, sai yace: ni manzon Allah ne zuwa garekada Saqon cewa lallai Allah yana son ka kamar yadda kakeson sa domin sa"[260].

An karvo kuma daga mu'azu Allah ya kara masa yarda yace: naji manzon Allah s.a.w yana cewa:

قال ٱللَّهَ تعالي المتحابون في جلالي لهم منابر من نوريغبطهم النبيون

والشهداء

Ma'ana: " Allah Maxaukaki yace: masu soyayya domin girmana sunada minbari na haske wanda annabawa da shahidai zasu rika masu kishi akansa"[261].

an rawaito daga Abu idris al kaulani Allah ya masa rahama yace: na shiga Masallacin damashk sai ga wani saurayi akan wata kujera ta alfarma ga kuma mutane kewaye dashi, idan suka samu sabani cikin wani abu sais u koma zuwa gareshi suna neman ra'ayin sa, sai nayi tambaya gaMai dashi sai akacemun ai Mu'azu Xan Jabal ne, da washe gari yayi sai

Muslim ne ya rawaito shi (2567) [260]
Tirmizi ne ya rawaito shi (2390) [261]

nayi sammako koda na iso Masallacin sai na saMai shin ya rigani zuwa, na saMaishi yana Sallah sai na jirashi har y agama daganan na karasa zuwa gareshi nayi masa Sallama sai nace mashi: wallahi ni inason ka domin Allah! Sai yace: da gaske? Sai yace masa: eh dagaske. Sai yace: da gaske kakeyi? Sai nace mas: eh, sai ya kama gefen mayafi nay a jawo ni kusa dashi yace ina maka bishara cewa lallai naji daga manzon Allah s.a.w yana cewa:

وَجَبَتْ مَحَبَّتِي لِلْمُتَحَابِّينَ فِيَّ، وَالْمُتَجَالِسِينَ فِيَّ، وَالْمُتَزَاوِرِينَ فِيَّ، وَالْمُتَبَاذِلِينَ فِيَّ.

Ma'ana: " Allah Maxaukaki yace: ya wajabta soyayyata ga masu soyayya domin ni da masu zama domin ni da masu ziyara domin ni da masu ciyar wa domin ni".[262]

## 15. Ayyukan taimakon al'umma:

### a) Daukan nauyin marayu:

Maraya shine wanda ya rasa daya daga cikin mahaifan sa ko su biyun duka kafin ya balaga, marayan da yake cikin wannan halin yanada matukar butane na tausaya masa da jin kai da rahama a wani lokuta ma yana neman taimako na Abunci da kudi. Domin manzon rahama ya zaburar da mutane akan renon maraya da kula dasu sai ya fadi cikin Hadisn da aka rawaito daga Sahal Xan sa'ad Allah ya kara masa yarda daga manzon Allah s.a.w yace:

« أَنَا وَكَافِلُ الْيَتِيمِ لَهُ أَوْ لِغَيْرِهِ فِي الْجَنَّةِ كَهَاتَيْنِ إِذَا اتَّقَى ». وَأَشَارَ بِإِصْبُعَيْهِ الْوُسْطَى وَالَّتِي تَلِي الإِبْهَامَ.

---

Malik ne ya rawaito shi cikin muwadda (1711) [262]

Ma’ana: " ni da wanda yake renon maraya Kaman haka muke cikin aljanna sai ya nuna yatsunsa na tsakiya da manuni ya hada tsakanin su"[263].

Da wannan falalar ne Mai girma maraya yake samun masu daukan nauyin sa cikin al'umma da renon sa,shi kuma wanda ya dauki nauyin sa ya samu matsayin makwabtaka da manzon Allah s.a.w cikin aljanna. Ibn Abdal yace: (wajibi ne akan wanda yaji wannan Hadis dayayi aiki dashi domin ya zama aboki ga manzon Allah s.a.w cikin aljanna wacce babu wani wuri cikin aljanna dayafi wannan falala)[264].

Daga cikin zaburarwa har wayau akan tausayawa marayu faxin manzon Allah s.a.w:

"مَنْ مَسَحَ رَأْسَ يَتِيمٍ كَانَ لَهُ بِكُلِّ شَعْرَةٍ حَسَنَةٌ"

Ma’ana: " Duk wanda ya shafi kan maraya yana da lada na ko wani silin gashin kansa ya hannun say a taba"[265].

Ya Allah kasanya mu cikin masu tausayin marayun mu da daukan nauyin da kulawar ka da kyautatawar ka.

## b) Taimaka mata gajiyayyu marasa miji da miskinai:

An karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

"السَّاعِي عَلَى الْأَرْمَلَةِ وَالْمِسْكِينِ، كَالْمُجَاهِدِ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ"

Ma’ana: " Mai taimakon mata gajiyayyu marasa miji da miskinai kamar Mai jihadi ne domin daukaka addinin Allah,

---

[263] Buhari da abu dawud da tirmizi ne suka rawaito shi

[264] Ibn hajar ya ambace shi cikin fathul bari a karkashin sharhin Hadisn

[265] Littafin garib na abu nu'aim fi hilyatul auliya'u, mujalladi na 8, shafi na 191

ina tsammanin kamar yace: Kaman Mai tsayuwan dare ne wanda baya hutawa da Mai Azumin da baya shan ruwa"[266].

## 16. Tausayawa dabbobi:

An karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

بَيْنَمَا رَجُلٌ يَمْشِي بِطَرِيقٍ اشْتَدَّ عَلَيْهِ الْعَطَشُ ، فَوَجَدَ بِئْرًا فَنَزَلَ فِيهَا ، فَشَرِبَ ثُمَّ خَرَجَ فَإِذَا كَلْبٌ يَلْهَثُ يَأْكُلُ الثَّرَى مِنَ الْعَطَشِ ، فَقَالَ الرَّجُلُ : لَقَدْ بَلَغَ هَذَا الْكَلْبَ مِنَ الْعَطَشِ مِثْلُ الَّذِي كَانَ بَلَغَنِي ، فَنَزَلَ الْبِئْرَ فَمَلأَ خُفَّهُ ، ثُمَّ أَمْسَكَهُ بِفِيهِ حَتَّى ارتَقَى فَسَقَى الْكَلْبَ فَشَكَرَ ٱللَّهُ لَهُ فَغَفَرَ لَهُ ، فَقَالُوا : يَا رَسُولَ ٱللَّهِ ، وَإِنَّ لَنَا فِي الْبَهَائِمِ لأَجْرًا ؟ فَقَالَ : فِي كُلِّ ذَاتِ كَبِدٍ رَطْبَةٍ أَجْرٌ

Ma’ana: " a lokacin da wani Mutum kishi ya daMai shi sai ya samu wata rijiya ya jawo ruwa yasha daga cikinta, sai ga wani kare nan yana cin kasa saboda tsananin kishin ruwa, sai yace Haqiqa wannan Karen kishi yakai mai makura kamar yadda yakaimun sai ya koma wnnan rijiya ya jawo ruwa da takalmin sa yaba wannan kare sai Allah ya gode masa ya kuma gafarta masa, sai sukace ya manzon Allah yanzu za'a rika bamu lada akan dabbobin mu, sai yace kuna da lada akan dukkanin wata hanta Xanya Mai rai"[267] .

Yakai irin wannan girma na wannan shari'a wanda take kula da himmatuwa akan dabbobi, daga cikin haka akwai Abunda aka anbata cikin Hadis daga Abdullahu daga baban sa yace:

---

Malaman Hadis shida sun rawaito shi banda abu dawud [266]

Buhari ne ya rawaito shi (6009) [267]

« كُنَّا مع رسولِ ٱللَّهَ –صلى ٱللَّهَ عليه وسلم– في سَفَرٍ ، فانطلقَ لحَاجَتِه، فَرَأَينا حُمَّرَة معها فَرخَانِ ، فَأَخَذْنَا فَرخَيها ، فَجَاءت الحُمَّرَةُ ، فجعَلت تُعَرِّشُ ، فَلمَا جاءَ رسولُ ٱللَّهَ –صلى ٱللَّهَ عليه وسلم– قال : مَنْ فَجَعَ هذه بِوَلَدِهَا ؟ رُدُّوا ولدَهَا إِليها، ورأى قَريَةَ نَمْلٍ قَدْ أحْرَقناها ، فقال: مَن أَحرَقَ هذه؟ قُلنا : نحن، قال: إِنَّهُ لا ينبغي أَنْ يُعَذِّبَ بعذاب النارِ إِلا رَبُّ النَّار»

Ma'ana: " mun kasance tare da manzon Allah s.a.w cikin tafiya sai muka tafi masa wani saka sai muka ga wata tsuntsu tare da Xanta sai muka dauko Xan sai wannan tsuntsuwar tazo tanata kuka tana neman yaronta, da muka dawo wurin manzon Allah s.a.w sai yace: wanene ya raba wannan yaron da uwarshi? Ku mayar mata da yaronta akan hanyar mu sai mukaga gidan tururuwa sai muka kona, sai yace: wanene ya kona wannan? Sai mukace mune, sai yace: baya halatta yin azaba da wuta sai ga ubangijin wutan"[268].

Kuma an umjurce mu da kada mu azabtar da dabba a lokacin yankata, manzon Allah s.a.w yace:

"إِنَّ ٱللَّهَ عَزَّ وَجَلَّ كَتَبَ الإِحْسَانَ عَلَى كُلِّ شَيْءٍ، فَإِذَا قَتَلْتُمْ فَأَحْسِنُوا الْقِتْلَةَ، وَإِذَا ذَبَحْتُمْ فَأَحْسِنُوا الذَّبْحَ، وَلْيُحِدَّ أَحَدُكُمْ شَفْرَتَهُ، وَلْيُرِحْ ذَبِيحَتَهُ"

Ma'ana: "lallai Allah ya rubuta kyautatawa akan komai idan zakuyi kisa ku kyautata kisan kuma idan zakuyi yanka ku kyautata yankan dayan ku ya wasa wukan yankan sa domin ya saukakawa dabbar sa"[269].

---

Abu dawud da ahmad ne suka rawaito shi [268]
Malaman Hadis shida sun rawaito shi sai buhari kawai [269]

## 17. Jihadi da shirin jihadi domin Allah:

An karvo daga sahal Xan sa'ad Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

مَنْ رَابَطَ يَوْمًا وَلَيْلَةً فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ كَانَ لَهُ أَجْرُ صِيَامِ شَهْرٍ وَقِيَامِهِ ، وَمَنْ مَاتَ مُرَابِطًا أَجْرَى لَهُ مِثْلَ الأَجْرِ ، وَأَجْرَى عَلَيْهِ الرِّزْقَ ، وَأَمِنَ الْفَتَّانَ

Ma’ana: " dakon yaki na wuni daya a rana domin Allah yafi Duniya da abun da ke cikinta alheri, kuma wurin da aka duki dayanku a wurin a cikin aljanna yafi Duniya da abun dake cikin alheri"[270].

An karvo kuma daga salmunul farisi Allah ya kara masa yarda yace: naji manzon Allah s.a.w yana cewa:

"لَغَدْوَةٌ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ أَوْ رَوْحَةٌ خَيْرٌ مِنَ الدُّنْيَا وَمَا فِيهَا، وَمَوْضِعُ سَوْطِ أَحَدِكُمْ مِنَ الْجَنَّةِ خَيْرٌ مِنَ الدُّنْيَا وَمَا فِيهَا"

Ma’ana: " dakon yaki cikin dare da rana yafi Azumin wata daya da tsayuwar dare a cikin sa alheri idan kuma yam utu za'aci gaba da bashi Ladan aikin da ya kasance yana aikatawa kuma za'a ci gaba da gudanar masa da arzkin sa kuma za'a tsareshi daga fitinar Karvari"[271],

an karvo kuma daga abu umamata albahili Allah ya kara masa yarda daga manzon Allah s.a.w yace:

"أَرْبَعَةٌ تَجْرِي عَلَيْهِمْ أُجُورُهُمْ بَعْدَ الْمَوْتِ: مَنْ مَاتَ مُرَابِطًا فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ، وَمَنْ عَلِمَ عِلْمًا أُجْرِيَ لَهُ أَجْرُهُ مَا عَمِلَ بِهِ، وَمَنْ تَصَدَّقَ بِصَدَقَةٍ فَأَجْرُهَا يَجْرِي لَهُ مَا جَرَتْ، وَرَجُلٌ تَرَكَ وَلَدًا صَالِحًا، فَهُوَ يَدْعُو لَهُ"

[270] Buhari da tirmizi ne suka rawaito shi

[271] Muslim da nasa'I ne suka rawaito shi

Ma’ana: " Mutum hudu Ladan su zai ci gaba har bayan mutuwar su, Mutumin daya mutu yana yana dakon yaki domin daukaka addinin Allah, da Mutumin daya koyar da wani ilimi Ladan sa zaici gaba da gudana akan ilimin sa da akayi aiki dashi, da Mutumin daya gudanar da wata sadaka za'a ci gaba da gudanar masa dashi matukar tananan, da Mutumin daya bar yaro nagari yana masa addu'a"[272].

An karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

« لاَ يَجْتَمِعُ غُبَارٌ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ وَدُخَانُ جَهَنَّمَ »

Ma’ana: " kuran yaki domin daukaka addinin Allah bazai taba haduwa ba da hayakin wutan jahannama"[273].

Jihadi yana kare sharrin makiya da kuma kare raunin su kuma yana yada da'awar muslunci ga Duniya baki daya kuma hasken musulunci ya shiga ko ina cikin faxin Duniya, da jihadi ne da kuma jarabawa Allah yake fayyace Mai datti daga Mai tsabta, Allah Maxaukaki yace:

﴿ أَمْ حَسِبْتُمْ أَن تَدْخُلُوا۟ ٱلْجَنَّةَ وَلَمَّا يَعْلَمِ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ جَـٰهَدُوا۟ مِنكُمْ وَيَعْلَمَ ٱلصَّـٰبِرِينَ ﴾

Ma’ana: " kuna tsammanin zaku shiga aljanna ne tun gabanin a jarabe ku da yaki Allah yaga wanda sukayi jihadi acikin ku domin daukaka addinin Allah da masu hakuri cikin ku na haduwa da makiya"[274].

Shahidai suna da matsayi Mai girma a wurin Allah zasu kasance rayayyu agunsa yana azurta su, Allah Maxaukaki yace:

---

[272] Ahmad ne ya rawaito shi (22702)
[273] Tirmizo ne ya rawaito shi (1633)
[274] Suratu al'imran

﴿ وَلَا تَحۡسَبَنَّ ٱلَّذِينَ قُتِلُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ أَمۡوَٰتَۢاۚ بَلۡ أَحۡيَآءٌ عِندَ رَبِّهِمۡ يُرۡزَقُونَ ١٦٩ ﴾

Ma'ana: " kada kuyi tsammanin wanda aka kashesu a wurin daukaka addinin Allah matattu ne, sun kasance rayayyu a wurin ubangijin su yana azurta su"[275].

Manzon Allah s.a.w ya bayyana Abunda aka tanadarma shahidai na karamci cikin faxin cewa:

« مَا أَحَدٌ يَدْخُلُ الْجَنَّةَ فَيَتَمَنَّى أَنْ يَخْرُجَ مِنْهَا وَإِنْ لَهُ مَا عَلَى الأَرْضِ مِنْ شَيْءٍ إِلاَّ الشَّهِيدَ فَإِنَّهُ يَتَمَنَّى أَنْ يَرْجِعَ فَيُقْتَلَ عَشْرَ مِرَارٍ لِمَا رَأَى مِنَ الْكَرَامَةِ »

Ma'ana: " babu Mutumin da zai shiga aljanna kuma yana neman ya dawo Duniya kuma bashi da komai a Duniyan sai shahidi kaxai, zaiyi burin dawowa Duniya a kashe shi a wurin yaki sau goma saboda Abunda ya gani na karamci"[276].

Jihadi yana kasance ne ko dai da kudi ko kuma da rai ko kuma dasu biyun duka, kuma wannan shine mafi falalar jihadi. Jihadi da kudi an gaVatar da ambaton sa akan jihadi da rai, saboda Abunda ke cikinsa na sauki da kuma iya aikata hakan, ba kowa bane cikin mutane zai yake da ikon yin yaki da rai kodai saboda rashin lafiyar jiki ko kuma saboda rashin hanya zuwa ga kasar makiya sabani jihadi da dukiya koda yana iyawa musamman kuma cikin wannan zamani da aka jarAbu musulmai da yawan makiya, Allah Maxaukaki yace:

---

[275] Suratu al'imran

[276] Burari da muslim ne suka frawaito shi

لَّا يَسْتَوِى ٱلْقَٰعِدُونَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ غَيْرُ أُو۟لِى ٱلضَّرَرِ وَٱلْمُجَٰهِدُونَ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ ۚ فَضَّلَ ٱللَّهُ ٱلْمُجَٰهِدِينَ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ عَلَى ٱلْقَٰعِدِينَ دَرَجَةً ۚ وَكُلًّا وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلْحُسْنَىٰ ۚ وَفَضَّلَ ٱللَّهُ ٱلْمُجَٰهِدِينَ عَلَى ٱلْقَٰعِدِينَ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿٩٥﴾ دَرَجَٰتٍ مِّنْهُ وَمَغْفِرَةً وَرَحْمَةً ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿٩٦﴾

Ma'ana: " wanda suke zaune a gida cikin mumunai wanda basu da wani lalura bazasu taba zama daya ba da wanda suka fita jihadi domin daukaka addinin Allah da dukiyar su da rayukan su, Allah ya daukaka mujahidai da dukiyoyin su da rayukan su akan wanda suke zaune a gida a daraja, dukkanin su Allah yayi masu alkawarin sakamako Mai kyau, kuma Allah ya daukaka mujahidai akan wanda suka zauna a gida da lada Mai girma (95) daraja daga gareshi da gafara da rahama, Allah kuma ya kasance Mai gafara ne Mai rahama (96)"[277].

Allah nake rook daya taimaki yan uwan mu mujahidai a ko wani wuri ya kuma tabVatar da musulunci da mutanen shi, amin.

Jihadi yana cikin kasuwanci Mai riba wanda Allah ya fada cikin littafin sa da cewa:

﴿ ۞ إِنَّ ٱللَّهَ ٱشْتَرَىٰ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ أَنفُسَهُمْ وَأَمْوَٰلَهُم بِأَنَّ لَهُمُ ٱلْجَنَّةَ ۚ يُقَٰتِلُونَ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ فَيَقْتُلُونَ وَيُقْتَلُونَ ۖ وَعْدًا عَلَيْهِ حَقًّا فِى ٱلتَّوْرَىٰةِ وَٱلْإِنجِيلِ وَٱلْقُرْءَانِ ۚ وَمَنْ أَوْفَىٰ بِعَهْدِهِۦ مِنَ ٱللَّهِ ۚ فَٱسْتَبْشِرُوا۟ بِبَيْعِكُمُ ٱلَّذِى بَايَعْتُم بِهِۦ ۚ وَذَٰلِكَ هُوَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿١١١﴾ ﴾

Ma'ana: " lallai Allah ya siya rayuka da dukiyoyin muminai daga wurin su da cewa suna da aljanna, suna yaki domin

277 Suratun nisa'I

daukaka addinin Allah akashe su suma su kashe, alkawari ne akan san a gaskiya cikin attaura da injila da Al-qur’ani, kuma wanene yafi Allah cika alkawari, kuyi murna da kasuwancin ku wanda aka siya daga gareku, kuma wannan shine rabo Mai girma"[278],

da kuma faxin sa Maxaukaki:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ هَلۡ أَدُلُّكُمۡ عَلَىٰ تِجَٰرَةٖ تُنجِيكُم مِّنۡ عَذَابٍ أَلِيمٖ ١٠ تُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَتُجَٰهِدُونَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ بِأَمۡوَٰلِكُمۡ وَأَنفُسِكُمۡۚ ذَٰلِكُمۡ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ١١ ﴾

Ma’ana: " yaku wanda sukayi imani bazan nuna maku wani kasuwanci ba wanda zai tsiratar daku daga azaba Mai radadi (10) kuyi imani da Allah da manzon sa kuma kuyi jihadi domin daukaka addinin Allah da dukiyoyin ku da rayukan ku, wannan shi yafi zama alheri a gareku da kun kasance kuna sani"[279]. Jihadi sabAbu ne na shiriyan Allah ga bawansa, Allah Maxaukaki yace:

﴿ وَٱلَّذِينَ جَٰهَدُواْ فِينَا لَنَهۡدِيَنَّهُمۡ سُبُلَنَاۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ لَمَعَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٦٩ ﴾

Ma’ana: " wanda sukayi jihadi saboda mu da sannu zamu shiryar dasu hanyoyin mu, kuma lallai Allah yana tare da masu kyautatawa (69)"[280],

jihadi yafi Duniya alheri da Abunda ke cikinta, manzon Allah s.a.w yace:

الغدو والرواح في سبيل ٱللَّهَ للمجاهد يكون خيرا من أن تكون له الدنيا وما فيها

[278] Suratul tauba
[279] Suratul saffi
[280] Suratul ankabut

Ma’ana: " sammako ko kuma yammaci na zuwa jihadi domin daukaka addinin Allah yafi Duniya alheri da Abunda ke cikinta"[281].

## 18. Siffifi na Qwarai wanda musulmi ya kamata ya siffatu dasu:

**GaVatarwa akan kyakyawan mu'amala:**

An karvo Hadis daga abuddar da'i Allah yakara masa yarda daga manzon Allah s.a.w yace:

(( مَا مِنْ شَيْءٍ أَثْقَلُ في مِيزَانِ العبدِ المُؤْمِنِ يَوْمَ القِيَامَةِ مِنْ حُسْنِ الخُلُقِ ، وَإِنَّ ٱللَّهَ يُبْغِضُ الفَاحِشَ البَذِيَّ ))

Ma’ana: " babu wani Abunda yake da nauyi akan sikelin mumini ranan Al-qiyama kamar kyawawun mu'amala, kuma lallai Allah bayason tantire Mai aikata alfasha"[282],

kuma manzon Allah s.a.w ya kasance yana cewa:

« إِنَّ مِنْ خِيَارِكُمْ أَحْسَنَكُمْ أَخْلاَقًا »

Ma’ana: " lallai daga cikin zababben cikin ku shine wanda yafi ku kyawawan mu'amala"[283],

kyawawan mu'amala suna daga cikin sabAbun shiga aljanna an karvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: an tambayi manzon Allah s.a.w aikin da yafi shigar da mutane aljanna, sai yace:

---

[281] Buhari da muslim ne suka rawaito shi
[282] Tirmizi da abu dawud ne suka rawaito shi
[283] Buhari da muslim ne suka rawaito shi

تَقْوَى ٱللَّهَ وَحُسْنِ الْخُلُقِ

Ma’ana: " tsoron Allah da kyawawan mu'amala"[284],

An karvo daga Aisha Allah ya kara mata yarda tace naji manzon Allah s.a.w yana cewa:

إِنَّ الْمُؤْمِنَ لَيُدْرِكُ بِحُسْنِ خُلُقِهِ دَرَجَةَ قَائِمِ اللَّيْلِ وَصَائِمِ النَّهَارِ

Ma’ana: " lallai mumini yana samun daraja da kyawawan halayen sa na Mutum Mai tsayuwan dare da yawan Azumi"[285]. Mai kyawawan ayyuka zai kasance mafi kusa da manzon Allah cikin mutane ranar Al-qiyama, an karvo Hadis daga JAbur Allah ya kara masa yarda manzon Allah s.a.w yace:

(( إنَّ مِنْ أَحَبِّكُمْ إِلَيَّ ، وأَقْرَبِكُمْ مِنِّي مَجْلِساً يومَ القِيامَةِ ، أَحاسِنكُمْ أَخْلاَقاً ))

Ma’ana: " lallai daga cikin wanda nafi so kuma yafi kusanci Xani na wurin zama a cikin ku ranan Al-qiyama shine wanda yafi ku kyawawan mu'amala"[286].

Allah kuma ya yAbu manzon sa s.a.w cikin faxin sa cewa:

﴿ وَإِنَّكَ لَعَلَىٰ خُلُقٍ عَظِيمٍ ۝٤ ﴾

Ma’ana: " lallai ka kasance akan kyawawan dAbu'u masu girma"[287].

Haka kuwa saboda ya kasance kamar yadda Aisha tace lokacin da aka tambaye ta gaMai dAbu'un sa sai tace: "

---

[284] Tirmizi da ibn majjah ne suka frawaito shi
[285] Abu dawud ne ya rawaito shi (4798)
[286] Tirmizi ne ya rawaito shi (2018)
[287] Suratul kalam

dAbu'un sa shine Al-qur'ani"[288]. An karvo Hadis daga Abdullah Xan mas'ud Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace gaMai da kansa:

أدبنى ربى فأحسن تأديبى

Ma'ana: "Ubangiji naya ladabtar Xani sai ya kyautata halayena"[289].

Kayi koyi yakai Xan uwana da yar uwata da halayen shugaban manzanni domin kasamu tsira Duniya da lahira.

Mawaki Mai suna Ahmad al shauki yace yana Mai bayanin anfanin kyawawan mu'amala ga al'umma:

Lallai kyawawan mu'amala shine daurewan al'umma

Idan kyawawan mu'amula suka kau suma zasu kau.

**Ga wasu daga cikin kyawawan mu'amula wanda akeson musumi ya siffatu dasu:**

## 1) Hakuri:

Hakuri kyakyawan hali ne Mai griMai, kuma koyi ne ga bayin Allah salihai kamar yadda Allah Maxaukaki ya fadi yana Mai hakaito labari akan annAbun sa yakubu lokacin da yaransa sukayi ikirarin karkeci ya cinye yusuf:

﴿ فَصَبۡرٞ جَمِيلٞۖ وَٱللَّهُ ٱلۡمُسۡتَعَانُ عَلَىٰ مَا تَصِفُونَ ١٨ ﴾

Ma'ana: " zanyi hakuri Maikyau akan wannan al'amari, kuma Allah shine mataimaki akan wannan Abunda kuka wasafta (18)"[290].

---

Buhari da nasa'I ne suka rawaito shi [288]

Albani ya raunata Hadisn cikin littan aljami'u (249) amma ma'anar Hadis ingantacce ne [289]

Suratu yusuf [290]

Haka kuma faxin sa bayan yaransa sun dawo daga misira ba tare da Xan uwan su ba karami:

﴿فَصَبْرٌ جَمِيلٌ عَسَى ٱللَّهُ أَن يَأْتِيَنِي بِهِمْ جَمِيعًا إِنَّهُ هُوَ ٱلْعَلِيمُ ٱلْحَكِيمُ ﴿٨٣﴾﴾

Ma'ana: " zanyi hakuri Mai kyau, ina fatan Allah zai zomun dasu baki dayan su, lallai shi masani ne kuma Mai hikima"[291]. Kuma hakuri na daga cikin sunnar shugaban mu Muhammad s.a.w da sahabban sa Allah ya kara yarda agaresu yadda sukayi hakuri akan cucarwan kuraishawa da sukayi masu kamar yadda ubangijinya wasaftasu dashi cikin littafin sa:

﴿وَٱلصَّٰبِرِينَ فِي ٱلْبَأْسَآءِ وَٱلضَّرَّآءِ وَحِينَ ٱلْبَأْسِ أُولَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ صَدَقُوا وَأُولَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُتَّقُونَ﴾

Ma'ana: " da masu hakuri a halin talauci da rashin lafiya da annuba da kuma hakuri a lokacin yaki da zalumcin makiya, wannan sune wanda suka gasgata kuma sune masu takawa (177)"[292]. Kuma masu ruko da faxin manzon Allah s.a.w cikin faxin sa:

« عَجَبًا لأَمْرِ الْمُؤْمِنِ إِنَّ أَمْرَهُ كُلَّهُ خَيْرٌ وَلَيْسَ ذَاكَ لأَحَدٍ إِلاَّ لِلْمُؤْمِنِ إِنْ أَصَابَتْهُ سَرَّاءُ شَكَرَ فَكَانَ خَيْرًا لَهُ وَإِنْ أَصَابَتْهُ ضَرَّاءُ صَبَرَ فَكَانَ خَيْرًا لَهُ »

Ma'ana: " akwai mamaki cikin al'amarin mumini saboda al'amarun sa dukkanin shi alheri ne idan wani alheri ya saMaishi sai ya godema Allah haka sai hakan ya kasance alheri a gareshi idan kuma wani sharri ya saMaishi sai yayi hakuri sai hakan ya zama alheri a gareshi"[293]. An karvo daga ubayyu Allah ya kara masa yarda yace: manzon allah s.a.w yace:

---

Suratu yusuf [291]
Suratul bakara [292]
Muslim ne ya rawaito shi (2999) [293]

« مَا يُصِيبُ الْمُسْلِمَ مِنْ نَصَبٍ وَلاَ وَصَبٍ وَلاَ هَمٍّ وَلاَ حُزْنٍ وَلاَ أَذًى وَلاَ غَمٍّ حَتَّى الشَّوْكَةِ يُشَاكُهَا ، إِلاَّ كَفَّرَ ٱللَّهُ بِهَا مِنْ خَطَايَاهُ »

Ma'ana: "wata musiba bazata samu musulmi ba ko kuma damuwa ko bakin ciki ko wata cutarwa ba hatta kaya face an kankare masa zunuban sa da hakan"[294].

**Hakuri iri uku ne:**

1- Hakuri akan biyayyar Allah, Allah Maxaukaki yace:

﴿إِنَّمَا يُوَفَّى ٱلصَّٰبِرُونَ أَجْرَهُم بِغَيْرِ حِسَابٍ ۝١٠﴾

Ma'ana: " lallai yana cikama masu hakuru Ladan sub a tare da Hisabi ba"[295].

2- Haquri akan Abunda Allah ya haramta, manzon Allah s.a.w yace:

من ترك شيئا لله أبدله ٱللَّهُ خيرا منه

Ma'ana: " Duk wanda yabar wani abu domin Allah zai canza masa da mafiyin sa alheri"

**3-** Hakuri akan kaddarar Allah, Allah Maxaukaki yace:

﴿ٱلَّذِينَ إِذَآ أَصَٰبَتۡهُم مُّصِيبَةٞ قَالُوٓاْ إِنَّا لِلَّهِ وَإِنَّآ إِلَيۡهِ رَٰجِعُونَ ۝١٥٦ أُوْلَٰٓئِكَ عَلَيۡهِمۡ صَلَوَٰتٞ مِّن رَّبِّهِمۡ وَرَحۡمَةٞۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُهۡتَدُونَ ۝١٥٧﴾

Ma'ana: " sune wanda idan musifa ta shafesu sai suce lallai ga Allah muke kuma gareshi zamu koma (156) wa'innan

---

[294] Buhari da muslim ne suka rawaito shi

[295] Suratul zumar

suna da yabo agun ubangijin su da rahama kuma wa'innan sune shiryayyu (157)"[296].

## 2) Barin jayayya da musu:

An karvo Hadis daga abu umamata Allah ya kara masa yace: manzon Allah s.a.w yace:

"أَنَا زَعِيمُ بِبَيْتٍ فِي رَبَضِ الْجَنَّةِ، وَبَيْتٍ فِي وَسَطِ الْجَنَّةِ، وَبَيْتٍ فِي أَعْلَى الْجَنَّةِ لِمَنْ تَرَكَ الْمِرَاءَ وَإِنْ كَانَ مُحِقًّا، وَتَرَكَ الْكَذِبَ وَإِنْ كَانَ مَازِحًا، وَحَسُنَ خُلُقُهُ"

Ma'ana: " la lamunce wani gadi a gefen aljanna ga duk Mutumin da yabar musu koda kuwa shine Mai gaskiya da kuma gida a tsakiyar aljanna da Mutumin daya bar karya koda kuwa wasa yakeyi da kuma gida a kololuwan aljanna ga wanda ya kyautata halayen sa"[297].

Saboda haka ne Allah Maxaukaki ya umurci manzon sa s.a.w dajin mujadala ga Abunda yafi kyau cikin faxin sa cewa:

Ma'ana: " kuma kayi mujadala dasu da abaun da yafi kyau"[298],

wannan cikin mujadala ne ga ma'abota litta, da kuma faxin sa ga Musa da Xan uwan sa Harun amincin Allah ya kara tabVata a garesu lokacin daya umurce su da yima fir'auna da'awa:

﴿ فَقُولَا لَهُۥ قَوۡلٗا لَّيِّنٗا لَّعَلَّهُۥ يَتَذَكَّرُ أَوۡ يَخۡشَىٰ ٤٤ ﴾

[296] Suratul bakara
[297] Abu dawud ne ya rawaito shi
[298] Suratun nahli

Ma'ana: " ku faxa masa Magana masu daxi koda zayyi tunani yaji tsoron Allah (44)"[299].

## 3) Hakuri da juriya:

Ibn Abbas yace Allah ya kara masu yarda: manzon Allah s.a.w yace am ashajju Xan abdulkais

إِنَّ فِيكَ خَصْلَتَيْنِ يُحِبُّهُمَا ٱللَّهُ وَرَسُولُهُ : الْحِلْمُ ، وَالأَنَاةُ

Ma'ana: " lallai kana da wasu halaye guda biyu Allah da manzon sa yana son su sai yace: ya manzon Allah Mainene su? Sai yace: hakuri da juriya"[300].

## 4) Cika alkawari:

﴿وَأَوْفُوا۟ بِٱلْعَهْدِ ۖ إِنَّ ٱلْعَهْدَ كَانَ مَسْـُٔولًا ﴿٣٤﴾﴾

Allah Maxaukaki yace: " ku cika alkawari, lallai alkawari ya kasance abun tambaya akai ne"[301].

Kuma yana daga cikin siffofin mumunai wanda suka rabauta cikin faxin sa Maxaukaki:

﴿قَدْ أَفْلَحَ ٱلْمُؤْمِنُونَ ﴿١﴾﴾

Ma'ana: " Haqiqa mumunai sun rabauta"[302]

sun kasance kuma:

---

[299] Suratu daha
[300] Muslim ne ya rawaito shi (2011)
[301] Suratul isra'I
[302] Suratul muminun

﴿ وَٱلَّذِينَ هُمۡ لِأَمَٰنَٰتِهِمۡ وَعَهۡدِهِمۡ رَٰعُونَ ٨ ﴾

Ma'ana: " sune wanda suke kiyaye amanarsu da alkawuran su"[303].

Kuma Allah Maxaukaki ya kara fadi har wayau:

﴿ وَٱلۡمُوفُونَ بِعَهۡدِهِمۡ إِذَا عَٰهَدُواْۖ ﴾

Ma'ana: " da masu cika alkawuran sui Xan sun dau alkawari"[304]

karshen su sai yazama sune

﴿ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ صَدَقُواْۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُتَّقُونَ ١٧٧ ﴾

Ma'ana: " wannan sune wanda suka gasgatakuma wannan sune masu takawa (177)[305].

Saboda girman alkawari da wajabcin cikashi ne ya sa Allah ya cire mushrikai wanda akayi alkawarin zaman lafiya dasu na tsawon wata hudun da aka basu a Masallacin ka'aba cikin faxin sa cewa:

﴿ فَسِيحُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ أَرۡبَعَةَ أَشۡهُرٖ ٢ ﴾

Ma'ana: " kuyi tafiya cikin kasa watanni hudu"[306]

zuwa karshen faxin sa Maxaukaki:

﴿ إِلَّا ٱلَّذِينَ عَٰهَدتُّم مِّنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ثُمَّ لَمۡ يَنقُصُوكُمۡ شَيۡـٔٗا وَلَمۡ يُظَٰهِرُواْ عَلَيۡكُمۡ أَحَدٗا
فَأَتِمُّوٓاْ إِلَيۡهِمۡ عَهۡدَهُمۡ إِلَىٰ مُدَّتِهِمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُتَّقِينَ ٤ ﴾

---

Suratul muminun [303]
Suratul bakara ayata 177 [304]
Suratul bakara [305]
Suratul tauba ayata 2[306]

Ma’ana: " sai dai wanda kukayi alkawari dasu cikin mushrikai sa'annan kuma basu tauye maku komai ba kuma basu taimaki wani ba akanku to ku cika masu alkawarin su zuwa lokacin da kuka dauka masu"[307]. Alkawarin Allah wajibi ne a cika shi, Allah Maxaukaki yace:

﴿ وَأَوۡفُواْ بِعَهۡدِ ٱللَّهِ إِذَا عَٰهَدتُّمۡ وَلَا تَنقُضُواْ ٱلۡأَيۡمَٰنَ بَعۡدَ تَوۡكِيدِهَا ﴾ ٩١

Ma’ana: " ku cika alkawarin Allah idan kun dauka kuma kada ku warware rantsuwa bayan ta tabbatu".[308]

## 5) Gaskiya:

An karvo Hadis daga ibn mas'ud Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

« إِنَّ الصِّدْقَ يَهْدي إِلي البِرِّ ، وإِن البِرَّ يهدي إِلى الجنةِ ، وإِن الرَّجُلَ لَيَصْدُقُ حتى يُكتَبَ عند ٱللَّهِ صِدِّيقًا »

Ma’ana: " lallai Gaskiya tana shiryarwa zuwa ga aikin alheri kuma aikin alheri yana shiryar wa zuwa ga aljanna, Mutum bazai gushe ba yana gaskiya kuma yana neman ta face an rubutashi Mai gaskiya a wurin Allah"[309].

Daga cikin anfanin gaskiya shine tana tsiratar da bawa a Duniya da lahira, anan Duniya kamar yadda ya faru cikin labarin wanda suka gudun ma yakin tabuka, a lahira kuma kamar yadda Allah Maxaukaki ya hakaito akan makomar shugaban mu isa s.a.w ranar Al-qiyama cikin faxin sa cewa:

---

[307] Suratul tauba ayata 4

[308] Suratun nahli ayata 91

[309] Muslim da tirmizi da abu dawud ne suka rawaito shi

﴿ قَالَ ٱللَّهُ هَٰذَا يَوۡمُ يَنفَعُ ٱلصَّٰدِقِينَ صِدۡقُهُمۡۚ لَهُمۡ جَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۖ رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنۡهُمۡ وَرَضُواْ عَنۡهُۚ ذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ١١٩ ﴾

Ma'ana: " Allah yace wannan rana ce wanda gaskiya zata yi anfani ga mai gaskiya, sunada aljanna wacce koramu take gudana a karkashinta suna masu dawwama acikinta har AbaXan, Allah ya yarda dasu kuma suma sun yarda dashi, wannan shine rabo Mai girma (119)"[310].

Kuma har wayau gaskiya natsuwa ne ga zuciya, a cikin Hadisn alhasan Xan Aliyu Allah ya kara masu yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

فإِن الصِّدْق طُمأْنينة والكذب رِيبَة

Ma'ana: " lallai gaskiya kwanciyar hankali ce, karya kuma shakka ce"[311].

## 6) Kishi:

Manzon Allah s.a.w yace:

أَتَعْجَبُونَ مِنْ غَيْرَةِ سَعْدٍ؟ فَوَاللَّهِ لأَنَا أَغْيَرُ مِنْ سَعْدٍ،

Ma'ana: " yanzu kuna mamaki akan kishin sa'ad? Lallai nafi shi kishi ni kuma Allah ya fini kishi"[312].

An karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

[310] Suratul ma'ida
[311] Tirmizi da nasa'I da Ahmad ne suka rawaito shi
[312] Buhari ne ya rawaito shi (107)

«إنَّ ٱللَّهَ يَغارُ ، وَإِنَّ المؤمنَ يغار ، وَإِن غَيْرَةَ ٱللَّهَ : أن يَأتِيَ المؤمن ما حرَّم ٱللَّهَ عليه »

Ma'ana: " lallai Allah yana kishi kuma daga cikin kishin Allah shine mumini yaje aikata Abunda Allah ya haramta"[313].

Manzon Allah s.a.w ya kasance fuskar sa tana canzawa saboda fushi idan an taka hurimun Abunda Allah ya harumta, ya zama wajibi ga musulmu ya kasance yana da kishin gaMai gari ga Allah da manzon sa da addinin Allah da shari'ar sa da malaman al'umma, da kuma kishi akan yaran sa da matan sa da iyalan sa, da kuma kishi akan wureren masu daraja na musulmai kada makiyan Allah su lalata su.

Duk wanda yam utu babu kishi a zuciyar sa to wannan babu alheri a tare dashi kamar gangan jiki ne wanda jinsa ya mutu, kofaton rakumi bayajin komai koda kuwa an soka masa kaya ne.

## 7) Tausayi da biyayyar iyaye:

Anason Mutum ya zama Mai tausayi ga kowa hatta dabbobi, an karvo Hadis daga abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

دَخلَتِ امْرَأَةٌ النَّارَ فِي هِرَّةٍ رَبطَتْهَا ، فَلا هِيَ أَطْعَمَتْهَا وَلا هِيَ أَرْسَلَتْهَا تَأْكُلُ مِنْ خَشَاشِ الأَرْضِ

Ma'ana:" wata mata tashiga wuta akan wata mage wacce ta klleta Vata Vata Abunci kuma Vata saketa ba taje ta rori a

[313] Buhari da muslim ne suka rawaito shi

binci ba a waje"[314]. Wannan shine sakamakon wanda babu tausayi a ransa, Allah ya tsaremu!!!

An karvo Hadis da Usamata Xan zaid Allah ya kara masu yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:

" إِنَّمَا يَرْحَمُ ٱللَّهُ مِنْ عِبَادِهِ الرُّحَمَاءَ "

Ma'ana: " lallai Allah yana tausayin bayin sa ne kawai masu tausayi"[315].

Kuma Allah ya wasifta muminai da cewa suna da tausayin junansu cikin faxin sa cewa:

﴿ مُّحَمَّدٞ رَّسُولُ ٱللَّهِۚ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلۡكُفَّارِ رُحَمَآءُ بَيۡنَهُمۡۖ ذَٰلِكَ ﴾

Ma'ana: " Muhammad manzon Allah ne, wanda kuma sukayi imani tare dashi masu tsanani ne ga kafirai masu tausayi a tsakanin su"[316].

An karvo kuma daga Abdullahi Xan Amru Xan Aas Allah ya kara masu yarda yace: manzon Allah s.a.w yace cikin wasafta al'ummar musulmai:

لَيْسَ مِنَّا مَنْ لَمْ يَرْحَمْ صَغِيرَنَا، وَلَمْ يَعْرِفْ حَقَّ كَبِيرِنَا

Ma'ana: " baya tare damu wanda baya jin tausayin kananan mu kuma baya girmama manyan mu"[317].

Lallai Ladan tausayi Mai girma ne saboda faxin manzon Allah s.a.w: " lallai Allah yana ba masu tausayi Abunda baya ba mugaye ko kuma wanin su"[318]. Manzon

---

Buhari da muslim ne suka rawaito shi[314]
Buhari da muslim ne suka rawaito shi[315]
Suratul fathi ayata 29 [316]
Tirmizi ne ya rawaito shi (1920) [317]
Muslim ne ya rawaito shi (2595) [318]

Allah s.a.w ya kasance Mai zuciyar rahama ne Mai tausayi ga miskinai da mata marasa mazaje da kuma marayu baya hana Mai rook ko kuma mabukaci.

An karvo daga Abu Huraira cewa akra'a Xan hAbus yaga manzon Allah s.a.w yana sunbaci hasan, sai yace: ni inada yara goma bantaba sunVatan daya daga cikin suba, sai manzon Allah s.a.w yace:

Ma'ana: " Duk wanda baya tausayi baza'a tausaya masa ba"[319].

عَنْ أَبِى هُرَيْرَةَ أَنَّ الأَقْرَعَ بْنَ حَابِسٍ أَبْصَرَ النَّبِىَّ –صلى ٱللَّهُ عليه وسلم– يُقَبِّلُ الْحَسَنَ فَقَالَ إِنَّ لِى عَشَرَةً مِنَ الْوَلَدِ مَا قَبَّلْتُ وَاحِدًا مِنْهُمْ فَقَالَ رَسُولُ ٱللَّهِ –صلى ٱللَّهُ عليه وسلم– « إِنَّهُ مَنْ لاَ يَرْحَمْ لاَ يُرْحَمْ ».

An karvo kuma daga Aisha Allah ya kara mata yarda tace: wasu mutane daga kauye sun zo wurin manzon Allah s.a.wsai sukace: yanzu kuna sunVatan yaran ku? Sai yace masu: eh, sai sukace: mudai wallahi baya sunVatar su, sai manzon Allah s.a.w yace: " ina tsoron ace Allah ya cire tausayi ne a zukatan ku"[320]

Da kuma faxin sa s.a.w:

" مَنْ لا يَرْحَمُ النَّاسَ لَمْ يَرْحَمْهُ ٱللَّهُ "

---

[319] Buhari da muslim ne suka rawaito shi
[320] Buhari da muslim ne suka rawaito shi

Ma’ana: " Duk wanda baya tausayin mutane Allah baya tausaya masa"[321]

- **Biyayyar iyaye:**

Allah ya sanya rahama ta zama fidira cikin zukatan mu akan yaran mu saboda haka ne bazaka samu wasu nassoshi ba dayawa akan wannan. Amma zaka samu dayawa cikin nassoshi wanda suke kwaxaitar da biyyay ga iyaye da kuma tausaya masu musamman ma idan sun girma sunyi rauni suna kasancewa ne cikin wannan yanayi cikin bukatar tausayi da tausasa masu da Kankan masu dakai da kuma kula daga wurin yaran su, Allah Maxaukaki yace:

﴿ وَقَضَىٰ رَبُّكَ أَلَّا تَعْبُدُوٓاْ إِلَّآ إِيَّاهُ وَبِٱلْوَٰلِدَيْنِ إِحْسَٰنًا ۚ إِمَّا يَبْلُغَنَّ عِندَكَ ٱلْكِبَرَ
أَحَدُهُمَآ أَوْ كِلَاهُمَا فَلَا تَقُل لَّهُمَآ أُفٍّ وَلَا تَنْهَرْهُمَا وَقُل لَّهُمَا قَوْلًا كَرِيمًا ﴿٢٣﴾ وَٱخْفِضْ
لَهُمَا جَنَاحَ ٱلذُّلِّ مِنَ ٱلرَّحْمَةِ وَقُل رَّبِّ ٱرْحَمْهُمَا كَمَا رَبَّيَانِى صَغِيرًا ﴿٢٤﴾ ﴾

Ma’ana: "kuma ubangijin ka ya hukunta cewa kada ka bautawa kowa sai shi kaxai kuma iyaye a kyautata masu, idan daya daga cikin su ko kuma su biyun duka suka girma tare dakai kada kace masu tir ko kuma ka tsawatar masu ka rika fada masu magana Mai dadi da girmamawa (23) ka shinfida masu fuka fukan ka na ram aka kuma ce ya Allah kayi masu harama kamar yadda suka raine ni ina yaro (24)[322].

Ya kuma kara fadi:

Muslim ne ya rawaito shi (2319) [321]

Suratul isra'I [322]

﴿ وَوَصَّيْنَا ٱلْإِنسَٰنَ بِوَٰلِدَيْهِ حَمَلَتْهُ أُمُّهُۥ وَهْنًا عَلَىٰ وَهْنٍ وَفِصَٰلُهُۥ فِى عَامَيْنِ أَنِ ٱشْكُرْ لِى وَلِوَٰلِدَيْكَ إِلَىَّ ٱلْمَصِيرُ ﴿١٤﴾ ﴾

Ma’ana: "munyiwasiyya ga Mutum dayi kyautatawa iyayen sa, mahaifiyar sa ta dauki cikin sacikin wahala akan wahala kuma ta shayar dashi na shekara biyu"[323], da kuma faxin sa Maxaukaki:

﴿ وَوَصَّيْنَا ٱلْإِنسَٰنَ بِوَٰلِدَيْهِ إِحْسَٰنًا ۖ حَمَلَتْهُ أُمُّهُۥ كُرْهًا وَوَضَعَتْهُ كُرْهًا ۖ وَحَمْلُهُۥ وَفِصَٰلُهُۥ ثَلَٰثُونَ شَهْرًا ۚ ﴿١٥﴾ ﴾

Ma’ana: " munyi wasiyya ga Mutum daya kyautatawa iyayen sa, mahaifiyar sa ta dauki cikin sa cikin wahala kuma ta shayar dashi cikin wahala, da daukan cikinsa da shayar dashi ya kasance watanni talatin"[324].

Mutumin kirki yana yima kansa addu'a da iyayen sa da zurriyyar sa saboda cikin addu'a ne shiryuwan mutane yake daga Vata wanda sune kalifofin Allah a bayan kasa kuma da haka ne ake raya Duniya kamar yadda Allah yakeson da kuma dacewa da munufar sa, Allah Maxaukaki yace:

﴿ حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ أَشُدَّهُۥ وَبَلَغَ أَرْبَعِينَ سَنَةً قَالَ رَبِّ أَوْزِعْنِىٓ أَنْ أَشْكُرَ نِعْمَتَكَ ٱلَّتِىٓ أَنْعَمْتَ عَلَىَّ وَعَلَىٰ وَٰلِدَىَّ وَأَنْ أَعْمَلَ صَٰلِحًا تَرْضَىٰهُ وَأَصْلِحْ لِى فِى ذُرِّيَّتِىٓ ۖ إِنِّى تُبْتُ إِلَيْكَ وَإِنِّى مِنَ ٱلْمُسْلِمِينَ ﴿١٥﴾ ﴾

Ma’ana: " har idan ya girma ya cika karfin sa yakai shekaru arba'in sai yace ya ubangiji ka bani damar godema

---

Surata lukman ayata 14[323]

Suratul ahkaf [324324]

ni'imarka wanda kayimun da iyayena kuma nayi aiki na Qwarai wanda zaka yarda dashi kuma ka shiryar Xani cikin zuriya na lallai na tuba zuwa gare ka kuma ni ina cikin musulmai (15)"[325].

Iyaye su sukafi cancanta a zauna dasu saboda Abunda aka rawaito cewa wani Mutum ya tambayi manzon Allah s.a.w cewa:

يا رسول ٱللَّهَ ، مَنْ أحَقُّ الناس بِحُسْن صَحابتي ؟ قال : « أمُّك » ، قال : ثم مَنْ ؟ قال : « أمُّك » ، قال : ثم مَنْ ؟ قال : « أمُّك » ، قال : ثم مَنْ ؟ قال : « أبُوك ».

Ma'ana: " ya manzon Allah wanene yafi cancanta na kyakyawanzama na dashi cikin mutane sai yace: mahaifiyar ka, sai Mutumin yace sai kuma wa? Sai yace mahaifiyar ka, sai Mutumin ha kara cewa sai kuma wa? Yace mahaifiyar ka, sai Mutumin ya kara cewa sai kuma wa? Sai yace mahaifinka"[326].

Kuma Haqiqa Allah ya hada godiyarsa da ta iyaye cikin faxin sa cewa:

﴿أَنِ ٱشۡكُرۡ لِي وَلِوَٰلِدَيۡكَ إِلَيَّ ٱلۡمَصِيرُ ١٤﴾

Ma'na: " ka gode mani da iyayen ka, gareni makoma take (14)"[327].

Duk yadda muka aikatawa iyayen mu bazamu taba biyan su dayan daga cikin hakkin su ba akan mu. Ibn umar yaga wani Mutum yana goye da mahaifiyar sa abayan shi yana dawafi da ita, sai ya tambayi ibn umar cewa: (na biyata hakkinta

---

Suratul ahkaf [325]
Buhari da muslim ne suka rawaito shi[326]
Suratu lukman [327]

dake kaina? Sai yace: a'a ko nishi daya baka biyata ba na lokacin haihuwar ka).

Biyayya ga iyaye yana cikin ayyuka na Qwarai wanda suke tsiratar wa daga halaka da yardar Allah, a cikin labarin mutane uku wanda dutse ya rufe su a cikin kogo suka roki Allah da ayyukan su na Qwarai, daga cikin su akwai Mutumin da yace: (ya Allah na kasance inada iyaye biyu tsofaffinaksance baya gaVatar da iyalai na ko kuma kudi akan su, wata rana na kasance akan bishiya ina aiki kafin nadawo na tarar sunyi Bacci na kawo masu Abunci sai naki tashin su daga Bacci na tsaya na jirasu da Abuncin a hannuna har sai da suka farka da asuba kuma ga yarana nan suna ta kuka sunajin yunwa Xana dawo bayan sun tashi suka sha wannan Abunci nasu sannan Mutumin ya roki ubangiji daya kawar masu da wannan dutse daya rufe su a kogo)[328]. Biyayyan iyaye sabAbu ne kai tsaye na shiga aljanna.

عَنْ أَبِى هُرَيْرَةَ عَنِ النَّبِىِّ –صلى ٱللَّهُ عليه وسلم– قَالَ « رَغِمَ أَنْفُ رَغِمَ أَنْفُ رَغِمَ أَنْفُ رَجُلٍ أَدْرَكَ وَالِدَيْهِ أَحَدَهُمَا أَوْ كِلاَهُمَا عِنْدَ الْكِبَرِ لَمْ يُدْخِلْهُ الْجَنَّةَ.

Ma’ana: An karvo Hadis daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarada daga manzon Allah s.a.w yace: " ya tabe ya tabe ya tabe Duk wanda ya riske iyayen sa a lokacin tsufar daya daga cikin su ko su biyun amma hakan be shigar dashi aljanna ba"[329].

Daga cikin biyayyar iyaye akwai cika masu alkawari da yi masu sadaka.

---

Buhari da muslim ne suka rawaito shi[328]
Muslim ne ya rawaito shi (2551) [329]

عَنْ عَائِشَةَ أَنَّ رَجُلاً أَتَى النَّبِىَّ –صلى ٱللَّهَ عليه وسلم– فَقَالَ يَا رَسُولَ ٱللَّهَ إِنَّ أُمِّىَ افْتُلِتَتْ نَفْسَهَا وَلَمْ تُوصِ وَأَظُنُّهَا لَوْ تَكَلَّمَتْ تَصَدَّقَتْ أَفَلَهَا أَجْرٌ إِنْ تَصَدَّقْتُ عَنْهَا قَالَ: نَعَمْ

An karvo daga Aisha Allah yakara mata yarda wani wutum yazo gun manzon Allah s.a.w sai yace: " ya manzon Allah an dauke ranta lokaci xaya ba tsammani kuma batayi wasiyya ba amma ina tsammanin da tayi magana da tayi sadaka shin tana da lada idan nayi mata sadaka? Sai yace: eh tana da lada"[330].

## 8) Sadar da zumunci:

Manzon Allah s.a.w yace: " lallai Allah ya halicci halitta bayan ya gama halitta sai dagantaka tace: wannan lokaci ne dazan nema tsarin ka daga yanke zumunci sai yace:bazaki yard aba ya sadar da Duk wanda ya sadar dake kuma na yanke Duk wanda ya yanke ki, sai tace eh na yarda ya ubangiji na, sai yace: nabaki haka"[331].

أبو هريرة – رضي ٱللَّهَ عنه – : أن رجلا قال : « يا رسولَ ٱللَّهَ ، إن لي قرابة ، أصلِهُم ويقطعونني ، وأُحْسِن إليهم ويُسيئُون إليَّ ، وأحلُم عنهم ، ويجهلون عليَّ ؟ قال : لئن كنتَ كما قلتَ فكأنما تُسِفُّهُم الملَّ ، ولن يزال معك من ٱللَّهَ ظهير عليهم ما دُمتَ على ذلك.

Ma'ana: An karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda cewa wani Mutum yace: ya manzon Allah ina da yan

[330] Muslim ne ya rawaito shi (1004)
[331] Buhari da muslim ne suka rawaito shi

uwa ina ziyartar su amma su basa ziyartata, ina kuma kyautata masu amma suna munana mun, ina hakuri dasu amma suna jahiltata sai yace: " idan dai haka ka kasance kamar yadda ka fadi to ka barsu da zunubi kuma Allah bazai gushe ba yana taimakon ka a kan su matukar ka doge akan haka"[332].

Sada zumunci sabAbu ne ya yalwatan arziki da tsawon rai, an karvo Hadis daga Anas Allah ya kara masa yarda cewa manzon Allah s.a.w yace:

مَن سَرَّهُ أن يَبسُطَ ٱللَّهَ عليه في رِزْقِهِ ، أو يَنْسَأ في أثرِه، فَلْيَصِلْ رحمه.

Ma'ana: " Duk wanda yake so a yalwata masa arzikin sa kuma a tsawaita kwanan sa to ya rika sada zumunci"[333].

## 9) Rufe ido daga kallon haramun da hijabu da kuma neman izini kafin shiga gidan mutane:

Allah Maxaukaki yace:

﴿ قُل لِّلْمُؤْمِنِينَ يَغُضُّوا۟ مِنْ أَبْصَـٰرِهِمْ وَيَحْفَظُوا۟ فُرُوجَهُمْ ۚ ذَٰلِكَ أَزْكَىٰ لَهُمْ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرٌۢ بِمَا يَصْنَعُونَ ۝٣٠ وَقُل لِّلْمُؤْمِنَـٰتِ يَغْضُضْنَ مِنْ أَبْصَـٰرِهِنَّ وَيَحْفَظْنَ فُرُوجَهُنَّ ۝٣١ ﴾

Ma'ana: " kacema muminai maza su rufe idanun su kuma su kare farjin su hakan shi yafi zama tsarki a garesu, lallai Allah Mai bada labari ne akan Abunda suke aikatawa (30) kuma kace ma mata muminai su rufe idanun su kuma su

---

Muslim ne ya rawaito shi (2558) [332]
Buhari da muslim ne suka rawaito shi [333]

kare farkjin su"[334], قَالَ رَسُولُ ٱللَّهَ –صلى ٱللَّهَ عليه وسلم– لِعَلِيٍّ رَضِىَ ٱللَّهَ عَنْهُ :« يَا عَلِيُّ لاَ تُتْبِعِ النَّظْرَةَ النَّظْرَةَ فَإِنَّ لَكَ الأُولَى وَلَيْسَتْ لَكَ الآخِرَةُ ».

Ma’ana: manzon Allah s.a.w yace: ya Aliyu kada ka rika bin kallo da kallo na mace domin kallon farko naka ne baza'a rubuta maka zunubi ba akai amma na biyu za'a rubuta maka zunubi akai"[335].

- **<u>Hijab (tsitirta jiki da kalliya):</u>**

Saboda rufe idon da Allah yayi umurni dashi sai ya wajabta sanya hijAbu ga mace musulma domin kiyaye darajarta da matsayinta da kuma kiyaye al'umma ya yaduwan sha'awa da biyanta ta hanyar da Vata dace ba, Allah Maxaukaki yace:

﴿ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِىُّ قُل لِّأَزْوَٰجِكَ وَبَنَاتِكَ وَنِسَآءِ ٱلْمُؤْمِنِينَ يُدْنِينَ عَلَيْهِنَّ مِن جَلَـٰبِيبِهِنَّ ۚ ذَٰلِكَ أَدْنَىٰٓ أَن يُعْرَفْنَ فَلَا يُؤْذَيْنَ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿٥٩﴾ ﴾

Ma’ana: " ya kai wannan Annbi kace ma matayen ka da yayanka da matan musulmai su rika sanya hijAbun su, hakan shi yafi dace wa domin a gane su kuma bazasu cutar ba, Allah kuma ya kasance Mai gafara da rahama (59)"[336].

- **Neman izini yayin shiga gidan mutane (an shar'anta haka ne saboda kada Mutum yaga Abunda be dace ba):**

Rude ido da kuma neman izini yayi shiga gidan mutane yana gadar da kaMaiwa da tsarkakan rai da kuma yardar

---

[334] Suratun nur
[335] Ahmad ne ya rawaito shi (1369)
[336] Suratul ahazab

Allah, ido shine akwatin zina dagana gani zina ke farawa, da Mutum ya gani sai ya fara tunanin yadda zayyi ya isa zuwa Abunda ya gani daga nan kuma sai dai wanda Allah ya tsare, wani mawaki yana cewa:

" dukkanin wani musifa dake faruwa ido ne mafarin sa

Kuma mafiya yawan yan wuta sune wanda suka raina girman sharri "

## 10) Kunya:

"الْحَيَاءُ مِنَ الإِيمَانِ"

Ma’ana " kunya tana cikin imani"[337],

haka manzon mu Mai daraja s.a.w ya wasafta kamar yadda imani yake hana Mai shi aikata ayyukan da aka haramta haka shima kunya yake hana Mai shi aikata abubuwa mara kyau wanda suke zubar da mutuncin Mutum, saboda haka ne kunya ya kasance darajara karami na imani, kuma Vangare ne nashi wanda baza'a iya rabasu ba, kuma baya zuwa saida alheri ga Mutum cikin mu'amalar sa da maganganun sa da ayyukan sa tare da iyalen sa da al'ummar sa,

عَنْ عِمْرَانَ بن حُصَيْنٍ، أَنَّ النَّبِيَّ صَلَّى ٱللَّهُ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ، قَالَ:"إِنَّ الْحَيَاءَ لا يَأْتِي إِلا بِخَيْرٍ."

An karvo daga Imran Xan Husain Allah ya kara masa yace: manzon Allah s.a.w yace: " kunya baya zuwa sai da alheri"[338].

---

Buhari da muslim ne suka rawaito shi[337]

عَنْ أَبِي مَسْعُودٍ، قَالَ: قَالَ رَسُولُ ٱللَّهَ صَلَّى ٱللَّهَ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ:"إِنَّ مِمَّا أَدْرَكَ النَّاسُ مِنْ كَلامِ النُّبُوَّةِ الأُولَى إِذَا لَمْ تَسْتَحِ فَاصْنَعْ مَا شِئْتَ".

Ma'ana: Kuma daga cikin maganar farko ta annabta Abunda aka rawaito daga Abu mas'ud ukubata Xan amru Allah ya kara masa yarda daga manzon Allah s.a.w yace: " idan baka jin kunya to ka aikata Abunda kake so"[339].

Kuma saboda haka ne malamai suka fassara Haqiqa nin kunya da cewa: kunya wata dAbu'a ce wacce take sanya akan mummunan abu kuma yake hana tuye hakkin wani Mai hakki"[340].

Kuma kunya ta kasance siffa ce ta manzon Allah s.a.w, an karvo Hadis daga Abu sa'id al khudri Allah ya kara masa yarda yace:

"كَانَ رَسُولُ ٱللَّهَ صَلَّى ٱللَّهَ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ أَشَدَّ حَيَاءً مِنَ الْعَذْرَاءِ فِي خِدْرِهَا، وَكَانَ إِذَا كَرِهَ شَيْئًا عُرِفَ ذَلِكَ فِي وَجْهِهِ".

Ma'ana: " manzon Allah s.a.w ya kasance mafi budurwar da take cikin lullubin ta tsananin kunya, kuma ya kasance idan bayason abu muna gane wa daga fuskar sa"[341],

kunya siffa ce Mai kyau ga maza wacce take daukaka dAbu'un su da mu'amalar su, a wurin mace kuma kunya siffa ce ta wajibi wacce take kare am mace martaban da da kaMaiwar ta, ita kunya kamar rigace ta jiki idan Mutum ya barshi sai al'aurarsa ta bayyana sai Abunda yake abuye na munanan dAbu'u da siffafin sa su bayyana.

---

Buhari da muslim ne suka rawaito shi [338]
Buhari ne ya rawaito shi (3483) [339]
Daga cikin littafin riyadussalihin [340]
Buhari da muslim ne suka rawaito shi [341]

## 19. Istigfari (neman gafara):

Istigfari Allah yana share zunuba bai da kura kurai da ita, Allah Maxaukaki yace:

﴿ وَٱلَّذِينَ إِذَا فَعَلُواْ فَٰحِشَةً أَوۡ ظَلَمُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ ذَكَرُواْ ٱللَّهَ فَٱسۡتَغۡفَرُواْ لِذُنُوبِهِمۡ وَمَن يَغۡفِرُ ٱلذُّنُوبَ إِلَّا ٱللَّهُ وَلَمۡ يُصِرُّواْ عَلَىٰ مَا فَعَلُواْ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ١٣٥ ﴾

Ma'ana: " sune wanda idan suka aikata wani aikin alfasha ko kuma zuka zalumci kawunan sai su tuna Allah su nemi gafara daga zunuban su kuma babu Mai gafaarta zunubai sai Allah, kuma bazasu kara komawa ba akan Abunda suka aikata suna sani (135)"[342]

kuma Allah Maxaukaki ya kara cewa:

وَمَن يَعۡمَلۡ سُوٓءًا أَوۡ يَظۡلِمۡ نَفۡسَهُۥ ثُمَّ يَسۡتَغۡفِرِ ٱللَّهَ يَجِدِ ٱللَّهَ غَفُورٗا رَّحِيمٗا

Ma'ana: " Duk wanda ya aikata zunubi ko kuma ya zalumci kansa sa'annan ya nemi gafarar Allah to zai samu Allah Mai gafara da rahama (110)[343].

عن زيد – رضي ٱللَّهَ عنه – : أنه سمع رسولَ ٱللَّهَ –صلى ٱللَّهَ عليه وسلم– يقول : « مَنْ قَال: أَسْتَغْفِرُ ٱللَّهَ الذي لا إِلهَ إلا هوَ الحَيَّ القيومَ وَأَتُوبُ إِليهِ ، غُفِرَ لَهُ وَإِن كَانَ فَرَّ من الزحفِ».

Suratu al'imran [342]
Suratun nisa'I [343]

Ma’ana: An karvo Hadisi daga zaid Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace:" Duk wanda yace astagfirullaha allazi la ilaha illahuwal hayyul kayyumu wa atubu ilaihi, za'a gafarta masa zunuban sa koda sun kasance ya gudu daga yawan su"[344]

عن أنس رضي ٱللَّهَ عنه قال : سمعت رسول ٱللَّهَ صلى ٱللَّهَ عليه وآله وسلم يقول : قال ٱللَّهَ تعالى يابن آدم إنك ما دعوتني ورجوتني غفرت للك على ما كان منك ولا أبالي يا ابن آدم لو بلغت ذنوبك عنان السماء ثم استغفرتني غفرت لك يا ابن آدم لو أتيتني بقراب الأرض خطايا ثم لقيتني لا تشرك بي شيئا لأتيتك بقرابها مغفرة ]

An karvo kuma daga Anas Allah ya kara masa yarda yace: naji manzon Allah s.a.w yana cewa: " Allah Maxaukaki yace: ya kai Xan Adam lallai kai baka taba kirana ba da neman gafara face na gafarta maka Abunda ka aikata kuma bazan damu ba, ya kai Xan Adam da ace zunuban ka zasu ciki faxin Duniya sai ka nemi gafarata akan su zan gafarta maka su baki dayan su kuma bazan damu ba, ya kai Xan Adam da zaka zo mun da zunubin da suka kai faxin Duniya yawa sa'annan ka riske ni baka mun shirka da komai ba to zanzo maka da kwatan kwacin sun a gafara"[345].

Istigfari yana daukaka rai ya kuma tsarkake ta da tafiyar da dattin zuciya, kuma ance wanda Mai tuba daga zunubi kamar wanda beda zunubi ne. ta Vangaren anfani kuma nata ga Mutum istigfari ya kasance yana jawo ni'ima ya kuma kara arziki, Allah Maxaukaki yace yana hakaito labari akan nuhu yana Mai yima mutanen sa alqawari da albishir:

---

[344] Abu dawud da tirmizi ne suka rawaito shi

[345] Tirmizi ne ya rawaito shi (3540)

﴿ فَقُلۡتُ ٱسۡتَغۡفِرُواْ رَبَّكُمۡ إِنَّهُۥ كَانَ غَفَّارٗا ﴿١٠﴾ يُرۡسِلِ ٱلسَّمَآءَ عَلَيۡكُم مِّدۡرَارٗا ﴿١١﴾
وَيُمۡدِدۡكُم بِأَمۡوَٰلٖ وَبَنِينَ وَيَجۡعَل لَّكُمۡ جَنَّٰتٖ وَيَجۡعَل لَّكُمۡ أَنۡهَٰرٗا ﴿١٢﴾ ﴾

Ma’ana: " kuma nace masu su nemi gafarar Allah lallai ya kasance Mai yawan gafara (10) zai kuma saukar muku da ruwan sama Mai akai akai (11) kuma zai kara maku yawan yara da dukiya da yara maza kuma ya baku aljanna kuma yasanya maku koramu (12)"[346].

Kuma an umurci manzon Allah s.a.w da lizimtar istigfari ga kansa da kuma muminai, Allah Maxaukaki yace:

﴿ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لِذَنۢبِكَ وَلِلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِۗ ﴿١٩﴾ ﴾

Ma’ana: " ka nemi gafarar ubangijin ka daga zunuban ka da muminani maza da mata"[347].

عَنِ الأَغَرِّ الْمُزَنِيِّ ، وَكَانَتْ لَهُ صُحْبَةٌ ، قَالَ : قَالَ رَسُولُ ٱللَّهَ صَلَّى ٱللَّهَ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ : إِنَّهُ لَيُغَانُ عَلَى قَلْبِي ، وَإِنِّي لأَسْتَغْفِرُ ٱللَّهَ كُلَّ يَوْمٍ مِائَةَ مَرَّةٍ .

Ma’ana: An karvo daga Agarri al muzini Allah ya kara masa yarda yace manzon Allah s.a.w yace: " lallai natsuwa ko tsoron Allah yana lullube zuciya ta kuma ina neman gafarar Allah ko wani rana sau dari"[348]

عَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ، أَنَّهُ سَمِعَ رَسُولَ ٱللَّهَ صَلَّى ٱللَّهَ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ يَقُولُ:"وَاللَّهِ إِنِّي لأَسْتَغْفِرُ ٱللَّهَ وَأَتُوبُ إِلَيْهِ فِي الْيَوْمِ أَكْثَرَ مِنْ سَبْعِينَ مَرَّةً

[346] Suratu nuhu
[347] Suratu Muhammad ayata 19
[348] Muslim ne ya rawaito shi (2702)

An kuma karvo daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: naji manzon Allah s.a.w yana cewa:

" wallahi ina neman gafarar Allah kuma ina tuba zuwa gare shi cikin ko wani rana fiye da sau saba'in"[349].

An kuma karvo daga ibn Umar Allah ya kara masu yarda yace: mun kasance muna irga ma manzon Allah faxin sa a majalisi sau dari

سبحانك اللهم وبحمدك أشهد أن لا إله إلا أنت أستغفرك وأتوب إليك.

Ma'ana: " ya ubangiji ka gafartamun kuma ka amsa tubana lallai ka kasance Mai yawan amsan tuba Mai rahama"[350].

Kuma an umurce shi da lizimtar istigfari a gabanin mutuwar sa s.a.w, Allah Maxaukaki yace:

﴿ فَسَبِّحْ بِحَمْدِ رَبِّكَ وَٱسْتَغْفِرْهُ ۚ إِنَّهُۥ كَانَ تَوَّابًۢا ﴿٣﴾ ﴾

Ma'ana: " kayi tasbihi akan godiyar ubangijin ka kuma ka nemi gafarar sa, lallai ya kasance Mai yawan amsan tuba"[351].

sabida haka ne aka rawaito daga Aisha Allah ya qara mata yarda tace:

manzon Allah ya kasance yana yawaita istigfari gabanin mutuwar sa yana cewa:

سُبْحَانَكَ وَبِحَمْدِكَ أَسْتَغْفِرُكَ وَأَتُوبُ إِلَيْكَ.

Ma'ana: "subhanaka wabihamdika astagfiruka wa atubu ilaika"[352].

---

Buhari ne ya rawaito shi (6307) [349]
Abu dawud da tirmizi ne suka rawaito shi [350]
Suratun nasri [351]

Istigfari yana tafiyar da bakin ciki ga Mutum kuma yana jawo arziki.

عَنْ ابْنِ عَبَّاسٍ , قَالَ : قَالَ رَسُولُ ٱللَّهَ صَلَّى ٱللَّهَ عَلَيْهِ وسَلَّمَ : مَنْ لَزِمَ الِاسْتِغْفَارَ جَعَلَ ٱللَّهَ لَهُ مِنْ كُلِّ هَمٍّ فَرَجًا ، وَمِنْ كُلِّ ضِيقٍ مَخْرَجًا ، وَرَزَقَهُ مِنْ حَيْثُ لاَ يَحْتَسِبُ.

Ma’ana: An karvo daga Xan Abbas Allah ya kara masu yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: " Duk wanda ya lazimci istigfari Allah zai sanya masa mafita cikin ko wani kunci, da waraka cikin ko wani damuwa, kuma za'a azurtashi ta inda baya tsammani"[353].

Allah yanason masu istigfari, Allah Maxaukaki yace:

﴿ وَٱسْتَغْفِرِ ٱللَّهَۖ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ غَفُورًا رَّحِيمًا ١٠٦ ﴾

Ma’ana: " ka nemi gafarar Allah domin Allah ya kasance Mai gafarada rahama (106)"[354].

An karnbo kuma daga Abu Huraira Allah ya kara masa yarda yace: manzon Allah s.a.w yace: "na rantse da wanda raina ke hannun sa da ace bakwa aikata zunubi da Allah ya tafiyar daku ya kawo mutanen da zasu riqa aikita zunubi suna neman gafarar say a faxarta masu"[355].

Kuma Allah yayiwa muminai alkawarin aljanna Mai ni'ima, Allah Maxaukaki yace:

---

[352] Buhari da muslim ne suka rawaito shi
[353] Albani ya raunata shi cikin littafin attargib, mujalladi na biyu shafi na 268
[354] Suratun nisa'I
[355] Muslim ne ya rawaito shi (2749)

﴿لِلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ عِندَ رَبِّهِمۡ جَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا وَأَزۡوَٰجٞ مُّطَهَّرَةٞ وَرِضۡوَٰنٞ مِّنَ ٱللَّهِۗ ١٥﴾

Ma'ana: " ga wanda sukaji tsoron Allah sunada Aljanna wacce koramu suke gudana a karkashin ta a wurin ubangijin su da mata masu tsarki da kuma yarda daga Allah"[356]

sune wanda daga cikin siffar su akwai:

﴿وَٱلۡمُسۡتَغۡفِرِينَ بِٱلۡأَسۡحَارِ ١٧﴾

Ma'ana: "da masu istigfari a cikin dare gab da fitowar alfijir"[357].

Kuma mutanen da suka gabace mu sun kasance Allah yana masu azaba a Duniya idan basuyi imani ba kuma basu gasgata manzanni ba, amma saboda rahamar Allah ga wannan al'ummar yayi mata alkawarin bazai saukar mana da azaba ba matukar manzon Allah s.a.w yana cikin mu kuma bayanmutuwar sa matukar muna neman gafara da koma wa zuwa gareshi, Allah Maxaukaki yace:

﴿وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُعَذِّبَهُمۡ وَأَنتَ فِيهِمۡۚ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ مُعَذِّبَهُمۡ وَهُمۡ يَسۡتَغۡفِرُونَ ٣٣﴾

Ma'ana: " Allah be kasance zai azabtar daku ba matukar kana cikin su, kuma Allah bazai azabtar dasu ba matukar suna neman gafarar sa (33)"[358].

---

Suratu al'imran ayata 15 [356]
Suratu al'imran [357]

Kuma Duk wanda ya lizimci shugaban istigfari yana Mai sakankancewa da ita cikin zuciyar sa sai ya mutu cikin wannan yara ko kuma cikin daren to yana cikin yan aljanna.

عن شَدَّادِ بْنِ أَوْسٍ ، عَنِ النَّبِيِّ صلى ٱللَّهَ عليه وسلم قَالَ: سَيِّدُ الاِسْتِغْفَارِ اللَّهُمَّ أَنْتَ رَبِّي لاَ إِلَهَ إِلاَّ أَنْتَ خَلَقْتَنِي وَأَنَا عَبْدُكَ وَأَنَا عَلَى عَهْدِكَ وَوَعْدِكَ مَا اسْتَطَعْتُ أَبُوءُ لَكَ بِنِعْمَتِكَ وَأَبُوءُ لَكَ بِذَنْبِي فَاغْفِرْ لِي فَإِنَّهُ لاَ يَغْفِرُ الذُّنُوبَ إِلاَّ أَنْتَ أَعُوذُ بِكَ مِنْ شَرِّ مَا صَنَعْتُ إِذَا قَالَ حِينَ يُمْسِي فَمَاتَ دَخَلَ الْجَنَّةَ ، أَوْ كَانَ مِنْ أَهْلِ الْجَنَّةِ ، وَإِذَا قَالَ حِينَ يُصْبِحُ فَمَاتَ مِنْ يَوْمِهِ مِثْلَهُ.

Ma'ana: An karvo Hadisi daga shaddad Xan aus Alalh ya qara masa yarda daga manzon Allah s.a.w yace: " shugaban istigfari itace Mutum yace: allahuma anta rabbi la ilaha illa anta kalaktani wa ana abduka wa ana ala ahdika wa wa'adika mastada'atu, a'uzu bika min sharri ma sana'atu abu'u laka bi ni'imatika alayya wa abu'u laka bi zanbi fagrilli fa innahu la yagfiruz zunuba illa anta, wanda wanda ya fade ta da rana yana Mai sakankance wa da ita sai ya mutu cikin wannan yini kafin ya yammaci gari to yana cikin yan aljanna, wanda kuma ya fade ta cikin dare yana Mai sakan kancewa da ita sai yam utu kafin safiya to yana cikin yan aljanna"[359] .

عَنْ ثَوْبَانَ قَالَ كَانَ رَسُولُ ٱللَّهَ صَلَّى ٱللَّهَ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ إِذَا انْصَرَفَ مِنْ صَلَاتِهِ اسْتَغْفَرَ ثَلَاثًا وَقَالَ اللَّهُمَّ أَنْتَ السَّلَامُ وَمِنْكَ السَّلَامُ تَبَارَكْتَ ذَا الْجَلَالِ

---

Suratul anfal [358]
Buhari da tirmizi ne suka rawaito shi [359]

وَالْإِكْرَامِ قَالَ الْوَلِيدُ فَقُلْتُ لِلْأَوْزَاعِيِّ كَيْفَ الْاسْتِغْفَارُ قَالَ تَقُولُ أَسْتَغْفِرُ ٱللَّهَ أَسْتَغْفِرُ ٱللَّهَ

Ma’ana: An kuma karvo daga saubana Allah ya kara masa yarda yace: " manzon Allah s.a.w ya kasance idan ya gama Sallah yana neman gafara sau uku. Sai akace ma auza'a, wanda yana daya daga cikin wanda suka rawaito Hadisn: ya yake neman gafarar? Sai yace yana cewa ne: astagfirullah, astagfirullah"[360], saboda zai mantuwa ko kuma rage wani abu da Mutum zai iyayi a cikin Sallah.

Muna neman gafarar ka ya ubangijin mu kuma muna tuba zuwa gareka na kura kuran mu da sakacin mu da mantuwa da rafkanuwa.

AMaien.

---

[360] Muslim ne ya rawaito shi (591)

# KARSHEN LITTAFI:

A karshen wannan littafi ina roqon Allah da ya sanar damu Abunda muka jahilta, kuma ya amfanar damu da Abunda ya sanar damu, domin lallai shi Mai karamci ne, karshen da'awar mu itace godiya ta tabVata ga Allah ubangijin talikai, amincin Allah su tabVata ga manzannin sa, Allah kai dadin tsira ga shugaban mu Muhammad da mafificin aminci da tsira da kuma iyalen sa da sahabban sa baki daya.

www.islamland.com



ISLAM LAND
GROW GOODNESS BY YOUR HAND
EXPLORE ISLAM IN ALL LANGUAGES
WWW.ISLAMLAND.COM